# Globethics Repository

Sake tunawa da horo- da-ilimanta tafiyar da koyarwa cikin wani zato a Afirika: littafin aiki zuwa ga malaman makaranta da masu horon malaman

This page was generated automatically upon download from the Globethics Repository. More information on Globethics see https://www.globethics.net. Data and content policy of Globethics Repository see https://repository.globethics.net/pages/policy.

| | |
|---|---|
| Item Type | Book |
| Publisher | [Globethics Publications];Université Abdou Moumouni de Niamey;Fondazione Vittorino Chizzolini;ERDIE |
| Rights | Attribution-NonCommercial-NoDerivatives 4.0 International |
| Download date | 2026-06-21 16:31:08 |
| Item License | http://creativecommons.org/licenses/by-nc-nd/4.0/ |
| Link to Item | http://hdl.handle.net/20.500.12424/4321204 |

# REPENSER L'ÉDUCATION ET LA PÉDAGOGIE DANS UNE PERSPECTIVE AFRICAINE

MANUEL PRATIQUE À DESTINATION DES ENSEIGNANTS
ET DES FORMATEURS D'ENSEIGNANTS

EDITEURS :
MOHAMED SAGAYAR MOUSSA | ABDELJALIL AKKARI | STEFANIA GANDOLFI

VERSION HAUSA

**Gabatarwa**

Ga wani littafin koyarwa da aka tsara don masu kula da makarantar Nijar da kuma na farko ga malamai da masu bada horo na ƙananan makarantu da sakandare. Wannan littafin yana datushe uku.

Da farko an yitunani da kuma samar da wannan ta hanyar haɗin gwiwa tsakanin ɓangare uku da tsakanin wata gidauniyar taimako ta ƙasar ItaliyaVittorinoChizzolini, jami'arƙasar Geneva da Zauren nazarin kimiyarHarsuna-Al' adu, da na nazarin Jawabai da Ɗabi'un Koyarwa (LACDIPE) na jami'ar Abdou Moumouni na Yamai. Ci gabanshi ya buƙaci haɗuwar ƙwararrun masanan ilimi dabam-dabam da ya ƙumshi ƙwararrun malamai, masanan halayyar ɗan adam da ilimin koyarwa, masanan ilimin tarihi, masanan ilimin zamantakewa, ƙwararrun masana adabi da kimiyar harshe, ƙwararru a cikin bugunlittattafanItaliyanci, Switzrland da na yan Nijar. Ɗayanabinda yake nuna asalin wannan littafi ba shakka shi ne abinda yake cikinshi da tsarinshi. Tabbas, littafin ya mayar da hankali kan shawarshi ga tsarin ilmantarwa wanda ya fifita tushen ilimi na Nijar : nassosi madogarai, al'adun zamantakewa, ɗabi'un zamantakewa da harsuna, abubuwan zamantakewa da al'adu da muhalli kamar yadda za a iya lura da su a cikin tarihi da abubuwan yau da kullum na yan Nijar. A jumulce, littafin ya yi amfani da mamaki masu yawa na karatunzamani ; a taƙaicedai, ya nuna, a cikin hanyoyin da albarkatu da yake bayarwa, cewa abu ne mai yiwuwa kuma abin yabawa, ta fuskar koyarwa da ilimi, dogaro da ɗabi'un abubuwan da suka gabata, da zago daga tsarin al'adu, da samun wahayi daga abubuwan da suke faruwa a yanzu, don ba da shawara ga ɗaliban, wata fahimtattar makoma. A taƙaice, wannan aikin yana nuna farin ciki da ƙarfin (hali da fahimta) : wanda makarantarmu dole ne ta dogara da kanta da kuma kula da kanta don amsawa tare da dacewa da ƙalubalen da suka shafi ƙasarmu da kuma neman amsa, ga tambayoyin da suke haifar da yanayin ɗan adam daga sauran duniya.

A ƙarshe, waɗanda suka wallafa suna da kyakkyawan ra'ayi na gabatar da abubuwan da suke cikin littafin na Faransanci da kuma cikin harsuna biyar na Nijar : Hausa, Zarma, Tamashek, fulfulde da Kanuri. Wato a daidai lokacin da ƙasar Nijar take ƙudirin ƙara haɓakailimi a cikin harsunan ƙasa, wannan takarda tana maraba da ita. Ya tabbatar da zaɓin siyasa wanda yake sa harsunan uwa ingantattun hanyoyin koyarwa. Littafin ya wadatar da tsarin kayan da aka sanya don aiwatar da irin wannan aikin ilimi.

Ainahin, wannan littafin koyarwa kira ne na kamun ƙafa. Yana kira ga dukan masu kulla da harakar makaranta na ƙasar Nijar da su sanya ido sosai kan mahangar karatu da kuma hanyoyin da ake ba ɗalibbai da malamansu, kan ilimin da ake koyar da su da ingantaccen shigarshi cikin tsarin ilimi na ƙasarmu. Don haka ta bi sahun hukunce-hukunce, ayyuka da burin mai girma shugaban Jamhuriyar Nijar **M. Mohamed Bazoum** da na ministan ilimi na ƙasa, wanda babban abin da ya fi damun shi, shi ne gina makarantar Nijar da take alfahari da kimar zamantakewa da take da shi ya haɗe kuma a shirye yake ya taimaka wa waɗanda suke yawan zuwa makarantar wajen gina makomarsu, goben ƙasarmu.

Kasar Nijar tana marhaba da wannan shiri. Ta hanyar muryata, shugaban ƙasa yana miƙa godiya da ƙarfafa gwiwa ga waɗanda suka ƙaddamar da shi, da masu fafutuka da kuma dukkan magoya bayan da suka bayar da gudummuwa wajen wanzuwar wannan littafi na koyarwa, wanda babu shakka yana da amfani.

Dr. Rabiou OUSMAN

Ministre de l'Education Nationale du Niger.

**Sake tunawa da horo- da-ilimanta tafiyar da koyarwa cikin wani zato a Afirika: littafin aiki zuwa ga malaman makaranta da masu horon malaman**

**Stefaniya Gandolfi**

Bayyana wannan littafin na tafiyar da ayyukan koyo da koyarwa « Sake tunawa da horo da ilimi tafiya da koyawa cikin wani zato a Afirika: littafin aiki zuwa ga malaman makaranta da masu horon malaman » ya zama wani babban farin ciki a gare ni a dalilin gaskiya biyu a kaɗan ma na masamman: ta farko ta shafi ilimi da horon waɗanda suka raka kullum kuma suka shiga cikin zurfin rayuwata ta kaina da ta aikina. Ta biyu ta danganta da wannan tsarin da ya shafi horon malaman makarantu a Nijar da yake shi ne yanki na masamman na ayyukan da suka danganta da hujjarmu da kuma mai kwaikwayonsa.**Vittorino Chizzolini** maras addini kuma mai bada horo wanda ya dangana rayuwarsa ga ilimi da horo na ƙashin kansa ga horon malamai a ƙasar Italiya da cikin yawancin ƙasashen duniya ma.
Aikin ilimi da horo wani yanci ne na kowa ya yi rayuwa ta hanyar ƙididdiga da mallakar albarkatun al'adun annashuwa , da bayar da darajar halin yawan irin mutane, sani da darussa. Kamar yadda mai rahoton, masamman, ta rubuta, bisa yancin aikin ilimi da horo sosai cikin rahotonta na bayan nan «sanin yanci ga aikin ilimi da horo kamar na yancin al'adu shi ne canza zaton sau dayawa saboda a kai ga aikin ilimi da horo cikakke kuma na ƙwarai**. (Koumbou Boly Barry, 2021, p.3)**
Don mene ne littafin tafiyar da aikin horo da koyarwa? Saboda a mayar da abun da ake da akwai ingantacce, kuma domin a bunƙasa shi tare da mahujaccin sani gaba-ɗaya na al'ummomin da kuma na aikin ilimi da horo duk ma'abutan aikin ilimi da horokuma domin a darajanta da bunƙasa ƙoƙarin mutanen a sabilin ilimi da horo da sanya hannun kowa da kowa kuma mai inganci.
Kuma littafin yana iya zama kayan aiki na koyarwa wanda za ya sanya a tsara da shirya aikin ilimi da horo tare da yin nazari bisa kan dukan abubuwan mahalli da suka shafi aikin ilimi da horo saboda a ƙididdige arziki, kawar da rishin ƙarfi ko yin cikas kuma da gina halin ƙwarai na aikin koyo da koyarwa da sabbin halayen aikin koyo da koyarwa wanda za su kyautata halin ƙwarai na ilimi da horo.
Wannan littafin yana da manufa da aƙida a lokaci ɗaya: guri saboda Afirika, bayan mulkin mallaka ba ta taɓa samun makaranta ba cikakka wadda take ita ce ta Afirika, amma kaɗai makaranta ta gwamnati a cikin Afirika inda a cikinta ake ganin al'adu da darajojin Afirika ba ta shafi ba aikin koyo da koyarwa ba da aikin tafiyar da tsarin ilimin koyo da koyarwa.
Aƙida, kuma daga baya saboda kowace ƙasa tana da yancin tsara nata halin ilimi da horo da aka rubuta shi cikin darajojin al'adu, a daidaice da al'adun yara domin yin nazari mai zurfi kan koyo da koyarwa mai amfani. Makarantar Afirika tana buƙatar alaƙa da yanayin al'adunta. Kamar yadda ya rubuta shi cikin matani na littafinsa **Moussa Sagayar**« Babu wani jaddawali tsayayye a rubuce ta hanyar gaskiyar jawabban da aka wallafa, kalmomi da sani daidai halattu cikin al'ummomin Afirika. Amma da wuri al'adun bunƙasa sani na zufar kansa bisa darajojji da ɗa'a, ba kan ƙa'idodin da aka lissafa ba da sharuɗɗa ba».
Ilimi da horo a Afirika yau sun ƙumshi kamar gatana iri uku : na farko, irin ƙari, yana meƙewa husa'o'in ilimi da horo na yanzu na gabanin mulkin mallaka; na biyun, na irin gyara, ya bi ta hanyar neman yanci na zamani; na uku na irin sauyi, yana bada shawarar wani sabon tsari na ilimi da horo, na jama'a kuma da na tare da tsoma sayyunsa cikin darajoji da na sanin Afirika na zufar kanta (**Sall, 2020**).

Ilimi da horo na yin gyaran fuskawata fusa’a ce ta ilimi da horo da take sanya sakewar gina gaskiyar jama’a ta hanyar tattaunawa mai ma’ana.Ilimi dahoro na yin gyaran fuska yana sawa yan makaranta su tuna da yin nazari da sake mayar da halin tambayar yanayin jama’a da al’adu waɗanda suka girku a cikinsu.

Wannan samfarin, da **Sall (2020)**take kira “zakuna sun kafi sansaninsu” haɓaka ƙirƙirar makarantar Afirika, mai iya ɗaukar sabon aikin zamantakewa da sabon tsarin ci gaba. Don cimma wannan, ya zama dole a gina tsarin zamantakewa da tattalin arziki da zamantakewar siyasa wanda ya sa ilimi ya zama mabuɗin sauye-sauyen da ake son cimma wa. Ta bakin **Ndoye** « sabon canje-canje ya sake sabunta ilimi da horo da, daga sabbin abubuwan ƙarshe da aka ƙayyade, da aka sake kwatanta da sake gina duka tsari na cikin rassansa dabam-dabam duka kamar na mahallinsa» (**NDOYE,2020**).

Halaye biyu sun zama na buƙata a ra’ayina haƙiƙanta makarantar Afirika. Ta farko ita ce rubutun tsari cikin tsinkayen kyakkyawan zato na tsawon lokaci mai zuwa saboda canje-canjen ilimi da horo suna bada sakamakonsu kuma suna kwatamta halin ƙarhin ƙundun kaɗai cikin dogon lokaci. Ta biyu ita canje-canjen suna iya samun fusa’o’i na tarihin cin gaban ɗan Adamsaboda ba za a iya raba makaranta da halinta da na al’umma ita da kanta **(Sall, 2020).**Ta wata hanyar kuma, cikin ilimi da horo na gargajiya, sanin kai da sanin gwaji tare da junansu suke; don haka ƙarfafa sanin mutum da ilimi da horo suna kama hannun juna kuma liƙe suke kullum(**Sall,2020**).

Akwai kuma wani ƙalubale na uku mai nuna wasu buƙatu« ƙauna da neman amfani da za su iya tura ɗan Adam wajen son rayuwarsa ta gaba. Wata aƙidar lokaci mai zuwa yakamata ta kasance saboda canje-canjen suna sanya zamani dayawa kuma ta hanyar aikata yarjejjeniya tsakanin dukan yan shekaru» da ya kamata a hango su».

Ilimi da horo na Afirika suna buƙatar wata husa’a ta tsakanin yanki dangance da gefinan mahalli,jama’a, arziki tsakanin tsare-tsaren ilimi da horo da sauran tsare-tsaren: na amfani, na mahalli na al’ummomi, na siyasa, na al’adu, na fusa’o’i da agaji mai mahimmanci da **Mamadou Ndoye** yake kira «tsarin fahimtar hadin kan al’umma «**NDOYE, 2020, shafi na 48**)» wanda yake inganta hadasuwar zamantakewa al’umma wanda yayinda yake tasowa daga masaƙin ilimi wanda su kansu sukezama ƙarhi da kuma tushen cigaba.Wani sabon tsinkayen ilimi da horo yana da dalilin hadasuwar dangantaka mai ƙarfi tsakanin dukan shikashikan ilimi da horo da al’umma saboda ta gama jin daɗin rayuwar kowa a tsakaninsu da ƙadarorin taron al’ummomi ta hanyar mahimmiciyar tuntuɓar juna saboda a yi aiki gaba ɗaya tare da dukan shikashikan.Wannan tsarin kama hannun juna yana huskantar wuya da cuɗayyar juna na ƙalubalai kuma wannan takin ƙafa ne na farko wanda za ya ɗora ƙarfi da arzikin karkara bisa kan naunin ilimi da horo na afirika.

Ilimi da horo ƙadarorin kowa da kowa ne kuma «kalmar ƙadara ta kowa da kowa yana sanya ƙarfi bisa matakan da suka dace a ɗauka don cimma gurin halarta, da yake a gare shi ma arzikin jama’a ne. Nazarin da aka rarraba na makirci ne da kayan aiki na ƙadarar ita da kanta. Ilimi da horo da ake tsammani na kowa ne, yana buƙatar kenan tsari ɓoyayyena bin hanyar mafita da tafiyar da siyasar jamahuriya.«**UNESCO 2015**). Manufa ta kayan jama’a ya kamata ya jawo a cikin Afirika cikin arzikin gado na al’adun nahiyar da yake cike da ayyukan bincike mafi kusancí (yanzu). Wannan mahimmin takaicinne wannan littafin ya nufata.

A matsayinsa na ƙadarar jama’a, ilimi da horo na Afirika wani babban jallin al’adu ne saboda yana da manufa : ƙirƙira ƙoƙarin kowa da na jama’a gaba ɗaya wanda yake da cibiya uku: cibiya ta mutum ɗaya da ya sani da akwai mahimmancin ƙoƙarin abun zacen da buƙatun bayyana su cikin halaye kuma da aikin zo-a-gani, wata cibiya ta jama’a ta hanyar cewa iyawa haɗuwa ɗaya

ce da sauran kuma ya taƙaita halin rayuwar ƙwarai ta mutum a wajen wani da kuma cibiyar ma'aikatu da ya shafi ma'abutan gwamnati,masu zaman kansu da na yan farar hula.
Wannan littafin ya kasance kamar gina arziki cikin ilimi da horo a Afirika da ta Nijar a taƙaice.Ilimi da horo da kamar zaman zuciyar ci-gaba na zufar kansa ne da ya ce « shiga daga kansa zuwa kansa.....wanada yake iya haɗa da ƙunla asuli, ƙwarewar mu'amala da sanin ya kamata » **(Kizarbo J, 2006 Shafi na 198-200).**
Haka ɗin yana nufin, kawai ilimi da horo ra'ayin al'adun Afirika yana iya sa wa Afirikar ta hango ci-gabanta: ilimi da horo da yake tsome cikin al'adun Afirika, kamar «icce maras sayyu kuma da ya yi sayyu kuma ya zurfuffa cikin al'adun jiƙaƙƙu saboda ya girma kuma ya bada yaya, hake ne ya iya kasancewa na ilimi da horo wadda idon tana so ta girma kuma ta yi yaya, kamata ta yi ta tsomu cikin al'adun Afirika.Wajibi ne a shirya makaranta da tsarin al'adunta, ta tafarkin mai shiga tsakanin al'adun ɗan adam mahimmancin maganta rayuwar yau-da-kullum, da na tsarin jama'a. ''Zancen yana ɗaukan niyya, yana ragargaza ko ya aifa... Makarantar ba za ta iya juyya wa kayan al'adun Afirika baya ba, idon ba haka ba ta zama makaranta a Afirika ba makarantar Afirika ba''.( **Ki Zerbo J, 1990, shafi na 79**).
Duk da haka,muna iya yin a hankali cikin yanayin halin mayewar harkokin duniya, al'adodin Afirika ba su gudun hatsarin mayar da martanin ainahi da cewar ta rufe kanta da kanta; amma idon bayyana kanta ga juye-juye shi ne hali na girmamawa, buƙatun buɗewa ba ya iya kaɗai mantawa da sayyu na ainahi. Wannan raunannen daidaito wanda mawallafan wannan littafin suka nufata.
Haka ɗin, ba a so ilimi da horo a ruhe bisa kansu amma «wani sarari na ilimi da horo na Afirika buɗaɗɗe ga shiga shugula na duniya da sharhin gabatarwar wani aikin da ba za a iya kaucewa ba na fasara, na wallafawa da kuma na jimiri ga waɗansu kalmomi da ƙirƙirowar wasu sabin canje-canje» kamar yadda **Akkari** ya bunƙasa shi da kyau cikin mataninsa. Kuma, wannan aikin wallafawar, **Akkari** ya ci gaba da cewa har- wa-yau, ana bukatar shi sosai na «abun bamban da kalmomin gama-duniya waɗanda za su iya sanya kansu ciki na gaskiya da gargajiyar karkara. Wai ba na fitar da kalamai da suke kaiwa har bakin duniya amma a sanya ga ƙungiyoyin Afirika da mayar da su na zamani ba tare da ɓarar da rayukansu ba».

**Halin Nijar/abun da ya shahi Nijar**

Tarihin halin ilimantar a Nijar an gano shi daga zaƙewar shikashikan ƙasashen waje, daga ƙungiyoyin duniya, da kuma daga bambancin kalaman shikashikai na ƙasa, na masu zaman kansu da na farar hula da aka sanya a gaba. Waɗannan bambancin kalaman shikashikan yana sanya halin ilimantarwa a saɓanin ƙa'idodin, tsarin tunani da tsarin sauye-sauye. Mayar da tsarin makaranta na gwamnati kamar wuri ne mai daraja na koyar da sani ya zama wata gona mai ɗaurin kai.
Wannan littafin yana tsunduma sayyunsa cikin Nijar kuma yana kwatanta gangama sani da yake cikin halin ilimi da horo daga waɗannan abukan tattaunawar na karkara. Saboda haka ne, yake darajanta dangantakar duka abukan shawara na rayuwar mahalli da maɗaukinsa tare da abukan shawara na al'adu da na gwamnati, ba za ya shiga ba cikin aji ba amma suna gina arziki da za ya amfana ilimi da horo na duka da na kowa. Cikin waɗannan abokan shawarwarin akwai maroƙa, masu yin gatana, da masu amfani da yan karin yan wasan kwaikwaiwo, yan jarida, masu fasaha, mawaƙa da sauran waɗansu dabam har-wa-yau. Game da saɓani tsakanin sani na gargajiya, sabin dubarun ilimi da horo da fusa'o'i, ana yin fatan makarantar Nijar ta kasance makaranta ce da ake kulawa sosai kuma mai samun tabi'un ƙwarai wadda take da hazaƙar ilimantar da matasa yan shekaru ɗaya.
Abubuwan koyawa da aka nuna cikin babuwan dabam dabam na wannan littafin suna so su kasance na hira da malaman makarantu da kuma duka al'ummar Nijar. Nijar wata ƙasa ce

wadda ba ta sanya sanin al'adu, da na jama'a da na tattalin arzikin gargjiya cikin abubuwan koyo da koyarwa, sanin da aka yi amfani da su a cikin iyali, cikin jama'a, kuma haka ɗin ya janyo wata irin rabuwa da harkokin ilimi da horo na gargajia, rabuwa tsakanin makaranta da mahallin iyali, da na al'umma da na addini.
Da jin kowa, wannan rabuwar ta yi ƙarhi sosai har ma da an yi nesa kaɗan da babban birnin da kuma sauran manyan biranen ƙasar. Wani gami ma, akwai wata niyyar haɗa koyo da koyarwa na ƙayyadaddu da koyo da koyarwa na addini tun ma da matsawar uwayen yara amma salon karatun biyu, ko da an gudanar da su a wuri ɗaya,sun kasance dabam dabam suke saboda koyo da koyawar ba guri ɗaya ba ake horar da su ba kuma suna yin amfani da tafiyar da koyawar iri-iri dabam dabam. Kudiri na **Buba Amadu** da yake zancen nazarin tsarin tafiyar da koyawar Alƙura'ani ''mai girma'' yana da ma'ana sosai a dalilin yana sanya tsarin ilimi da horo ƙayyadadde da maras ƙayyada cikin tsarin horo da na sauyawar al'umma. Yana sanya jayi da cewar «Idon ana buƙatar koyo da koyarwa na Alƙura'ani ''mai girma'' ya cimma gurinsa na hanyar ilimi da horo, sai malaman makaranta sun ƙirƙiro wata dubara wadda za ta ba wa Alƙura'ani ''mai girma'' ayyukan tsarin tafiyar da koyo da koyawar darussa».
Harkar ilimi da horo na gargajiya a Nijar ya zama kamar na gado da ya shafi duka abun da mutum ya kamata ya gada daga iyalinsa, da gungun abokan aiki, da na uwaye da kakannu, amma kuma da na koyo ko ma irin yadda ya kasance. Yana wakiltar hiye da daga na ƙadara, saboda kuma ya kasance na ƙwaƙƙwalwa, na al'ada na makaranta, na sana'a, ƙayyadadde da na falfasar duniya» ( **Meuniyer 2008, P 310**). Matanin **Ali Rufai** yana bin wannan ra'ayin tare da bada haƙiƙar « Mafarin ilimi da horo na gargajiya ya dogara bisa koyo da koyarwar darajoji. Darajojin ba su rinjayen ƙarfi, ba a tsaye suke ba waje ɗaya amma suna da ƙwazo, da ci-gaba. Su ne dai suke sa wa ɗan Adam ya yi rayuwa cikin daidaito mai armashi tare da shi kansa ko da sauran ». Kenan ya kyautu a gano hanyoyin tunani saboda a gane halin da mutane za su iya gudanar ma kansu sani kuma su hango su da kansu a matsayinsu na maɗaukan sani .
Akwai cikas dayawa da suke sanya tazara tsakanin ilimi da makaranta da kuma ilimin gargajiya kamar su, allal misalance, harshen da aka yi amfani da shi. A Nijar, « dokar shaikarar 2019 ta keɓe da kiran sunayensu harshunan uwa su goma- sha- ɗaya (11) da ta lauya masu darajar matsayin harshunan ƙasa daidai » (**MALLAM GARBA MAMAN**).
Ana iya ɗaukan harshe kamar wani gida, kamar wani hili na sanin ciwon kai mai zurhi na ciki mai zaman maɓoya, wurin tarbe da hilin ƙaura mai sanya wa zuwa wajajen waɗansu don a tarbe su **(MAYER-BISCHP, 2011, shafi na .5).**
Shi harshen uwa tushe ne na ainahin bin sassala, da aka wallafa kamar ''gidan halitta, na zurhin hali'', ra'ayin tunani da na son rai, na samun cikakken horo na mutum kaɗai da na jama'a, da yake ba duniya ma'ana. Harshe shi yake yin dalilin tunani amma, ana yin shi waje, tunanin yana yunƙura bisa harshen; akwai wani faɗi-a-ji na jin juna. Harshen uwa shi ne tushe da in ji, hanya ce mai tabbatar da tashin fari na ilimin yaro, yana kawo masa daidaito na ginshiƙi idon babu shi yana rage darajarsa. Ga harshen uwarsa, yaro lafiya yake kuma,''bayan an hana masa damar yin amfani da madogara ta yaren da ya saba na iyali, makaranta tana sanya shi ta kai tsaye cikin halin ci-da-baya '' (**Poth,1988, shafi na 11**).
Da janye wa yaro ba'afirike damar yin amfani da harshen uwarsa don a ba shi kayan tattaunawa har-ya-yau sam-sam ma da ake kasa yi a mafarin tsawon shekarun karatu, makaranta ya sanya cikin kasa nuna ra'ayoyinsa na ƙwarai da cin amfaninsa.« Kara war yaro da wani baƙon harshe..... tana sanya shi ya ƙyale kuma cikin lokutta mafi yawa, waɗansu mawucin halaye ta wani bi ma cikin kwatancin magana «Ta wani halin, ta hana mashi yancin harshen uwarsa, makarantar tana ƙaurace mashi amfanin komai saboda yaron yana da tunani, yana bambanta, yana bada sakamako ta hanya harshen uwarsa saboda wagga ita ce

halin yin magana na kai-tsaye. Da ma, nazarin yana haƙiƙanta da ce wa koyo da koyarwar harshe na biyu (**Poth 1988, shafi na 12-13**).
Kuma tazara mafi yawa ta haƙiƙa a cikin jahar Maraɗi, Zandar,Tawa da Difa yawan kammala makaranta, masamman na ƴan mata, kasance ƙasa **(Jamhuriyar Nijar**, **kundin ƙayyada na shekarar 2004-2005).**

Fasarar wannan littafin cikin tsare-tsaren harshunan ƙasa yana nuna amincewar masu hannu da shuni / masu bayar da gudummuwarsu don sanya yancin yin amfani da harshen uwa a tsakar tattaunawa bisa makaranta.
Ilimi da horo a Nijar yana nuna taƙaƙa wani tsarin da ba ya goya wa yare baya a tsakanin sani na ilimin zamani da sani na karkara yana fuskantar rishin cin nasarar ilimi da horo kuma dangance da makaranta ta hanyar wani shashe na al'umma. Masu riƙe da sanin cikin karkara « yana ga jama'a masu zaman garin da al'ummomin yankuna masu ɗauke da sanin al'umomminsu ta kansu da jama'ar karkarar » (**Hill, 2020 , shafi na 11**).
A taƙaice ya shafi sanin da aka girka bisa wurare kuma da aka mallaƙawa yan makaranta da ba za su iya rarrabuwa ba da halaye na al'ummomi, na al'adu, na ma'aikatu da na siyasa: '' ba a ba yancin kai na dauri daraja ba lokacin da aka ɗauki sani a matsayin ƙayadaddun baiko saboda ganin ɗaukan hukunci na zaman jama'a duka'' (**Latulippe & Klenk, 2019, shafi na 7**).
Ta ra'ayin **Ki-Zerbo «**mutanen da suka iliminta ta hanyar gargajiya sun hi samun makami don su rayu cikin mahallin Afirika hiye da waɗanda aka mayar ƙauye».
Makaranta a Afirika ta zauna »cikin mulkin ƙasashen turawan yamma, ƙasashen yan mulkin mallaka»**(Ki- Zerbo J,2014 ).**Saboda makaranta ta dawo makarantar ci-gaba bai kamata *ba ta rarraba kalmomi da abubuwa, abun da ake faɗi da abun da ake rayuwa,* sai in ta shiga cikin al'adu, ta «janyo ƙarfinta cikin Afirika da kanta», ta sake dawowa yar Afirika, ta zamanto ta wadda ba ta kamata ba ta bar zama''.
Aikin makaranta shi ne darajantar da sani, tarben uwayen yara a makaranta,yin amfani da karin magana da gatana a matsayin tushen koyo da koyarwa da sani, ta buɗe kofa ga husa'a kuma ta ɗauki yaunin bambance-bambance kamar saɓanin ra'ayin makarantar gwamnati «A Nijar, Matasa sun fi yin amfani da karin magana don su horar da matasa a cikin zamantakewa..... suna fasarar ba abun da suka faɗa amma kuma har-wa-yau yadda suke gani, da tunani: wani halin kasancewa....Wani irin kashi-kashi ne na al'adu. Bayan ƙarin aikin tattaunawa da yake ɗauke, kuma yana da wani aiki madaidaici ». Ana iya yin nazarin halaye uku na al'adu ta hanyar karin magana: al'ada, yawanta al'adu, tsakanin al'adun **(AMADOU dans cet ouvrage.).**
"Yakamata a koyi sauraren gatana, koyarwa, tarihi ko kallon abubuwa masu hayi iri-iri a lokaci ɗaya. Wannan shi ne koyo da gaske, sani ne mai zurhi na abun da aka koya cikin ɓoyyayar magana. Siffar ita ce hira. Halitar ma hira. Komai hira ne » **Amadou Hampâté Bâ (HAMPATE BA, 1990)** ya rubuta**.** Gatanan *wani sani ne na yanki;* A tafiya ɗaya husa'a ce, wani salon binkicen sani ne da kuma wani kayan aikin koyo da koyarwa ne. A daidai da saɓanin karatun ka kuma da aikin darussa, yana a zaman babban matsayin a tafarkin forkon koyawa yara ilimi tare da wata alaƙa ta sani mai yawa dagance da yin amfani na masamman na magana **(HAMPATE BA, u, 1990).**
Mahimmancin jawabin na dauri yana tsakiya saboda ya gaje wuri mai ƙarfin arziki a cikin halayen aikin ilimi da horo."Yana nishaɗantarwa kuma yana haɗa zumunci amma yana ilimantar kuma inda aikinsa na kayan aiki bada darussa da ilmantarwa da ake ganin shi ta

hanyar sanya darajojin ɗa'a, na wani tsarin mutunci da na kyakkyawan hali **(ISSOUFOU a cikin littafinsa).**
Daga wannan kyakkyawan zaton, makaranta ta sanar wa malaman makaranta wani ƙudiri na gabata saboda zaɓen hanyoyin da suka fi iyawa dangance da aikin ilimi da horo na yan makarantarsu. Tana zama makaranta *rufaffa,* wanda ba ta yin zaɓe ta rarraba, amma wadda ta ƙirƙiro koyo da koyarwa da horo kan al'adu na gaba-ɗaya, wadda take tabbatar da dacewa bisa mafarin sani kan ainahi, al'adu, da dangantaka tsakanin al'ummomi dabam dabam. Kamar yadda **Moctar** ya hakiƙanta cikin wannan littafin « Ta ganin haka ya kamata makarantata raka kuma ta sanya uwayen yara cikin harkokin sabon tsarin da ya danganta kuma dayawa saboda a kauda nisansu dangance da makaranta kuma don ta ba su ƙarin yarda ga malaman a cikin abubuwan makarantar » .Yayin da dangantaka tsakanin uwaye da makaranta take inganta, yayin da aikin koyo da koyarwa yake tafiya da kyau, yayin da ilimin karkara da harsunan gida sun fi samun daraja da kuma ɓangaren aikin ilmantarwa ya fi kira da babbar murya da kuma darajantar da al'umma.
A ƙarshe dai , wannan littafin yana nufin haɓaka tsarin ilmantarwa wanda ya san tushen mutum da al'umma da suke yunƙura wajen tsara ayyukan ilimi.

**Madogara**


1. HAMPATE BA Amadou, 1990, Il n'y a pas de petite querelle, Nouveaux contes de la savane, Pocket, Paris.
2. HILL_ R., Working with indigenous local and scientific knowledge in assessments of nature and nature's linkages with people 2020, p. 11
3. KI ZERBO, Eduquer ou périr, Unesco-Unicef, Dakar 1990, p. 79
4. KI-ZERBO J., La semaine africaine, Unesco, 2014
5. KI-ZERBO Joseph, A quand l'Afrique? Ouagadougou, 2006, p. 198-200
6. KOUMBOU BOLY BARRY, Droit à l'éducation : les dimensions culturelles du droit à l'éducation ou le droit à l'éducation en tant que droit culturel, Rapport de la Rapporteuse spéciale sur le droit à l'éducation, Nations Unies, 2021
7. LATULIPPE N., and Klenk N. Making room and moving over knouldge_co-production indigenous, 2019, p. 7
8. MEUNIER OLIVIER, Ecole d'aujourd'hui et savoirs traditionnels (Niger, Réunion, Brésil) dans Cahiers internationaux de sociologies 2008/2 N°125, pp 310
9. MEYER-BISCH P., L'hospitalité politique par la langue, Document de travail de l'IIEDH n°19, 2011, p. 5
10. NDOYE Mamadou. (2020). « Réformes éducatives : attentes et conduite du changement ». *Revue internationale d'éducation de Sèvres,* Paris, n° 83,

11. POTH J., L'enseignement des langues maternelles africaines à l'école, Breda, Dakar, 1988, p. 11
12. SALL A., Regards sur l'éducation en Afrique subsaharienne à l'horizon 2040, Revue internationale de Sèvres, n. 37, Paris, 2020,
13. UNESCO, Repenser l'éducation. Vers un bien commun mondial, Paris, 2015, pp. 87-88

**Babi na 1**

Hakkoki yaro, tarbiya cikin halin haɗuwar al’adu a kan yanƙasanci : Waɗanne ginshiƙai ne a cikin yanayi irin na Afirika

**Abdeljalil AKKAI et Rita Locatelli**

***Taƙaicewa***
Kalmomin tarbiya da ake ji a ƙasashen duniya sun shigo Afirika ba tare da wani amarshi ga yanayi na al’ada da tarifin na Afirika. Cikin wannan matanin, za mu kwatanta kawo sauyi ga ma’anar waɗannan kalmomin ta hanyar binciken dalilai da akan juyewa a ƙasashen Afirika inda za mu yi wasu tambayoyi ko mu amfani da wani killattacen yanayi.
Da farko, za mu yi nazarin iya fasarorin na jawabai na ƙasa da ƙasa bisan hakkokin yaro. Za mu yi nazarin, manyan wahalhalu na da yadda ake juyensu a yanayi na Afirika. Waɗannan wahalhalu suna tayar da hankali matuƙa musamman ma a fannin da shafi aikin yara ƙanana, da daidaito tsakanin yan mata da yan maza, auren wuri da kaciyar mata.
Bayan wannan, za mu yi nazarin ƙalubalan makarantar Afirika da take fuskantar barazanar fasa’o’in haɗuwar tabi’u da suka bambanta na tarbiya. Za mu kuma duba hulɗa tsakanin ƙabilu da kuma buƙatar tarbiyar shimfiɗa zaman lafiya, rishin isassar damar samun ilimi na wasu yan tsararun ƙabilu da kuma canje-canjen tabi’u da halayen da ake samu a halin yanzu cikin al’umomin Afirika.
A ƙarshe, matanin namu za yi nazarin hanyoyin girka tarbiyar yanƙasanci, a cikin yanayi na ƙasa da kuma yanayi na gaba-ɗaya. Hakan yana da kyau a cikin yanayi na tarifin sauyin kalmar *yanƙasanci* da aka maido a dalilin bunƙasar sabbin fusa’o’i na zamani na sadarwa da suka hadassa cakuɗewar iyakokin tsakanin fage na halarta na zahiri da shafinan sadarwa. Za a yi kuma nazarin sauye-sauye da aka samu daga shigowar waɗannan sabbin fusa’o’i na zamani na sadarwa.
Hashashen da za mu hujjanta cikin wannan matani ya samo tushe daga buƙata ta barin ƙofar fagen koyar da tarbiya na Afirika buɗe ga mahimman tabi’u na wasu ƙasashe na duniya, amma da sharaɗin girka wani aiki na fasara. na daidaitawa da kuma ƙiye wa wasu kalmomi da wasu sabbin juye-juye a cikin nafiyar Afirika.

**1. Hakkokin yaro ɗan Afirika : Manufofi na ƙasa da ƙasa da halaye na zahiri na Afirika**

Daga shekara 1945, dokoki na duniya a kan hakkokin ɗan Adam sun ƙumshi ƙudirai da suke kiyaye damar samun tarbiya da ilimi da kuma haramta dukkan wani cin zarafin yara. Kamar yadda Kola (2017) ya ce, gwaggwarmayar neman amincewa da manya-manya hakkokin na yara ta samo tushe daga matakai dabam-dabam da aikin haɗakar ƙungiyoyi ta ƙasa da ƙasa mai kawo wa yara agaji a shekara ta 1923. Wannan kokowar ita ce ta sanya aka amince da jawabi na Geneba (Genève) da kumaamincewar dokar daga Al’uma ƙasashen duniya a shekara ta 1924. Daga nan, Majalisar Ɗinki Duniya ya yaɗa jawabin dokokin hakkokin yara a 1954. Bayan nan, amincewar yarjejeniya dangance da hakkokin yara na babban taro na Majalisar Ɗinki Duniya a 1989 ya yi tasiri wajen wannan doguwar kokowa. Usular Afirika ta hakkokin da jin daɗin rayuwar yara wata doka ce da ƙasashe mambobin ƙungiyar ƙasashen Afiirika suka

amince da ita a 1999 ita. Dokar tana bin tsarin da yarjejeniya Majalisar Ɗinkin Duniya da take da na son cimma gurin daidaito da yanayi na Afirika.
Don haka, aka sanya hakkoki yara cikin yarjejeniyoyi da dokokin na ƙasa da ƙasa, na yankin ƙasashe da na cikin ƙasashe da aka jima da amincewa da su a cikin ƙasahe na duniya. Waɗannan ci-gaba dabam-dabam a cikin rubuce-rubuce masu ƙa'ida na dokoki na tsakanin ƙasa da ƙasa sun kasance a yau wata mahimmiyar nasara saboda dalilai da dama. Da farko, suna tunatar wa gwamnati da ma ginshiƙin aikinta na samar da kariya, damar samun ilimin mai inganci da kuma kula wa ta musamman zuwa ga yara. Da yawa da cikin ƙasashe na duniya sun rattaɓa hannu bisan yarjejeniyoyi na ƙasa da ƙasa kuma sun fasara su cikin tsarin dokokin na ƙasashensukuma sun sanya su cikin yarjajjeniyoyi tsakaninsu da ƙasashen wasu nahiyoyi.
Bayan hakan, manufofi na ƙasa da ƙasa da suka amince da hakkokin yara suna tunatar da uwayen yara, malaman makaranta da dukkan wani mai bada tarbiya ko horo babba, da buƙata ta shirya mahimman matakai don ba wa kowane yaro damar bunɓusa. A wani mataki kuma ƙayadaddun rubuce-rubuce na ƙasa na ƙasa suna iya shiga cikin sharuɗɗa girka huroje-huroje da jadawalan hulɗa tsakanin ƙasa da ƙasa. Suna iya zama wata hanya tursasawa da take bada damar kyautata halin da yara musamman ma masu fuskanatar barazanar rayuwa.
Sanyawarhakkokin yaron Afirika cikin shawarwarin ƙasa da ƙasa da suka kawo sauye-sauye, ci-gaba babba amma da bai isa ba, da sauran kifi cikin ruwa. A wani ɓangare, kamar duk wata niyya ta siyasa ta shiga cikin tsarin ƙa'idoji ƙasa da ƙasa, akwai wahalhalu idan ana son wucewa ga aikatawa zahiri da sumun karɓuwa wajen mutane. Rarraucin ƙasashen Afirika yana ƙaruwa a kullum, shekaru dama da suka wuce. Uzurai da sauye-sauye a fannin tattali arziki da na ingancin mulki sun bar shaida ga tsarin tafiyar da gwamnati da yaran Afirika (Adepoju, 1993 ; Thomson, 2017).
A Afirika ta Yamma, wasu ƙasashe kamar su Nijar, Burkina Faso, Kawdibuwa, Sanagal, sun rattaɓa hannu wajen girka wata dubarar « yi-yi » ko« faire-faire » da faransanci. Ita wannan dubarar tana bada damar a miƙa wa wani fanni mai zaman kanshi da kuma ƙungiyoyi masu zaman kansu (ONG) na gida da na ƙasashen, wasu muƙamai na gudanar da wasu ayukkan da suka rayata a wuyan gwamnati kamar taimakawa wajen kiyon lafiya da kuma bunƙasa ilimin na makarantu.

> « Wannan dubara tana bada damar janyo abokan hulɗa a matsayin yan kwantaragi inda za bayyana musu abubuwan da suka rataya a wuyansu da hakkokin kowane ɓangare (Gwamnati da abokan hulɗa) don ganin an aiwatar da kusancin jadawalin yaƙi da jahilci. » (MCAPLN, p. 9, 2010).

Waɗansu ƙasashen sun girka siyasar tsarin rarrabe-rarraben mulki da cin gashin kai amma har yau ba a samu yadda ake so saboda juyen kuɗaɗe suwa ga jahohi yakan ɗauki lokaci mai tsawo ko kuma kuɗin ba ya isowa cikin jahohinDaga bisani, matsayin hulɗa tsakanin ƙasa da ƙasa na sasantawar tsarin rarrabawar mulki ba ya ba ta damar zama ginshiƙi cikin al'adar siyasar Afirika (Hyden, 2017 Idan rarrabar mulki don cin gashin kai a fannin tarbiyantarwa ya dogara da mahimmiyar manufar kusancin ɗaukan matakai daga al'umomi, to ya zamanto girkawar tsare-tsare cikin al'uma mai cin gashin kai ya haddasa jaye hannu gwamnati daga wasu tsare-tsare na jaha da kuma al'umomi na zagaye.Akwai wani giɓi babba tsakanin al'kawalan ƙasashen na

kiyaye hakkokin yara a Afirika da kuma yanayi da abubuwan ake gani a zahiri. Hakan ya zama wajibi a wasu ƙasashe da suka tsinci kansu cikin hali na matsuwa waɗanda a yau suna da yawa a Afirika inda aka fi samun yawan adadin yara yan gudun hijira. Rishin sani waɗannan dokoki na ƙasa da ƙasa a kan hakkin kare al'umomi da suke cikin hali na matsuwa daga masu faɗi-a-ji da yan siyasa na waɗannan ƙasashe ya zama tarnaƙi ga tashi-tsaye na gaba ɗaya kan wannan batu(Akkari et Sagayar, 2021).

A bangare gudan, wasu manufofi cikin dokokin na ƙasa da ƙasa suna iya fuskanta bujerawa, canhe-canhen al'adu, na addinai da na al'umomi. Hakan ba ya bada damar aiwaitarwa a zahiri. Daga bisani, ya kamata manufofi da kalmomi da ka tsaida tsakanin ƙasashe su dogara da yanayi da kuma al'adu na gida. Ba. Ba bayyana saƙo da kalamai na tada jijiyoyin wuya a fannin ƙasa da ƙasa za a yi kawai, amma a ba wa al'umomi na Afirika damar sabinta tabi'unsu ba tare da sun yadda su gaba ɗaya. Za mu yi nazari ɗaya bayan ɗaya na misalai huɗu na miyagun halaye da suke nuna buƙatar shiri na fuskantar ƙasashen Afirika don aiwatarwa ta gaba ɗaya ta ci-gaba a fanni hakkokin yaro.Da daɗewa an yaƙi aiki na yara a tarurrika na ƙasa da ƙasa. Rayuwa yaro da yake aiki tana fuskantar barazanar : kasancewa yaro da talauci. Wannan hatsari yana haddasa miyagun siffofi na cin zarafi yara wajen sa su ayukka da suka fi ƙarfinsu (BIT, 2002). Bisan titunan manyan birane na Afirika ta yamma, an bar yara da yawa su kaɗai, suna bara ga kuma fama da ƙwamaso, matsaloli na kiwon lafiya da cin zarafi iri-iri. Daga ƙididdigu da dama, adadin yara ƙanana da suke aiki a Afirika za ya iya kai miliyan 100 nan da shekaru goma zuwa goma sha biyar masu zuwa, hakan zai kasance ƙalubale ga masu faɗi-a-ji a fannin sayasa a Afirika. Talauci yana ɗaya daga cikin manyan dalilan yawantar matsalar aiki yara a Afirika (Admasie, 2002).

Sai yaƙar wannan babban al'amari na aikin yara yana buƙatar a ruguwar talauci amma da kuma a ƙalla ayukkan biyu na sanin ciwon kai da shiga hankali da kuma faɗakarwa da waye kan al'uma a kan tarbiyantarwar tabi'a da addini. Ya kamata su uwaye su ɗaukin nauyin da ya rataya a kansu na kariya da kula da yaronsu. Bada yaro da uwaye suke yi, tabi'a uwaye da kakanni a Afirika tana son gyaran fuska, kullawa da kuma bi-sau-da-ƙafa. Su kuma manya da suke aika yara cikin tituna suna bara maimakon su tura su makaranta, kamar a ƙasar Senagal yadda ake yi wa yara « Talibe », ya kamata ƙungiyoyi masu zaman kansu da shuganan addinai su yake su. Ya kamata a samu mafitata «zamantakewar al'uma » don a gano wannan lamari na aikin yara. Daga haka ba za a iya gano dalilai da irin aikin yara da kuma matsaloli da ribar da take tare da aikin yaran idan ba a yi aiki ba yanayi na gidaTunani na duniya bisan wata duniya idan an bar sanya yara aiki na iya kasancewa tunani da ba ya da kangado a yanayi na rayuwar yara a ƙasashen Afirika da kuma a cikin iyalansu da al'umominsu (Abebe&Bessell, 2011).Halarta yara fulani wajen ƙananan ayukkan na kiwo yana da amfani sosai idan ba za ta hana yaron zuwa makaranta ba koyon karatu. Kenan makaranta ta yi aiki yanayi na rayuwar makiyaya amma ba sa su fulani zaɓin da ba sa su iya ba : rayuwar iyali ko zuwa makarantar yara. A yi bayani sosai cikin dokoki na ƙasa da ƙasa a kan daidaito tsakanin yar yarinya da ɗan yaro kuma a yi wa dokokin wuri cikin wani kundi na ci-gaban maiɗorewa 2030.Sai dai idan kuna da karin magana a Indiya da Nijar da yake cewa *« aifuwar ɗiya mace da ciyar da ita tamƙar ka ba gona maƙwabci ruwa ne! »,* hakan yana nuna daɗaɗɗen tarihi na rishin daidaito

tsakanin maza da mata. Kenan ya kamata a yi aiki sosai a kan ire-iren sauye-sauyen tabi'u da ake samu. Saɓanin haka, fusa'ar jinsi da aka kawo a Afirika da kuma hulɗa ƙasa da ƙasa ta haɓɓaka ba ta da wani tasiri kuma ba ta yi aiki ba a kan nazarin mai zurfi da sabbin tabi'u na zamantakewar ɗan AdamMaimakon a wakilta waɗannan suka da ce ta hanyar gwada musu mahimmancin daidaito tsakanin yarinya-yaro, sai a ɓata al'adu da tabi'u na uwaye da kakanni kuma ɗora musu laifi ba tare da a bayyana dalilan.
A samun ci-gaba na zahiri amma akwai tafiyar hawainiya cikin lamarin saboda akwai tabi'u biyu da suka girku cikin asuli da tabi'u. Cewar haka matsayin makaranta yana da mahimmanci. Riƙe ɗiya mata a makaranta daga shekaru 12 zuwa 18 yana ba su damar kiyaye ɗaukan ciki da hana auren da wuri amma kuma da koya wa mafiyawan yaran mata karatu don a samu a yi yaƙi da kaciyar mata da rishin zuwa makarantaA taƙaice, yaƙi da waɗannan muyagun halayen yana buƙatar yunƙurin da ba sassautawa na tsarin horo da ilimantarwa, daga yara, uwaye, malaman makaranta da al'uma gaba ɗaya. Misali, ƙaruwar kaso na bisa ɗari na malamai mata cikin al'uma malaman makaranta na ba yan mata a Afirika damar su ci gaba da karatunsu ta hanyar koyi da malaman mata (Stromquist et al. 2017). Waɗannan muyagun halaye da muka gani sun taɓarɓare a cikin halin matsuwa. Yara da suka baro garuruwansu da yan gudun hijira na gida da na waje suna fuskantar cin zarahi kai tsaye.Kasar Nijar kai da ma yanki Sahiyal gaba ɗaya suna fuskantar wannan matsalar. Girmamwa ta gaba ɗaya na hakkokin yaro y
danganta da dalilai da yawa, musamman ma yaƙi da talauci na iyalai a Afirika. Amma wannan ba zai kawar da hali na take hakkokin ɗan Adam idan ba a tushe hanyoyi na samar da ilimi ko na zamantakewa

**2. Fusa'o'i na haɗuwar tabi'u/al'adu**

Mafiya yawa tsare-tsare bada horo da ilimi na ƙasashen Arewa sun aiwatar da fusa'o'i na huɗuwar tabi'u don su daidaita su da tsarin samar da horo da ilimi ga al'uma yan makaranta da ya zamanto a halin yau tana ƙunshe da al'umomi da tabi'u dabam-dabam saboda tashe-tashe da ƙaurace-ƙauracen mutane (Akkari & Radhouane, 2019). Cikin ƙasashen Kudu musamman ma a Afirika girkuwar fusaa'o'in haɗuwar tabi'u suna tafiyar hawainiya kuma sun dogara da yan tsare-tsare da suka zo daga wajeSai dai, a Afirika muna ganin ƙasar Nijar za ta fi dace wajen aiwatar fusa'o'in haɗuwar tabi'u a fanni samar da horo da ilimi. Lalle, kar a manta da cewa makarantar boko, da aka gada daga mulkin mallaka ta wulaƙanta al'adu da tabi'u na Afirika. Bayan samun yancin kai, ba a samu wata makaranta ba da karɓi al'adu da tabi'u na gida da ƙasa gaba ɗaya. Cikin waɗannan halayen, ya kyautu a ce fusa'o'in haɗuwar tabi'u suna buƙatar suma su samu yancin kai (Aman, 2017).
Wata babbar manufa da rishin samun cikakkar tabi'a shi ƙaranci harsuna da tabi'u/al'adu na Afirika a makaranata. Kenan, ba a kiyaye hakkin yaro ba wanda ya ce kowane yaro yana yanci samun horo da ilimi a cikin harshensa na gida, a ƙalla a farkon shekarunsa da na shiga makarantar, duk da yake da daɗewa bincike ya bayyana mahimmanci koyarwa cikin harshen gida (Cummins, 2017). Lokaci ya yi na buɗewa harsuna Afirika ƙofofin makaranta.A 2017, wani rahoto ƙungiyar ta ƙasa da ƙasa a fanni horo da samar ilimi na UNESCO mai laƙanin « Koyarwa da koyon karatu cikin yanayi na haɗuwar harsuna » ta nuna buƙatun maida manufa wajen amfanin da harsuna biyi a makaranta a ƙasashe na Afirika ta Kudu da Sahara.

Rahoton ya karkata musamman wajen nazarin tsare-tsaren samar da horo da ilimi na Burkina Faso, Nijar, Senagal, kuma ya ja hankali wajen mahimmancin yin amfani da dalilai da suka dace ganin kasancewar akwai samfarirrika dayawa na tsare-tsaren koyarwa cikin harsuna biyu (BIE-UNESCO, 2017).Abun da ya yi saura, a ƙarfafa da yawanta su kuma a samu yardar dukanwaɗanda suke kawo tasu gudumma a fanni samar da horo da ilimi. Fusa'o'in haɗuwar tabi'u musamman a yankin Sahiyal suna iya temakawa wajen kyuatata karatun yara a cikin yankunan jahohi masu fuskantar matsi da tashe-tashen hankula. Hare-hare na yan ta'adda sun kakkaɓe da lalata makarantu dayawa. Bancin hakan, zaman lafiya da kwancin hankali tsakanin ƙabilu da addinai da aka san Nijar da shi ya taɓarɓare. Kenan akwai buƙatar habɓaka horo kan zaman lafiya ta hanyar girka shi cikin al'adu da tabi'u na gida. Yana da kyau a ce mun tattali *zumunta tsakanin ƙabilu* da ake aiwata musamman a ƙasar Kwaddibuwa (Côte d'Ivoire) kamar wata hanya da ake iya amfani da ita a Nijar.K*ulla zumunta tsakanin ƙabilu* na nufin wata alaƙa tsakanin gunguna biyu ko fiye da haka na ƙabilu. Zumuntar wata dagantaka ce mai ƙwari tsakanin iyalai biyu ko gunguna biyu na ƙabilu, da aka girka bisan kan wata yarjejeniya ta aure ko aurace-aurace. Yana ba mutanen cikin iyalan damar zaman dindin cikin yan'uwantaka da junansu.Zumuntar tsakanin ƙabilu a ƙasar Kwaddibuwa ko « Tukpe » wata yarjejeniya ce ta zaman lafiya da ake sanya hannu a kai tsakanin uwaye da kakani na ƙabilun dabam-dabam na ƙasar. Tsarin yana dogaro da tabbastaka, kuma bada damar tattalin zaman lafiya da cuɗaya tsakanin al'umomi ?Kula zumunta tsakinin ƙabilu yana bada damar yin wasan tabbastaka waɗanda suke da amfani saboda zoleya tun da dole ka amince ba tare da ka ɓata rai ba bisa zoleyar da ake wa al'adarka ko tabi'arka :

> « Kulla zumunta tsakanin ƙabilu ya dogara da canhe-canhe, almara ko wani tsari. Wannan zumunta ko ta hanyar rantsuwa ko tabbastaka, wata yarjejeniya ce da ake yi bayan rikice-rikice da kuma shaida ba za a ƙara shiga cikin irin wannan hali na zubar da jinin juna. A hakan ana dogara da wasu halaye nagari kamar su ƙawantaka da zumanci, tabi'u da suke iya sanya a samu tsakanin masu zumuncin halaye na zaman lafiya da rishin tashin hankali da yafayya da suke kawo kwanciyar hankali. Waɗannan sune halaye na samar da zaman lafiya da kuma tattalin daidaiton al'uma »(Insiata, 2013).

A ƙasar Sengal misali, tsakanin ƙabilun Serar da Fulani, akwai wata tabi'a wasan tabbastaka. Baseraye da bafulatani suna ɓacin juna cikin wasa ko da a rana ɗaya suka taɓa gamuwa. Kowane yaceabokin wasan nashi shi ne « bawanshi » cikin wasa da dariya. Wannan tabi'ar ta zamantakewa cikin wasa, zolaya tsakanin ƙabilu dabam-dabam kariya ce ta ƙabilanci kamar yadda bincike a fannin nazarin halayar ɗan Adam da na zamantakewa yana nuna.

Ko da tsarin samar horo da ilimi na ƙasar Nijar yana da wasu matsaloli da suka fi fusa'o'in haɗuwar tabi'u kamar ƙarancin azuzu da kayan aiki ko ƙaranci horo na malamai, bai kamata ba a manta da al'adu da tabi'u da harsunan gida ba a share idan za a sabinta ko kawo gyara ga tsarin samar horo da ilimi a nan gabaa. Batun karɓar tabi'u da al'adu a makaranta a Nijar ya ƙi zama cikin kanun mutane saboda an fi son a je wurin abun za haɗa mu. Inganci, juriya da hazaƙa sun fi samuwa ta hanyar ƙarfafa ire-iren al'adu da tabi'u a makaranta a Nijar.Wannan mafita tana da kyau saboda wasu daga cikin jahohi suna fama da tashe-tashen hankulla

**3. Horo/Tarbiya kan yanƙasanci : A ƙaƙarfa girkuwar yan Afirika**

Don a ba yara manya gobe a Nijar da Afirika gaba ɗaya dama zama al'umomi na cuɗayya, ya kamata a sauya fusa'o'in horo kan yanƙasanci a cikin makarantu ta mahimman hanyoyi biyu : (1) a wuce horo na gishin ƙasa (2) a aikata horo kan yanƙasanci a duniya ta hanyar dogaro da abubuwa da al'adu da tabi'u namu na Afirika suka kawo wa wannan kalma ta ƙasa da ƙasa da ake son ginawa.

A da ana tunkarar yanƙasanci a makaranta tamkar wani irin horo a fannin kishin ƙasa. Akasarin lokaci ana yi wa yan makaranta bayani kan kundin tsarin mulki, tafiya da tsarin hukumomin siyasa da hakkoki da abubuwan da suka rataya a wuyan da ƙasa. Jadawalin koyarwa na ba da wani ɗan lokacin don gudanar da darasin. Ya kamata mu wuce wannan tsarin na darasin yanƙasanci, zuwa ga mahimman batutuwa da suka shafi rayuwa ta yau da kullum a makaranta da cikin al'umaKenan halartar yan makaranta wajen tafiyar da rayuwa a makaranta za ta ba su damar yi bayani da gwajin kalmomin da tabi'u kamar su demokaraɗiya, canjinmulki, bambance-bambance, hakkoki, abubuwan da suka rataya a wuyansu, kulawa da muhalli da tattaunawa ta canjin ra'ayi

A wani fanni, ya kamata wajen samar da horo a kan yanƙansanci a yi bayani a kan dalilan tushen sauye-sauye da aka samu daga shigowar fusa'o'i na zamani na sadarwa (TIC). Yana da kyau a ƙarfafa a ƙananan makarantu da makarantu na sakandare ƙoƙarin yan makaranta na ganin su tsunduma cikin yanƙansanci na ƙasa da za ta haɗa abubuwa da yawa, da suka haɗa da iya tafiya da yawan ƙabilu, yawan addinai na yanki da na gaba ɗaya (Sagayar 2020). Lalle, kafofin watsa labarai na zamani suna taka rawar gani cikin al'umominmu inda suke kawo sauyin na halayenmu na tunkara rayuwa da ta shafi ayukkanmu da kuma alaƙa tsakaninmuda wasuAmfani fusa'o'i na zamani cikin hankali da fahinta ya zama dole cikin yanayi na rishin tsaro, kamar a Nijar inda akwai gungunan miyagun masu tsattsauran ra'ayinn ta hanyar sadarwa da kafofin watsa labarai suke iya janyo hankalin matasa na gari. Ya kyautu a ƙarfafa dubaru na horo da za su taimaka wajen riga-kafi, kamar misali « ayukkan waye-kai dangance da yankansanci wajen amfani na'unar zamani ko yadda za iya amfani Yanar gizo ta hanya mai kyau da kuma wasu daga cikin kafofin sadarwa musamman ƙididdige mugun saƙo ko saƙo na banza da kuma tsira wasu shififfuka na sadarwa na tattaunawa da fahintar juna » (UNESCO, 2017, pp. 54-55).

Horo kan yanƙasanci a faɗin duniya shi ma hanya ce mai kyau da ake yi nazari a kai (Akkari & Maleq, 2020). Wannan kalma akwai ta matsayin Guri na 4-ƙudiri 4.7 na kundi na ƙasa da ƙasa 2030 na samar da horo da ilimi :

> *Nan da 2030, a yi yadda dukan yan makaranta za su samu sani da ƙwarewa isassu da su ba su damar bunƙasa ci-gaba mai ɗorewa, musamman daga horo kan ci-gaba da kuma halaye na rayuwa masu ɗorewa.da hakkoki ɗan Adam, da daidaito na jinsi, da bunƙasar tabi'a ta zaman lafiya da rishin mugunta, da yanƙasanci a faɗin duniya, da amincewar bambanci tabi'u da kuma gundummawar tabi'a da al'adu wajen ci gaba mai ɗorewa.*

*Cewar UNESCO, Horo kan yansanci a faɗin duniya wani salo ne na horo inda « yan makaranta suke gano cuɗayyar juna, hulɗa a faɗin duniya da kuma gungunanta dabam-dabam na al'uma. Suna koyon yadda za su ƙarfafa da kuma girmama cuɗuwa cikin yawa da bambanci, kuma su samu ƙwarewa, da iyawa, halaye da su ba su damar bada tasu gudummawa wajen gina al'umomi cikin cuɗayar yawa da bambance-bambace kuma su walala. Amma, kafin nan, horo kan yanƙasanci a faɗin duniya yana son a kama juna da kuma ganuwa da dukkan yan adam cikin ƙasarka, bayan iyakar ƙasarka da kuma ayukka nagari da su iya kawo sauyi » (UNESCO, 2017, pp. 38-39).*

Idan aka gabatar da mahimman matakai da ake samu cikin kowace tabi'a da suke bada damar gano cewa dukkan mutane guda ne, horo kan yanƙasanci a faɗin duniya yana shika cikin darussan makaranta. Waɗannan matakan da ake iya tsarawa ko da dabam-dabam kuma a gabatar da su da wani suna kamar *« horo a kan tabi'u na zaman lafiya »* ko*« koyo rayuwa tare »,* suna ƙarfafa juriya da sabawa yara da matasa kuma suna sanya a samu wasu halaye na amincewa da tabi'unka.Gurin shi ne na haɓɓaka yancin faɗin albarkacin baki ga dukkan yan ƙasa da kuma cikkaken yanciccikansu. Hakan yana son a ƙarfafa sauye-sauye fusa'o'in koyarwa ta hanyar daidaita su da yanayi dabam-dabam na ƙasa, da horar da masu bada horo da malaman makaranta kuma a janyo al'uma da uwayen yara cikin har da iyalai wajen kawo wannan sauye-sauyen na zamantakewar al'uma.Muna ganin Afirika tana da wani ƙwarin gwiwa na girka horo kan yankasanci a faɗin duniya cikin tarihinta da al'adunta na gargajiya. Misali, Usular Manden da take ɗauke da saƙo na girmamawa, ƙauna, ƙawance, da ake ta yabawa shekaru aru-aru na ƙarni *« na bada manufofi da hanyoyi kan yadda za a tafi da wasu tabi'u da al'umomi cikin girmamawa da kwanciyar hanakali, masu nuna mahimman kalamai na horo kan yankasanci a faɗin duniya, cewa da girmamawa al'adu/tabi'u da zumunci »* (UNESCO, 2018, p.3). Duk da yake Usular ba a rubuce take ba, ta ƙunshi batutu kamar kalmomi na girmama rayuwar ɗan Adam, yancin rayuwa, matakan daidaito da na rishin wariya, adalci, gaskiya da zumunci, da aka samun daga tarihin baka. Wannan usular ta zo da bayanai na zaman lafiya al'umma cikin amince da tabi'u, halin na rishin tauye rayuwar ɗan Adam,da kuma horo, ɗayancin ƙasa , tanadin abinci da yancin faɗin albarkacin baki A wajen wani taro tattaunawa ta ƙasa da ƙasa na ƙarfafa ƙwarewai ma laƙanin *« A bunƙasa horo kan yanƙasanci a Afirika ta Yamma »*da aka tsara a 2015, da ya haɗa ƙasace goma sha biyar na **kunyiar tattalin arzikin ƙasashen Afirika ta Yamma** ( CEDEAO), an gano cewa babu bambanci tsakanin *kalmomi na yanƙasanci da na horo kan yanƙasanci a faɗin duniya.*Kasashe mambobin Kungiyar da suka halarci taron sun samu ƙwarin gwiwa waye kan masu ruwa-da-tsaki da kafofin sadarwa a fanninhoro kan yanƙasanci a faɗin duniya da su ƙarfafa sanin malaman makaranta, masu bada horo, kuma a bada horo zuwa ga masu faɗi-a-ji da hukumomin kula da ilimi, jagororin makarantu, marubuta litattafai da kayan aikin koyarwa.An bada shawarwari bunƙasa shafiffuka sadarwa na koyo daga nesa cewa da « e-leraning » a turance, don ganin a ƙarfafa amfani da fusa'o'i na zamani (TIC) kamar wata madogara koyarwa ta horo kan yanƙasanci a tsari na duniya. An kuma ƙara wa mahalartan taro ƙwarin gwiwa wajen yaɗa kyakkyawun halaye da sabbin fusa'o'i da kuma halartar al'umomi (UNESCO, 2015). A ƙarshe, muna tsammanin tunani ko nazari a kan buƙatar daidaita horo kan yanƙasanci da yanayi a

Nijar da Afirika gaba ɗaya, a gudanar shi cikin tsari na horo a kan al’adu da tabi’u na Afirika kuma a kiyaye amfani dalilan da matsalolin irin na waje. Musamman ma, a bunƙasa hakkokin yan tsiraru, horo na kama kai. Ya kamata a yi aiki da yanayi na ɗan Nijar idan ba a son samun saɓanin gurin da ake son cimma. Kamar yadda Pelizzaru (2020) ya ayyana, yana kamata nazarin haɗin tarbiyar makaranta da hakkokin ɗan Adam ta hanyar nazarin mai zurfi na rayuwar da tabi’un ɗan adam.

**4. Kalubalen tarbiya dangance da sabbin fusa’o’i**

A fannin bunƙasar sabbin fusa’o’i, ya kamata a yi nazarin yiyuwar saɓanin da za su iya janyowa tsakanin ɗa’a da aka samu daga yanar gizo da ɗa ta zahiri daga al’umomin Afirika. Tabi’u da fusa’o’in suke yaɗawa, da kuma su nuna ire-ire misalan tabi’u na waje, na iya kai wa nesa tsakanin abubuwa da ake gani kamar na *zamani* da *al’adun gargajiya da uwaye da kakanni* da kuma al’umomi na Afirika.Sabbin fusa’o’in suna iya kawo tangarda ga dangantar iyalai da kuma alaƙa tsakanin matasa da duk wani abu da zai kawo tikas ga tsarin al’uma da gargajiya. Yana da kyau a ce an bunƙasa wani tunani a kan amfani da sabbin fusa’o’i na sadarwa (TIC) musamman ma a tsakanin matasa da suke fuskantar waɗannan abubuwa da suka zaman ruwa, dare gama duniya. Hukumomin ilimi suna taka mahimmiyar rawa wajen ganin an ci moriyar sabbin fusa’o’in ta hanyar samar da kyakkyawar manufa ga matasa cikin wannan lokaci da ba ya da tabbas. Amfani da sabbin fusa’o’in zaman na iya taimakawa wajen bunƙasa tsare-tsare na samar da horo da ilimi ta hanyoyin da za su bada damar fahintar daidaita matsayin tarbiyar gardajiya, sauyi da ake buƙata a halin yanzu. Shekaru da dama, makarantun boko sun taka rawar gani wajen samar da sani da ilimi da ake buƙata na aiki da na rayuwar al’uma. Sai dai gaugawar bunƙasar fusa’o’in na’ura yana ba makarantu wahala ganin yadda abubuwa suke tafiya musamman wajen samin zafafan bayanai da sani.Ana ɗaukan sabbin fusa’o’in tamkar wata hanya da za iya bunƙasa ilimi da tarbiya zuwa ga mutane dayawa kuma kamar wata hanyar warware matsalar tarbiya cikin yanayi na yawa. Matsalar ba ta yawa ba ce ko sabinta kayan aiki da ke akwai a makaranta. Abu mai mahimmanci shi ne yadda za a yi amfani da kayan aiki da kuma gurin da ake so a cimma da su. Don haka ya kamata malaman makaranta su samu horo don su daidaita ayukkansu da zamani na ƙarni na XXI, kuma kar horo ya tsaya a iya na’ura ko sanin fusa’ar koyarwa. Ana son ƙarfafa sanin malaman a kan fusa’o’in koyarwa da za su kowo sauyi ga aikinsu na masu koya tarbiya. Kuma dai, ya dace a san da cewa yaɗuwar TICE tana janyo matsalolin tafiyar da mulki da ta danganta da lamura na daidai da rishin wariya. An gano da cewa lokacin allobar korona cewa da Covid-19, mutanen da suke fuskantar wariyar su ne, rufe makaranta ya fi addaba saboda rishin galihu ko wahalar cin moriyar honyoyin da suke bada damar samun ilimi daga nesa (UNICEF, 2020).Rishin rezo/konakso na yanar gizo, wutar lantarki, na’urar aiki, rishin hali na iyalai da suke rayuwa cikin yanayi da ba ya bada damar samun ilimi daga nesa, sun ƙara bambanci cikin al’umar yan makaranta. Cikin wannan yanayi, alloba ta ƙara yawan bambace-bambace tsakanin iyalai, yan makaranta, jinsi, ɗalibai, malaman makaranta, makarantu, tsakanin marantar gwamnati da ta biya, tsakanin tsari da tsari na koyarwa. Waɗannen bambace-bambace sun danganta da halin iyalai, jinsi, matsayi na ƙaura, shekaru, mazamnar yan makaranta (maraya ko ƙauye) da ɗalibai da kuma halin na

azuzuwa da kayan aiki (samun lantarki, Yanar gizo…) da ci-gaba a fannin tsare-tsaren koyarwa.(Igodoe & Lange, à paraitre

**5. Kammalawa : mahaɗa tsakanin mamayar tabi'u na sauran duniya da tabiyar Afirika da aka daidaita**

An buɗe wa tabi'u na sauran duniya kofar mamayar tarbiya a Afirika tun lokacin mulkin mallaka har bayan samun yancin kai. . Wannan ƙofar tana amfani kuma za ta ba nahiyar dama shiga yanayi na duniya. Sai dai muna ganuwannan buɗe kofar bai gyara Afirika ba saboda ya lalatar al'adu da tabi'un AfirikarWannan babi ya nuna cewa duk da ci-gaba da aka samu a fanni dokoki na ƙasa da ƙasan akwai giɓi babba tsakanin *alkawarra na gwamnatoci* kan hakkoki yaro a Afirika da kuma *abubuwa da ake gani a zahiri*. Tun da daɗewa aka yaƙi aikin yara cikin yarjjejeniyoyi na ƙasa da ƙasa amma yar yau matsalar tana nan cikin ƙasahen dayawa na Afirika da yawanci suke fama da tallauci. Daidaito tsakanin yarinya-yaro bai je ko'ina ba, kuma ba a samu wani sauyi ba cikin sayasar jama'a. Ko da yake an samu raguwar aure yara da kaciyar mata, wannan tabi'a ta girku cikin al'adun wasu al'umomi inda take ci gaba da haddasa matsalolin kiwon lafiyar jiki da na hankali ga miliyiyikan yan mataA gano cewa, idan ana son shirya yara zuwa ga manya gobe a Nijar kai har a ma a faɗin Afirika zuwa ga al'umomi da za su haɗa tabi'u dabam-dabam, ƙarfafawar tarbiya cikin haɗuwar tabi'u da fusa'o'i na horo kan yanƙasanci ( tabi'u duniya) tana da mahimmanci. Hakan zai taimaka wajen ƙalubalen halin matsuwa da mutanen yankuna dabam-dabam suka samu kansu a cikiSabbin fusa'o'i na zamani suna iya taka mahimmiyar rawa wajen bunƙasa al'umomi da ƙofarsu take buɗe kuma masu bin tafarkin demokaraɗiya, amma suna janyo matsaloli na wariya da mamaya daga halaye na waje cikin irin wannan yanayi. Ingancin tarbiya yana da mahimmanci wajen samar canji don girka al'umomi marasa wariya kuma mai zaman lafiya. Don cimma wannan guri, yana da kyau malaman makaranta su san abubuwa da darussa suka ƙumsa da kuma dubaru da za su taimaka musu don su ƙarfafa ƙwarewa da za ta ba su damar samun canje-canje.Wannan babi da yake cikin wani ɓangare na wani littafin koyarwa, yana iya zama wani kayan aiki na zahiri wajen wayar da kai, wandan daga baya, za ya ƙarfafa ingancin ilimi a Nijar. Za a fasara shi cikin harsunan guda huɗu na ƙasar Nijar da kuma masu horar da malaman makaranta suke iya amfani da shi, har ma malaman da suke cikin jahohin tsarin ya shafa. Littafin na iya taimaka musu wajen daidaita abun da ya ƙunsa da abun da al'uma ta fi so. Wannan nazari ya kasance wani kayan aiki na ci gaba da horo na malaman makaranta da za suke iya kusantar matsaloli don ƙarfafa ingancin tsarin samar ilimi da ya danganta da buƙatu da cikakken sani ya yi daidai da yanayinsu. Halartar yan makaranta, malamansu, uwaye wajen girka makaranta da al'uma da take neman sani (Bougma &al. 2021) shi ne mahimmin mataki na bisan hanyar ƙarfafa ingancin ilimi a Afirika

**Madogara**

Abebe, T., &Bessell, S. (2011). Dominant discourses, debates and silences on child labour in Africa and Asia. *Third world quarterly*, *32*(4), 765-786

Adepoju, A. (Ed.). (1993). *The Impact of Structural Adjustment on the Population of Africa: the implications for education, health, & employment*. London: James Currey.

Akkari, A., & Maleq, K. (2020). *Global citizenship education: Critical and international perspectives*. Cham: Springer.
Akkari, A. & Sagayar, M.M. (2021). L'éducation dans les situations d'urgence en Afrique de l'Ouest : Contexte, solutions expérimentées et alternatives possibles. *EDUFORM AFRIQUE MAGAZINE, Edition I*, Février 2021.
Aman, R. (2017). *Decolonising Intercultural Education: Colonial differences, the geopolitics of knowledge, and inter-epistemic dialogue*. New York: Routledge.
Benson, C. (2020). An innovative 'simultaneous' bilingual approach in Senegal: promoting interlinguistic transfer while contributing to policy change. *International Journal of Bilingual Education and Bilingualism*, 1-18.
BIE-UNESCO. (2017). *Teaching and learning to read in a multilingual context: Ways forward for three sub-Saharan African countries (Burkina Faso, Niger, Senegal).*Genève: BIE-UNESCO.
BIT. (2002). *Un avenir sans travail des enfants*. Genève. BIT.
Bougma, M, Dalbera, C., Gandolfi, S., Meyer-Bisch, P. &Ouedraogo, G. (Eds.). (2021).*Participer à une société qui apprendManuel méthodologique pour observer les réalisations du droit à l'éducation en tant que droit culturel*Geneva: Globethics.net&Fondazione VittorinoChizzoloni.
Hyden, G. (2017). The decentralization experience in Africa: beyond donor-driven approaches. *AfricaReview*, *9*(1), 98-114.
Igodoe, A. & Lange, M.-F. (à paraitre). L'impact de la Covid-19 sur les inégalités scolaires dans l'espace francophone. *L'éducation en débats : analyse comparé, 11*(2), …-…..
Insiata, G. (2013). Les notions du vivre-ensemble dans les manuels scolaires de l'enseignement de base en Côte d'Ivoire et leurs perceptions par les acteurs. *McGill Journal of Education/Revue des sciences de l'éducation de McGill*, *48*(1), 115-129.
Kola, É. (2017). Idéologie des droits de l'enfant et réalité en Afrique subsaharienne, quels paradigmes mobilisateurs?.*Éthique en éducation et en formation: les Dossiers du GREE*, (3), 69-83.
MallamGarba, M. (2004). Education bilingue au Niger: entre convivialité et conflits linguistiques. *Penser la Francophonie, Concepts, actions et outils linguistiques, Actes des Premières Journées scientifiques communes des Réseaux de chercheurs concernant la langue*, 455-471.
MCAPLN. (2010). *Document cadre de mise en œuvre de la stratégie du "faire-faire" au Bénin*. Porto Novo : Ministère de la Culture, de l'Alphabétisation et de la Promotion des Langues Nationales.
Moody, R. K. (2020). Women human rights defender's fight against female genital mutilation and child marriages in Africa. *Cities & Health*, 1-6.
Pelizzari, E. (2020). (Ed.). *Education scolaire, droits humains, laïcité : quelle place pour la jeunesse en Afrique de l'Ouest ? Analyses socio-anthropologiques à partir du cas du Mali*. Paris : Harmattan.
Sagayar, M. M. (2020). Citizenship Education in Niger: Challenges and Perspectives. In *Global Citizenship Education* (pp. 89-98). Springer, Cham

Schneuwly, B., Daghé, S. A., Leopoldoff, I., Cordeiro, G. S., Thévenaz-Christen, T., &Toulou, S. (2019). Teaching and Learning to Read and Write in a Multilingual Context: Burkina Faso, Niger, and Senegal. In *Improving Early Literacy Outcomes* (pp. 229-243). Brill Sense.
Stromquist, N. P., Klees, S. J., & Lin, J. (Eds.). (2017). *Women teachers in Africa: Challenges and possibilities*. Taylor & Francis.
Thomson, M., Kentikelenis, A., & Stubbs, T. (2017). Structural adjustment programmes adversely affect vulnerable populations: a systematic-narrative review of their effect on child and maternal health. *Public healthreviews*, *38*(1), 13.
UNESCO. (2015). *Promouvoir l'éducation à la citoyenneté mondiale en Afrique de l'Ouest. Atelier international de renforcement de capacités des pays de la CEDEAO*. 7 –9 Juillet 2015. Dakar : Bureau régional de l'UNESCO à Dakar.
UNESCO. (2017). *La prévention de l'extrémisme violent par l'éducation : Guide à l'intention des décideurs politiques*. Paris : UNESCO.
UNESCO. (2018). *Education pour la citoyenneté mondiale : pour une approche locale*. Paris. UNESCO.
UNICEF. (2020). *COVID-19: Are children able to continue learning during school closures? A global analysis of the potential reach of remote learning policies using data from 100 countries.* New York. UNICEF,

**Babi na 2**

**Ɗimbin arzikin dabarun koyarwa na Kur'ani**

**Bouba ADAMOU**

**Taƙaitawa**:

Wannan babin da muradin yin nazari kan tsarin koyar da ilimin Kur'ani domin ya zama tushen dacewa kuma mai inganci ga makarantun gwamnati nayau a cikin yanayin ƙasar Nijar.Domin haka an yi nazarin ilimin koyar da karatun Kur'ani ta hanyoyi dabam-dabam da kuma canje-canje da ya samu na tsawon lokaci a cikin wannan yanayin. Nazarin yana maida hankali kan Kur'ani a matsayin hanyar koyarwa, madogararkoyarwa da na harshe. Har ila yau, binciken ta dogara kan gudunmuwar dabam-dabam da ilimin Kur'ani yake kawo wa wajen bunƙasa basirar ɗalibbai kafin gabatar da kacici-kacicin a aikace wanda malamman da masu bada horo za su iya amfani da su a cikin darusan koyarwa-koyo na darussa karatunmakarantu.

**Mahimman kalmomi**Kur'ani, gundummawar dubarar koyarwar da na madogarar koyarwa, makaranta, Nijar

GABATARWA

A Jamhuriyar Nijar, makarantar ƙur'ani ta ƙumshi ɗumbun albarkatu na al'adun gargajiya da suka rarrabu cikin kowane fannin zamantakewa tsawon ƙarni dayawa. Kwaikwayo daga gareta yana daidaita ma'anar makaranta da kuma al'adun mutanen da ya kamata ta yi wa aiki. Haka kuma na sanya yaro ɗan Nijar ne cikin hakinsa na ƙwarewa a makaranta ta hanyar fifikon amfani da ilimin baya wanda ya laƙanta kuma ya saba da sh. Hakan zai taimaka wajen kare dubban matasa daga illolin jahilci da gazawar makaranta. A bisa ga wannan jigon, wannan babin na yanzu yana bibiye da wasu manufofi guda huɗu na musamman, wato:

1) fiddo dubaru da fusa'o'in koyarwa waɗanda ake amfani da su wajen koyar da karatun Kur'ani a Nijar;2) tantance mahimman takardun da malamman ƙur'ani suke amfanida su;3) yin nazarin kayan aikin makarantun Kur'ani da kuma yunƙurin sabintawar da suka samu a cikin yan shekarun nan;4) bayyana hanyoyi masu bada damar tsaida fusa'o'in koyarwa na Kur'ani don amfanin makarantun a hukumance.

Domin cimma waɗannan manufofin, da farko binciken ya yi nazarin yadda koyarwar karatun ƙur'ani take gudana da kuma sauyin da ta samu a cikin yanayin ƙasar Nijar. Sannan binciken zai kawo bayyani kan ayyukan koyarwa da kayan aiki wannan koyarwar. A ƙarshe, babin yana ƙoƙarin fiddoƙa'idodin koyar da ƙur'ani kuma yana bada kacici-kacicin a aikace waɗanda za a iya amfanin da su wajen koyar da darussan karatun na makaranta.

## 1. Hanyoyin koyar da Kur'ani a Nijar

Baya ga makarantun madarasa da suka samo asuli daga gwamnati, a Nijar ana tantance nau'o'in koyar da karatun ƙur'ani iri-iri da za a iya karkasa su zuwa mahimman hayi biyu: Nau'o'in gargajiya da kuma waɗanda ake gani kamar na zamani. Na farkon sun kasance ƙarni aru-aru kuma an yaɗa su daga uwaye da kakanni bisa ga yardar halayen zamantakewa da siyasa ko tafiye-tafiyen malammai da almajrai na ilimin isilamiya a cikin faɗin ƙasar Nijar. Kashi na biyu ya ƙumshi sabbin fuskokin da suka koyi koyar da karatun ƙur'ani tun daga ƙarshen lokacin mulkin mallaka wanda ya haifar da sauye-sauye mai zurfi a cikin al'umma.

Karƙashin wannan  tasirin da kuma na sauyin rayuwa a halin yanzu, nau'o'ina gargajiya na koyar da karatun ƙur'ani, a wasu lokuta sun samu mahimman canje-canje  . Duk da haka canje-canjen suna ɗauke da  shaidar abubuwan da suka shuɗe.

**1.1 zurfin tarihi**

Batun  koyar da karatun Kur'ani a Nijar ya taso tun daga lokaci mai tsawo idan muka yi la'akari da cewa binciken na ƙarshen yana tafiya ƙafa da ƙafa tare da tsarin musuluntar da al'umma a sararin ƙasar Nijar (Hamani, 2007).Kafawar shahararrun jami'o'i kamar  ta Sankoreya aTumbuktu (Mali ta yanzu), da cibiyoyi dayawa na koyarwar musulinci kamar ta Agadas (tatsakiyar Nijar) ko kuma ta bayannan, ta Sayi (yammacin Nijar) sun zama tamƙar shaidu tabbatattu  na kasancewar karatun ƙur'ani a yammancin afirika. A yau baya ga"târikh" guda biyu masu iko a tsakanin masanan tarihi na wannan yankin na Afirika, saƙon Al-Maghîli mai laƙanin*Amsoshi bakwai na tambayoyin Askiya*, sun nuna  yadda aka saba dogara da doka da kuma koyarwar ƙur'ani ya zama jiki wajen masu mulki da al'ummar da suke cikin sararin ƙasar Niyar tsawon ƙarni dayawa. Koyarwarkaratun ƙur'aniaNijar yahaifarda taƙamaiman falsafarna daidai da wannanhalin. Wannanfalsafartanabayyana a mahimmance ta hanyar mamayewa da watsa sanin da aka samo daga ƙur'ani.Matsalarkoyar da wannanlittafin tana ɗauke da abubuwa masu halaye iri-iri kamar su:

-Iyaye za su iya ɗaukar shawarar bada ɗan makaranta (al'amarin ƙanananyara)kokuma shikansamaikoyon zai bada kansa(al'amarinwaɗansumatasadamanyan mutane);

-Lokuttan koyo suna da sauƙi kuma gaba ɗayasun shafi,sa'o'in farkonyini da ƙarshenshi (daga ƙarfe 5 na safe, sannan ƙarfe 8 na yamma). Lokuttan yin bita na mutum ɗaya, ƙarin kacici-kacicin ko aikin gyara sun bambanta daga samun damar ma'abutan;

- Harshen koyarwa kusan koda yaushe shi ne na al'ummar da ma'abutan suke cikinta, a kowane irin matsayi na mutanen da abin ya shafa;

- Koyarwar karatunƙur'ani an buɗe ta ga dukkan al'umma kuma kowa na iya bayar da gudummawarsa don ɗaukar nauyinta gwargwadon ikonsa;

- A lokacin rani  da yakelokacin rishin aiki,ta fuskar ayyukan tattalin arziki da suka fi girma, ɗalibbai za su iya balaguro tare da malamin ƙur'ani tare da yardar iyayensu don maida hankali gakaratun;

- Yanayin koyarwa da koyonkaratun ƙur'ani ba lallai bane ya raba malami da masu koyo da ayyukan samar da tattalin arziki;

- A cikin tsarin karatun, cigabanna mutum ɗaya ne. Malamin yana wuce kowane ɗalibi zuwa gaɓa ta gaba da zarar ɗalibin ya ƙware ga karatun baya;ana buƙatar amincin tattarawa a kowane mataki;

- Mutanen da suka sami ilimin ƙur'ani ana ɗaukar su kamar abin koyia cikin al'umma. Ana sa ran sun ƙumshi hankali a kowane hali, amadadin darajojin da suka koya daga Littafi mai Tsarki ;

- Ilimin da aka samu an sake maida shi a cikin hidimar mai koyo da kuma al'umma gaba ɗaya; wanda ya sa su zama marasa tunani da kuma ba su kariya ta gama-gari wacce ta sasu zama dindindin;

- Don haka yaɗuwar iliminmasana,ɗalibbai da takardun, kyauta ne a cikin duk karkarar.

A Jamhuriyar Nijar, hanyoyin da koyarwar mazahabar malikiyya sun kasance mafi yaɗuwa, koda kuwa wasu mazahabobin sun kasance tare da su. Tsarin koyar da ƙur'ani na al'ada an san shi da sunnan Dudal (cibiyar ilimi), wanda da ake aza tambayoyi dayawa akan aikinshi a yau (Meunier, dir. 2009). Tuni, a lokacin mulkin mallaka, gwamnati tana ganin (kuma a cikin kyakkyawan imani), wani tsarin mai wuya a daidaita shi da manufofinta. Sai kawai, yin la'akari da matsalolin da sokewar makarantar Kur'ani zai iya haifar da kuma ƙiyawar al'umma don rubuta yara a cikin " makarantar farar fata", mai mulkin mallaka ya ƙirƙiro daga 1947 wani tsarin "yarda" da ake kira Madarasa inda karanta Faransa-balarabci domin samun amincewar mutanen da aka ambata.Lallai,Madarasa tana bada darussa cikin faransanci da larabci tare da wani ɗan ƙaramin ilimin ƙur'ani zalla tare da lalataccen ilimin da akekoyarwa a cikin harsunan biyu. Makarantar ƙur'ani ta gargajiya, duk da haka, ta ci gaba da wanzuwa saboda ta ɗan dace da wasu muradaina mai mulkin mallaka wanda kuma yana ganin a cikin ta wani mugun abune wanda zai iya sanya a gane cikin sauƙi da kuma sa ido kan shugabanni masu ilimin boko. Fagenilimi a Nijar,tare da ƙirƙirar makarantun madarasa ya ƙumshi, nau'o'iuku na makarantun a jere da suka daɗe: na ƙur'ani, Faransanci da faransanci-larabci. Na biyun na ƙarshe, tare da albarkaryan siyasa, sannu a hankali suka killace na farko zuwa wani wuraren wuri. Duk da haka,makarantar Kur'anita gargajiya har yanzu al'umma tana shawarta saboda tushenta a cikin al'adun al'ummomin da gaba ɗaya suka dace da ɗabi'un musulunci.

**1.2 Makarantar Kur'ani: tsakanin gargajiya da zamani**

A cikin ƙarni na ashirin an tabbatar da koyarwar Kur'ani a lokaci guda a cikin tsofinnau'o'i na ilimi da ake kira makarantun ƙur'ani da sabon nau'i mai suna Medersa. Na ƙarshenne kawai ya samu tallafin Gwamnati tunda an yi wa makarantar ƙur'ani gadar zuwa matsayin a yau da kullum duk da kasancewarta a cikin al'umma. Wannan yana haifar da tazara ta hankali tsakanin abubuwa na zahiri gida da aka sani da abun cikin makaranta. Wannan yasa Kulibali (2010) ya ce « makarantar "zamani" ta Nijar tsari ne "nagefe», wato ba ta samun ƙarfi ko hallaci daga haƙiƙanin zamantakewa da al'adun al'ummar da take yiwa hidima.

A cikin ma'ana guda, Sow (2020) ta yi nadama cewa har yanzu,yawancin iyayen yara ba su da masaniya game da abun da makarantar zamani take koyarwa yayansu, balle su yi la'akarin

wata gudunmuwarsu cikin yabon tsare-tsare makaranta. A cewarta (Ibid), ana ganin an yanke alaƙa tsakanin muhallin da dole ne a gano,tare,dacewar ilimin da aka koyar: muhallin kafa (al'umma) da kuma muhallin da aka kafa (makaranta). Ko yaya, duk wani nisan da yakeraba al'adun makaranta da na ɗalibai zai iyakance shawarsu game da wannan (Meunier,Dir.,2009).Wanda da kyar yake wasa da yaron da ya tsinci kansa a tsaka mai wuya a tsakanin duniyoyi biyu masu zancen kurame; na al'ummar da ta riga ta watsa masa hanyar ma'amala da duniya da kuma na makaranta da ta mika shi ba tare da canza dokoki waɗanda bai san ma'ana ko amfaninsu ba.

A matakin ilimin Kur'ani, munga cewa an samu sauye-sauye sosai ya zamanto makarantar Madarasa ce ko ta karatun ƙur'ani na gargajiya na kafin mulkin mallaka (cf.Mahaman Mahabubu, 2017). Amma maye gurbi ya shafi shari'ar tabiyu.Wannan shi ne yadda za mu iya bambanta manya-manyan canje-canje: a cikin aiki na tsare-tsaren da tafiyar da ayyukansu, tsarin makaranta, darussan da ake koyarwa, hanyar biyan albashin malamai, hanyar cigaba da rarraba matakan karatu, yadda ake yaɗawa zuwa ga sauran tsarin ilimi, da dai sauransu. Yawancin waɗannan gyare-gyare sun fito ne daga hukumomin karkara. Haka kuma yakan sacewa sun fito ne daga Gwamnati ko kuma daga ƙungiyoyi masu zaman kansu bisa ga gwaji. Amma fatan da ake yi ta hanyar gwaje-gwaje dabam-dabam ya yi saurin kawar da rashin siyasa maiɗorewa, kamar yadda Mahabubu ya ce (Ibid).

A halin da ake ciki, dubban makarantun Kur'ani da yunƙurin zamanantar da su bai shafa ba suna cigaba da jan hankalin ɗimbin ɗalibai. Juyin halittarsu yana samun wahayi ne tahanyoyi masu zamankansu. Allon da yake da zai biyo baya yana bada ra'ayi game da canje-canjen daaka gani a cikin rarrabe-rarraben gudanarwar da ayyukan waɗannan makarantu.

**Allo na1:misalan canje-canjen da makarantun ƙur'ani na gida suka yi a Nijar**

| girma | tsoffin dubaru | sabbin dubaru |
|---|---|---|
| Asalin inda malamman koyarwa suke fito | Tsoffin ɗaliban makarantun ƙur'ani na gargajiya | Tsoffin ɗaliban makarantun ƙur'ani na gargajiya ko na zamani |
| Tsarin karatu a tsakiyar | madogoran kayan aikin da aka watsa : ƙur'ani, littattafai shari'a na mawallafa sananni, ds | Rarrabe-rarrabe daidai da zagayowar makarantun zamani : ƙananan makarantu, sakandare, ilimi mai zurfi |
| Gine-gine | ƙaramci(bukkoki, kara, inuwar bishiyoyi, ds) | Kayan gini tabbatacci (tol/kwano, siminti, ds) |
| Bayar da difiloma | Akwai wuya ya kasance (Tabi'a da ta fi ƙarfi da baka) | kullum |
| wuraren darajanta ƙwarewar da aka samu | A cikin haron na gargajiya kaɗai | A cikin tsarin ƙasa da na gargajiya |

| | | |
|---|---|---|
| Lokacin karatu | Dubarar tana sauƙaƙwa kuma ta danganta da daidaito tsakunin buƙata da abun da ake iya samu | Ba mai sassauci sosai ba |
| Yanayin cigaba cikin ayyukan da aka koya | Na mutum ɗaya | Cikin rukuni (ta hanyar ƙungiyar) |
| Madogaran kayan aiki | Tsayayyu, girkakku a gaba da yin nazari ta hanya madaidaiciya bisa ga matakai da kuma manufofi | Canje-canje, na ƙididdiga dangane da manufofi da kuma matakai |
| Koyon tushe da aka tsaida a kan : | Karatu da hardar ƙur'ani | Karatu da hardar Kur'ani da ƙarin wasu ayyuka. |
| Harsunan koyarwa | Harsunan gida kawai | Harsunan gida da larabci |
| Harshen larabci ya zama abun koyarwa | A hawana gaba kawai (ƙarshen karatun ƙur'ani) | Ga kowane hawa |
| Abubuwan cikin tsare-tsaren | Addini tsantsa | Garwaye : addini da maras addini |
| yiwuwar shiga tsarin ƙasa | Wuya/wahala | Sauƙi |

Canje-canjen da aka samu a rayuwar makarantun Kur'ani sun samo asali ne daga sauye-sauye masu yawa da suka samo asali daga yunƙurin iyayen ɗalibbai, Waɗanda suka kafa makarantu ko gwamnati (Meunier, 1995).Waɗannan canje-canjen sun fito ne daga canjin gine-gine zuwa nahanyoyin koyarwa. Har ila yau,suna rinjayar zaɓin hanyarkoyarwa da yiwuwar haɗingwiwa tare da sana'o'in jama'a cikin tattalin arziki na zamani. Ko yaya girman canje-canjen da koyarwar ƙur'ani ta yi, da alama yana riƙe ayyuka iri ɗaya kamar waɗanda suke cikin al'ummar gargajiya: ayyuka na zamantakewa, addini, tsaida asilin kowane mutum da na gamayya, dadai sauransu.Sai dai sauye-sauyen suna sake fuskokin yanayin tsarin ilimi a Nijar.

**Allo na 2 : Karatun yanayin ilimi da horo a Nijar dangance da ingancin jadawalai da aka sani da kuma matsayin na karatu irin na ƙur'ani.**

| | | |
|---|---|---|
| Nau'in makaranta | Daidaici da tsare-tsaren hukumomi | A dadin koyarwar ƙur'ani a cikin tsarin |

| | | |
|---|---|---|
| Na faransanci na gwamnati | E | Ko ɗaya |
| Na faransanci masu zaman kansu | E | Maras ƙarfi |
| Na faransanci da larabci | E | Tsaka-tsakiya |
| Na ƙur'ani waɗanda ƙungiyoyi masu zaman kansu da gwamnati suka gyara | E | Mai ƙarfi |
| Na karatun ƙur'ani da aka gyara ta fusa'ar masu zaman kansu | A'a | Mai ƙarfi |
| Na ƙur'ani na gargajiya | A'a | Mai ƙarfi ƙwarai |

Wannan allon ya nuna cewa koyarwar Kur'ani wata ɗabi'a ce a cikin kowane nau'in makaranta in banda Faransanci (tsarkakewa), wato wanda gwamnati ta dogara da shi.Koda awannan yanayin, makarantun Faransa masu zaman kansu wani lokaci suna koya darussan Kur'ani don biyan buƙatun iyaye. Don haka adadin makarantun da suke haɗa karatun larabawa da na addini yana ƙaruwa,musamman a cikin makarantu masu zaman kansu saboda irin wannan nau'in yana da matuƙar godiya ga al'ummar da take nuna shawarta ga makarantar zamani da za ta iya yin la'akari da ilimin ɗan lokaci da na addini na yara. Idan ba haka ba, iyalle suna shigar da yayansu makarantun ƙur'ani cikin sauƙi a cikin unguwoyi a lokutan da makarantar zamani ba ta mamaye su ba.Wani lokaci yaran suna zuwa makarantar ƙur'ani da sassafe maimakon su zo "makarantar fararfata". Dole ne a fahimci a cikin wannan hali cewa ainahin buƙatar ilimi a Nijar yana gayyatar masu tsara tsarin da aka ce su wuce waɗannan hanyoyi masu ban ƙyama tare da sakamako maras kyau: gwamnati-al'ada, zamani-addini.Waɗannan masu adawa a wasu lokuta su kansanya zaɓubɓukan gwamnati sun koma baya tare da gwadin al'ummar da ya dace ya yi wa aiki. Wannan ya samo asali ne daga wani ƙaƙa-nika-yi da gwamnati ta yi ƙoƙarin ragewa a cikin shirin ɓangaren bada ilimi da horarwa (PSEF,2014-2024) wanda ya tanadi cewa: *« Kashi na farko na shirin zai bada damar kimanta gwaji a makarantun ƙur'ani da aka sabunta da nazarin sharuɗɗan yaɗa irin waɗannan makarantu cikin faɗin ƙasa gaba ɗaya »*p16.PSEF (ibidem) na fatan cewa « *waɗannan makarantu za su iya zama madadin yaran da ba su da damar zuwa makaranta saboda iyalai ba su so* » .
A matakin kowane nau'i na koyarwa inda aka yarda da Kur'ani, yana taka rawa iri-iri.

## 2. Kur'ani a matsayin kayan aiki da na koyon aiki

Tarihin karantarwar Kur'ani ya nuna cewa wannan ya san hanyoyin sadarwa guda biyu a tsawon lokaci: yanayin baka inda ɗalibaisuke hardace nassin Kur'ani a ƙarƙashin kulawar malami, da kuma yadda ake rubuta nassin da hannu ko kuma a buga shi da ƙusa (Godin).2013). Domin ilimin Kur'aniya cimma manufofinsa, malammai suna amfani da dubaru iri-iri na koyo da koyarwa.

### 2.1 Ayyukan littafi cikin koyarwa

Kur'ani ya yi magana akan jigogi dayawa waɗanda asirai na imanin musulunci suka mamaye wuri na tsakiya.

Ana nufin rukunnan musulunci guda biyar, ginshiƙƙan imani guda shida, kuma da na ginshiƙi guda ɗaya na ƙwarewa cikin ibadar da mumini yake yiwa Allah. A tsarin taƙaicewa, ana iya tare da Qardawi (2006) cewa tsarin musulunci yana iya taƙaituwa ta hanyoyi huɗu waɗanda sune aƙida (Aƙidah), ibada(Ibadat), zamantakewa (Mu'amalat) da kuma shari'a(*Charîa*). Waɗannan girmamawan sun kawo nau'o'in alaƙoƙi guda biyu waɗanda mumini yake yitsakaninsa daAllah (aƙida da ibada musamman) da kuma wadda yake tsakaninsa da mutane (girmama jama'a). Hadisin akan kyakkyawar makwabtaka (Duba hadisanArba'inna Nawawy) ya nuna cewa girma na biyu ana amfani da shi ga kasancewa da kuma ingancinsa na farko.
A matsayin tushen wannan tunani, tanadin ƙur'ani da yawa sun zo don koyawa mutum yanayin rayuwa bisa ga tunanin musulunci, asalin halittarsa, yanayi naduniya da lahira. Don haka,suna bada misalin mutanen da suka gudanar da kansu bisa koyarwar Ubangiji da farincikin da ya biyo baya; sannan na mutanen da suka zaɓi saɓa masa da kuma masibar da ta same su.Salo na juya magana dasauran, salon tattaunawa suna bada hujja akan kowane batu da aka tattauna. Malamman ilimin Kur'ani suna amfani da abun ciki na kai-a-kai dangane da ilmantarwa dahorar da mambobin al'ummominsu.Yanayin Nijar bai bambanta ba da wannan doka ba. Don wannan dalili, ana kiran malamin da ya ba wa almajiransa hanyoyin iya rayuwa, yana maida su zuwa ga tushe, zuwa abubuwan da suka gabata ko na baya da aka samu a cikin nassin Kur'ani. Duk waɗannan kayan aikin sun haɗa da dubaru don siffanta ɗan adam(Aldjazâiry, 2011) tare da dogara musamman daga koyina Annabci da aka fi sani da Sunna, wanda ya ƙumshi ayyuka, yarda da faɗar Manzon Allah (SAW) na musulunci. Na ƙarshen ya koyi,a cikin shekaru 23 na tsawon wahayin Kur'ani, ɗa'ar wanzuwa wanda ta haifar da wani adadi na ɗabi'u wanda suke ƙayyade rayuwar mummunai da hulɗarsu cikin duniya. Wannan shi ya haifar da ƙarfafa da hukunce-hukuncen shari'a, ɗa'a da zamantakewa da muke kiyayewa a yau a tsakanin mabiyanta. Don samun cikakkiyar fahimtar abinda ya shafi ilmantarwawanda Kur'ani yaba Annabi (SAW) ya kamata a maida hankali a kan wannan ba tare da fidda ido ga ilimin koyarwa wadda aka gudanar tare da ita da kuma yanayin jigogin da aka gabatar.
A mahangar dubarun « ilimin koyarwa », Kur'ani ya bada labarin yadda aka saukar da abin da yake cikinsa, ya kuma gabatar da maƙasudin hakan: *« (Mun saukar da) wani Kur'ani da muka karkasa shi, domin Ka karanta shi a hankali ga mutane. Kuma Muka saukar da shi a hankali.* »(17:106);*« …Me ya sa ba a saukar masa da Kur'ani a lokaci ɗaya ba ? »Kamar wannan ne Muka saukar da shi domin muƙarfafa zuciyarka. Kuma Muka karanta shi a hankali.... » (*25:32-33).
Yanayin sabkar da wahayi (kamar yadda malamman tafsirin sura ta 96 suka rubuta musamman) sun sanar da cewa haɗuwar farko tsakanin Mala'ika Jibirilu (wanda yake nana matsayin malami) da Annabi (PSL) lokaci ne mai wahala a gare shi. Samunayoyibiyarna farkon a sura ta 96 an yi su ne bayan wani lokaci mai wahala. Ta hanyar fayyacewa ƙwararrun masu tafsirinKur'ani(duba ƙungiyar ma'ana a ƙasa) bayan su yi nazarin wannan al'amarin da yake nuna farkon wahayin, ana iya gano muhimman dokokin ilimin koyarwa guda biyu:1) ba wanda zai iya samun ilimi ba tare da wahala ba, ba tare da sadaukarwa ba,ƙoƙari; 2) don abin da aka koya yayi tasiri,ya zama dole a samu malamin da yake jagorantar matakansa.Kamar yadda aya

ta 106 a cikin sura ta 17 ta nuna, Kur’ani ya sabko da gutsuttsure a ware domin bai wa Manzon Allah (SAW) damar haɗa wata hanyar da ta dace da saƙon da Mala’ika ya koyar da shi. Kuma an hana shi yin gaggawa don karanta sassan da Ya samu, marubucin saƙon yana bayyana kansa garantin ingancin koyon da ake ci (Koran, 75:16-18). Anan ma akwai darussa guda biyu na ilimin koyarwa da suka shafi alhakin malami (ko tsarin ilimi): Koyarwa a cikin hanzarin da ya dace, da ɗaukar matakai don kare tsarin ilmantarwa. Idan, saboda kowane dalili, ɗalibi ya ɗauki ɗabi'a wadda za ta iya shafar ingancin koyo, ya dacea gano asalin kuma a magance ta, ta hanyar magance matsalar daga tushenta. A cikin hargitsin da ya biyo bayan tsoron kada abarshi a gaban abin da za a haɗeshi, ana nufin a  tabbatar masa da sharuɗɗan da aka tattara don jagorantar tafiyarsa zuwa ga nasara. Donhaka gina amana yana da mahimmanci a tsarin koyo-koyarwa.
Nassin, ƙur'ani ya yi iƙirarin cewa bai bar kome ba a matsayin jigo (6:38). Don ilmantar da mutane, yana gayyatar su su yi tunani akan kowane abu, musamman ma abubuwa biyu kamar manya maras iyaka (cosmos) da ƙananan-ƙananan, bayyananne da wanda ba a gani, cikakke da wandan ya danganta, mai ɗorewa da mai wucewa, da sauransu. Yana kuma kiransu da su yi tunani akan abinda yake tare da su, da kuma akan nasu. Don wannan nau'in tunani na biyu, Kur'ani yana ba wa masukaratu kayan aikin kamar asalin gama gari na ɗan adam kafin a cigaba da bayanin bambance-bambancen al'adu da alaƙa tsakanin siffar jiki da hayyaci  waɗanda suke nuna mu. Nassin ƙur'ani ya jaddada  cewa waɗannan bambance-bambance ba ta wata hanya ba ma'auni ne na fifiko ko zaɓe amma bambance-bambance na zahiri da suke ba mutum damar gane ɗan uwarsa.
Bambance-bambancen launi, yanki ko asalin ƙabila, wanda muguwar  fassararsau dayawa ta sanya ɗan adam cikin wahala, saboda haka ba zai iya zama tushen halayenmu ba. Da ƙarfin wannan tunannin da yake fitowa daga “ilimin koyar da ƙur’ani” wanda Manzon Allah (SAW) ya yi nasarar kafawa, tun farkonlokacin musulunci, wata al’umma da ta ƙumshi dukkan asalin zamantakewa da ƙabilu. Don haka za mu lura a cikin manyan sahabbansa Suhayb Ba’arama,wato bature, Bilal Bahabashe, ma’ana baƙar fata mai tawali’u, Salman yariman Farisa, da dubban sahabbai larabawa da waɗanda ba larabawa ba. Ɗabi’arKur'ani, duk da haka, ta wuce waɗannan la'akaran tahanyar nuna halayen ɗan adam waɗanda dole ne kowa ya koya. Allal misali,surata 23 (aya ta 2-11) tana koya wa ma su bi muhimman halaye guda shida don samun nasara ta duniya da ta lahira: natsuwa a cikin sallah (Sallah), nisantar abubuwan banza, bada zakka, kamun kai,girmama alƙawulla/ajiya, kiyaye sallah. Sura ta 25 (aya ta63-74) ta koma ga wasu daga cikin waɗannan halaye yayin da ta ƙara wasu.

**Gida *na 1***:*Kamar yadda mai karatu zai gani,batutuwan da aka tattauna a wannan ɓangare sun ƙumshikaɗan ne daga cikin ɗumbin abubuwan koyarwar Kur'ani. Koyaya,za mu iya zago ƙa'idodi dayawa da darussan ilimi masu amfani ga al'umma. Yananufin gabatar da ƙur'ani kaɗai wanda yake tunatar da, allal misali, masu tsara shirye-shiryen ilimi mahimmancin tsaida yanayi da ayyukan shirye-shiryen ilimi. Dole ne waɗannan shirye-shiryen su kasance masu yawa, su iya fayyace wasu abubuwan ban mamaki ta yadda ɗalibin ya san ma'anar shigar da shi, abin da ake tsammani daga gareshi, abin da aka lamunce masa da sauran bayanai masu yawa. Daga wannan hangen nesa, ire-iren salon koyarwa masu ƙarfi sune waɗanda*
*suke gabatar da saƙon su a sauƙaƙekuma tare da bai wa ɗalibbai cikakken buɗe ido game da duniya.*

Kur'ani ya gabatar da kansa a matsayin jagoraga mutum (Sura 2, aya ta201). Don haka, ɗarurruwan ayoyi sun keɓe ga kyawawan halaye masu mahimmanci ga farincikin ɗan adam. Don haka ana ayyana asalin duniya a matsayin matsayi wanda manufarsa ita ce bautar Allah tare da guje wa duk wani cin hanci a bayan ƙasa. Amma wannan yana yiwuwa ne kawai idan mutanesun damu da ilimi. Don haka ne ake kiran malammai da su faɗakar da al'ummarsu a kan abun da yake mai kyau da maras kyau. Kuma an bada fifikon cancantar ilimi da mai ilimi a sassa da dama domin waɗanda suka sani da waɗanda ba su sani ba ba su zama ɗaya (Kur'ani,sura ta39:9).Don haka, jimlolin annabci sun tabbatar da cewa neman ilimi wajibi ne akan kowane musulmi. Haka nan Annabi Ya tabbatar da cewa neman ilimi dole ne ya kasance tun daga jarinta har zuwa kabari, wato a duk tsawon rayuwa.

**2.2** Aiki da ƙur'ani wajen koyarwa

Ayyukan ƙur'ani wajen koyarwa suna samuwa a matakai dayawa. Ana amfani da wannan littafi a matsayin abun dogara a lokacin koyarwarsa amma kuma ta hanyar koyar da wani ilimi na musulunci wanda ya zama tushe, matsiri da abin ƙarfafawa. Don haka ne ma kalmomin "makarantunKur'ani" da "makarantun musulunci" sukan yi karo da juna da nufin ma'ana guda. Haƙiƙa, ba za a iya tunanin ilimin musulunci ba tare da ƙur'ani ba,kuma duk wani ilimin Kur'ani yan maidawa ga karantar da musulunci gaba ɗaya.

A matakin shari'a, allal misali,an san ƙur'ani a matsayin tushen farko na dokoki na addinin musulmi (Ramadan, 1999). Don haka,yana aiki a zaman abin dogarana kayan aiki don koyar da doka da kuma gina mahawara akan duk wasu tambayoyi. Malamman shari'a suna tsamo ayoyi da tanadi daga cikin sa a matsayin hujja da suka amince ko suka ƙin amincewa da wani yanayi. A cikin tunanin ƙur'ani, wannan aikin yana nan daram koda kuwa ba batun rarrabuwa ba ne. Haka nan kuma wuri ne don (meta) wasa ƙwaƙƙwalwa kamar tunani, haddace, lissafi, iya magana da jama'a, da sauransu. Ta hanyar matsayinsa na tallafi na kayan aiki, ƙur'ani kuma ya zama cikin hulɗar ɗalibi da malami wuri don tattara ƙwararrun ma su wahala waɗanda sauran ilimin kimiyya suka fiso.

**2.3. Gudunmuwar wasu ilmomin ƙur'ani**

Kalmar « nazarin Kur’ani » tana da ma'anoni da dama tun daga koyon karatun wannan littafi zuwa matsayi mafi girma cikin wannan ko waccan kalmar ilmomin ƙur'ani. Baya ga karantawa, ya kamata a yi la’akari da salon yin karatun (tajwîd) da yake taimakawa ingantatar ma’ana da tsananin kiyaye ƙa’idodin karatun. Sannan akwai tafsirin da yake kira zuwa ga nazarin yanayin saukar kowane nassi na Kur’ani. Wannan yana taimakawa ɗalibbai su fahimci matanin kuma su gujewa wasu kurakurai waɗanda suke "basu cikin tafiyar" ta yanayin wahayin. Wannan ya kasance yana da alaƙa da gano wurin da wahayin ya sabka (Madina ko Makka). A cikin wannan akwai ƙarin nazarin alaƙatsakanin mabambantaayoyi na jigo guda, musamman idan aya ta gyara wani tanadi da aka samu a waninsa: ilimin shafewa. Tare da ɗaya ko ɗaya daga cikin waɗannan ilmomin, ɗaliban Kur’ani na gargajiya ana koya masu harshen larabci. Amma a zamanin yau, koyon wannan harshen yana farawa a shekara ta farko cikin wasu makarantu.

Tare da waɗannan la'akarin a musamman ga a bunciki ko bayanan baya, ɗalibin zai rigaya sabada samun kansa a cikin nassin Kur'ani ta hanyar rarrabuwarsa da aka sani da hanyar kasa shi zuwa surori 114 ko waɗanda suke cikin hizibi 60. Sauran nau'ikan yanke-yanke suna taimakawa ƙwararrun masu karatu su karanta Kur’ani gaba ɗaya cikin kwanaki bakwai ko ukku (Godin, 2013).

Dangane da inganci, ana samun ƙarin sabbin littattafai waɗanda suke bada dubarun tattalin arziki (dangane da lokaci) a cikin koyon karatu. Wannan shi ne lamarin madogarai dabam-dabam waɗanda wasu daga cikinsu aka ɗauke su a matsayin littafin koyarwa da harshen larabci na ƙasa a matsayin harshen rayuwa a makarantar gaba da sakandare. Kari ga wannan akwai ayyukan sabbin fusa’o’i na karkara kamar ɗan littafin "koyon karatunKur'ani a cikin zamanaiki 12" na Salifu (2010). A kowane hali, lokacin farawa zuwa karanta haruffan larabci yana buɗe hanyar koyar da surorin ƙur'ani da kansu.

**3. Nazarin Kur’ani a zaman kayan aikin koyon harshe**

A halin da ake ciki a Nijar, kusan dukkan ɗalibanmakarantun Kur’ani ba ma su jin larabci ba ne. Da farko dai, ba sa fahimtar yaren da aka rubuta Kur'ani da shi.Wannan ya zama babban nakasu a cikin fahintar umarnin Kur'ani,wanda abun cikinsa ya kasance babban maƙasudin koyo. Don shawo kan wannan matsalar harshen, malammai suna amfani da harsunangida.

***Gida na 2:*** *Koyar da iliminKur’ani dabam-dabam a tsakiyar al’adun gargajiya a Nijar na kira ga masu ilimin addini tsaurara amma kuma ga ƙwararrun masanan harshe malami. Harsunan gida, ta hanyar fassara-bayani, su ne hanyoyin wannan koyo-koyarwa. Wannan hanyar ta ɗauke da babi-babi na tushe waɗanda su ne Daga harshen mai koyo zuwa harshen Kur'ani waɗannan sun tsaya tsakanin su da hanyoyin bayyana ko yin takaici da aka yi shi don bada labarin saƙon ƙur’ani*

*Cimma manufofin sadarwa tsakanin malami-dalili a cikin Kur'ani yana samun goyon baya ta hanyar dubaru na cikawa kuma iri-iri.*
*Ayyukan Bucaille (1976) da na Mohamed (2010)har ila yau , sun nuna yadda ba zai iya yin watsi da ɗimbin ayoyin ƙur'ani da suke magana da binciken kimiyya a kowane fanni ba. Wannan ya sa nassin Kur'ani ya zama wata gada mai tasiri wajen ilimi iri-iri*

### 3.1 De la langue de l'apprenant au langage coranique

Aikin ko da a matakan binciken da ake ganin ya cigaba sosai.
Lokutan da ake bada darussa don haka sun zama dama ga koyo iri-iri: na farko horo kan amfani da harshensu sannan kuma horarwa don dacewa da nau'ikan ilimin Musulunci dabam-dabam. Suna koyon kai tsaye cikin yarensu/al'adarsu, koda kuwa rubutun Kur'ani yana "fito da su" lokaci zuwa lokaci a cikin sanin wasu gaskiya wasu lokuta masu nisa cikin tarihi ko yanayin ƙasa.Kamar yadda darusan suke biya bayan cigaban littattafan sananni, ana fuskantar wani « ilimin koyarwa da ya dogara da littattafai ». Ana amfani da shi a duk tsawon lokacin, a kowane lokaci da tafiyar. Amfani da harsunan farkon a ɗalibbai da na ilimin littattafai sun ƙumshi abubuwa guda biyu masu muhimmanci na wannan tsarin rarraba da samun ilimi.
Nazarin waɗannanlittattafai yawanci ana yin su ne da na wasu sassa na asali akan allunan katako.don sauran karatun, ɗalibin da yake so (kuma yana da abubuwan da suka dace) zai iyafara nazarin nahawu da ilimin halittar harshen larabci (nah da na Larabci).zafi). Amataki natafsirin Kur'ani (tafsiri), littafin IbnKathira ne game daJalal guda biyu suke zama farkon sa ƙafa, , duk da yawan su. Bayan haka sai tafsirin daAke ɗauka sun fi zurfafa, kamar tafsirin Suyutiy, Qurtubiy, da sauransu.
A kowane hali, ana tabbatar da kasancewar koyarwa ga duk ɗalibbai ta hanyoyi iri-iri lokacin da aka samu dama na karatu ko hardaceKur'ani. A sauƙaƙe ɗalibin yana ganowa daga malaminsa lokacin da ya dace don kusanci irin wannan ko irin wannan littafi. Hanyoyin daidaikun mutane sau dayawa ba su dace ba saboda ba bu rabuwa tsakanin makarantun Kur'ani dabam-dabam, ko tsakanin sanidabam-dabam da aka yi nazarin su: Kowannensu, tare da Taimakon malammansa, marubucin bayanan kansa

**KAMMALAWA**

Ilimin ƙur'anita san tsarin rabo wanda ya haifar da ayyuka iri-iri a cikin ƙasar Nijar. Halayen koyarwa na gaskiya musamman ga wannan yanki, waɗannan koyarwar sun samu canzawa ƙarƙashin tasirin zamani. Amma canje-canjen sun iyakance ga nau'in da tsarin koyarwa. shirye-shiryen da hanyoyin cigaba suna rike da tsohuwar tafiyarsu. Bisa la'akari da ƙaƙƙarfan shawar zamantakewar al'umma da nau'ikan abubuwan da suke tattare da ita, makarantar Kur'ani ba za ta iya zama wata taska da za a yi amfani da ita ba don kafawa da haɓaka wani tsarin ilimi wanda yake bada ilimi a gargajiyence don cigabanta. Abin da ya
Rage shi ne ayyana cikakkun bayanai masu amfani na irin wannan yunƙurin.

Wannan abu ne mai yuwuwa a cikin wata tafiyar aiki da Nijar ta sa hannu matsayin hanyar koyarwa tun da ga wasu yan shekaru. Don haka gyare-gyaren tsarin ilimi na Nijar na gaba dole ne ya bada matsayi mafi girma ga al'amuran zamantakewa da al'adu na ƙasar a cikin littattafan Makarantuidan wannan cibiyar tana son samun dacewa da inganci

**Corpus indicatif cité dans le chapitre**


Al-Maghîlî, Muhammad. (1985). *Sharia in songhay : the replies of Almaghili to the questions of Askia Alhajj Muhammad*. Oxford university press.

Ibn Kathîr, Ismail Ibn Umar (Trad. Muhammad Mahdi Al-Sharif, 2006). *Tafsîr ibn Kathîr. L'Exégèse du Grand Saint Coran.* Daral-Kutub 'Ilmiyah, Beyrouth, Liban.

Djalâlud-dîne, AlMahalliy&Djalâlud-dîne, AsSuyûtiy. (1505*). Tafsir al-Jalâleyn*.

Al-Qurtubiy, Muhammad bin Ahmad (1353-1369). *Tafsir Alqurtubiy. disponible sur* https://www.australianislamiclibrary.org/tafsir-qurtubi.htmlLeroux



Al-Maghîlî, Muhammad. (1985). *Sharia in songhay : the replies of Almaghili to the questions of Askia Alhajj Muhammad*. Oxford university press.

Ibn Kathîr, Ismail Ibn Umar (Trad. Muhammad Mahdi Al-Sharif, 2006). *Tafsîr ibn Kathîr. L'Exégèse du Grand Saint Coran.* Daral-Kutub 'Ilmiyah, Beyrouth, Liban.

Djalâlud-dîne, AlMahalliy&Djalâlud-dîne, AsSuyûtiy. (1505*). Tafsir al-Jalâleyn*.

Al-Qurtubiy, Muhammad bin Ahmad (1353-1369). *Tafsir Alqurtubiy. disponible sur* https://www.australianislamiclibrary.org/tafsir-qurtubi.html


**Références bibliographiques**


Aldjazairy, A. (2011). *La voie du musulman*. Maison d'Ennour

Al-Qardawi, Y. (2006). *La foi et la vie*. Traduction de Dabback, C. Arrissala.

Atoui, H. (1978). *L'Arabe langue vivante*. EDICEF/NEA

Bucaille, M. (1976). La bible, le coran et la science. Les Écritures saintes examinées à la lumière des connaissances modernes. Seghers.

Coulibaly, M. (2010). La formation des enseignants au Niger. Formation et profession, Avril 2010. 1(17),41-43

Draz, M.A. (1999). *Les hommes à la découverte de Dieu*. AlBouraq. Beyrouth. Liban.

Godin, A. (2013).*Les sciences du Coran*. Alqalam

Hamani, Dj. (2007). *L'Islam au Soudan central. Histoire de l'Islam au Niger du VIIe au XIXe siècle*. L'Harmatan

Hamidullah, M. (1410H). *Le Saint Coran et la traduction en langue française du sens de ses versets*. Complexe du Roi Fahd. Médine

Mahamane Mahaboubou M. S. (2017). « Recompositions et dynamiques de l'enseignement arabo-islamique au Niger : le cas de Zinder ». *Cahiers de la recherche sur l'éducation et les savoirs* [En ligne], Hors-série n° 5 | 2017, p. 75-99. Consulté le 16 janvier 2022. URL : http://journals.openedition.org/cres/3120

Mohamed, Y. K. (2010). *Gloire à Dieu ou les milles vérités scientifiques du Coran.* Le bureau de prêche de Rabwah. Riyad. Arabie Saoudite

Meunier, O. (1995). Enseignements de base, politiques d'éducation et stratégies éducatives en milieu haoussa : le cas de la ville de Maradi (Niger). In : Lange Marie-France (ed.), Martin Jean-Yves (ed.). Les stratégies éducatives en Afrique subsaharienne. *Cahiers des Sciences Humaines*, 31 (3), 617-634.

Meunier, O. (dir. 2009). *Variations et diversités éducatives au Niger*. L'Harmattan

Ramadan, T. (1999). *Être musulman européen*. Tawhid

République du Niger, Institut national de la statistique. (2012). *Recensement général de la population et de l'habitat.* INS. Niamey

République du Niger. (2014). Programme sectoriel de l'éducation et de la formation 2014-2024.

Salifou, L. (2010). *Savoir lire le Coran en 12 séances*. (2è ed. 2020). Alfurqane. Niamey

Sow, A. Z. (2020). Rapprocher le milieu institué du milieu instituant : Une mission attendue des comités de gestion décentralisée des établissements scolaires, CGDES. *Socio texte. Août 2020*. (7) 196-211

Salifu,L.(2010).Sanin yadda ake karanta Alqur'ani a cikin zama 12.(2nded.2020). Alfurqane.Yamai

Shuka, A.Z.(2020).Kawo muhallin da aka kafa kusa da muhallin kafa:Manufar da ake sa ran kwamitocin gudanarwa na makarantu, CGDES.Sociotext.Agusta2020.(7)196-211

**Rataye : wasu misalan darussan aikatawa (don daidaita su kamar yadda ake buƙata).**

**Kacici na 1 : *Madogaran aikin koyarwa na masu bada hora ga malaman ƙananan makarantu/firamare***

Daga kwamitin da aka kawo a wannan babi, wanda za ku cika da wasu takardu masu alaka,

Za a zayyana jerin takardu 10 wadanda malamai za su iya shirya darussa kan tarihin Zamantakewa da siyasa da tattalin arzikin Nijar.

***Kacici na 2: Ililimin lissafi da lissafi ga daliban firamare***

Annabi Muhammad (SAW) yana da shekaru 40 a duniya Mala'ika Jibrilu ya ziyarce shi a Karon farko.Ya rasu bayan shekaru 23. Shekara nawa yarayu gabadaya?

***Kacici na 3 : Ilimin al'umma da tarbiyya kan zaman lafiya a makarantar sakandare***

Bayan karanta yerjejeni yar Hudeybi yahda aka sanya wa hannu a tsakanin Annabin Musulunci da kabilun mushrikai na zamaninsa, sai a zana darussan adabi'a guda biyu kan Dabarun komowar zamanlafiya da aka samu a cikin wannan labari.

***Kacici na 4 : Zubin labarin falsafar amakarantar gaba da sakandare.***

Shin aiki horo ne na Allah? Ku bada amsarwannan tambayar ta hanyar zubin labari, kuma kwatanta batunku da hujja daga Kur'ani da hadissai na annabta.

**Matani na 3**

Al'adun afirika da goyan baya na uwaye a makaranta: waɗanne haɗe-haɗe ne?

**Mahamadu Moktar Abdurahamane**

**Taƙaitawa**

Wannan babin yana ambatar danganta tsakanin makaranta da iyali cikin harkokin al'adun Afirika. Da an san tun da daɗewa ce wa filaye biyu ne dabamdabam, yau iyalai da makaranta sun ƙunla dangantaka ta haɗin kai da taimakar juna saboda uwayen suna kulawa sosai da tattalin ilimin yaransu.Cikin hali na Afirika, ɗaurin kanu da ƙoƙarin zuriyar iyalai ba su sauƙaƙawa dangantaka da makaranta. Da ganin tsarin tafiyar koyawa wannan babin yana dogara da sakamakon da aka harhaɗa lokacin tambayoyin neman sani na kayan aiki a taƙaice ma na kimiya da karatu da aka samu a kewayen al'adun al'ummar Nijar. Bayan an nuna kai -_da- kawo tsakanin uwaye da makaranta tana ɗaya daga cikin ƙalubalan dindindin na harkokin ilimi, babin yana matsawa kan halayen uwaye dangance da makaranta. Haka shi ya sanya aka yi wa malaman makarantu tsari cikakke bisa sanya hannun uwaye gadan-gadan a harkoki na makaranta da ganin za ya sausauta riƙo da cin nasarar yara a makaranta.

1**. Mahimman kalmomi: makaranta, uwaye, bada-kai, sani/ilimi.**

**Gabatarwa**

Dangantaka tsakanin uwaye da makaranta ba su fasa zama ba tambayar shikashikan daba ilimi. Dangance da tarihi, makaranta da iyali filaye biyune masu iyakoki da aka kurta tsakanin bada ilimi da horo. A tsawon shekaru, an biyo ta kan «makarantar cibiyar sani » zuwa makarantar waye kanun al'umma. Da daɗewa ana ɗaukar shi kamar sarari biyu ne dabam dabam, a yau, uwaye da makaranta sun gina dangantaka ta yin aiki tare ko ta wakiltar juna saboda uwayen su ma sun fi damuwa ma da ilimantar da yaransu. Ko da yake dangantaka tsakanin makaranta da uwaye da wuya da ɗaurin kai, yau sabin manufofin sun ɓullo kai a kewayen makaranta. Tsare-tsare dayawa na makarantu don su kawo sausauci tsakanin makaranta da al'umma (Maubant da Leclec, 2008).Lokacin da uwaye su kaɗai ne a gaban makarantar yaransu ko kuma malamai suna nesa da su cikin ajinsu, ba tare da ganawa ba da sauran shikashikan tsarin, sakamakon ba ya yin armashi. Amma idon kuma shikashikan suna yin aiki tare, sa'ar cin nasara za ta armashi.

Mafi yawan ayyukan bincike bisa ilimin iyali sun nuna da uwaye masu ɗan abin hannunsu ko masu arziki sun fi kulawa da cin nasarar malaman makarantu (Asdih, 2002). Maganar malamai za ta je nesa da kusancin rashin kulawa aƙidar uwaye. Da yawa daga cikin malaman, uwaye maras «tsinkaye» sun banzata da harkokin kuma waɗanda sukeyin ƙoƙarinsu wajen harkokin ilimi suna kasancewa masumamayewa. Wakillan masu nitsattsan kai suna kwatantawa da kamar kalmomin « barin ilimi ne» (Thin.1999; perier, 2005)« uwaye masu gudu »Verba, 2006), « maras ƙoƙarin bin yaransu» (Lorcerie daCarvalo, 2002).Ta wani fanni, samun malaman makaranta sun gamu da matsalolin makaranta da kasawar iyali, masamman ma matsalolin kuɗi. Kenan malaman makaranta ya cancanta su daidaita dangantakarsu da uwayen yara tare da ƙarfafa bada ilimiga yara (Maubant da Leclerc, 2002 ; Asdih, 2012).

Tsinkayen al'ummomi a kewayen makaranta a Afirika gaba-ɗaya ya nuna gujewar makaranta da al'ummomin suke yi. Amma, yau ana ganin sosai samun amfanin makaranta daga fuskar

al'umma saboda yawancin uwayen yara suna son ilimintar da yaransu ta hanyar zamani. Amma fa, a Afirika a wani gami, a taƙaice ma a Nijar, jan jikin uwayen yara daga makaranta yana da babban mahimminci ci gabankaratu da cin nasarar makarantar yara. Da ganin haka kin, suke yin faɗi- ka-tashi don tattalin makaranta. Wannan al'amarin yana sawa a ce uwayen yara sun tashi tsayin daka don farin cikin makarantar yaransu.

An rubuta wannan babin dangance da labarun da aka tattaro a lokacin binciken kayan aiki masamman na adabin kimiya da adabi na rubuce-rubuce.Babbar manufarsa ita ce kwatancin ma'anar kawo goyon baya ga harkokin makaranta daga dogara kan al'adun gargajiya na karkara. A taƙaice shi ne:

- A ba malamin makaranta hanyoyin da za su ba shi damar sanya uwayen yara cikin ayyukansa tare da dogara kan al'adun karkara. ;
- A sanya malamin makaranta ya dogara kan al'adun gargajiya na karkara saboda uwayen yara su shiga cikin harkokin makaranta;
- A ƙayyade dubarun da suka dace da za su sanya malaman makaranta su jawo uwayen yara cikin ayyukan koyo da koyarwa

## 1. Ilimin gargajiya cikinal'adun Afirika

### 1.1 Bayani

Ilimin gargajiya ya ƙumshi nitsattsen arzikin mahalin Afirika. A taƙaice, ana gudanar da wannan bada horo ta hanyar magana tare da gani da ido da kwaikwayo, fusa'a da wasa, kaɗe-kaɗe da rawa. Ta sanya mutunta dangantaka a gaba, haɗin kai, kama hannun juna,mahimmacin ƙungiya.

Karshen bada horo cikin al'ummar gargajiya ta Afirika ya juya gaba ɗaya wajen ruƙon daidaitaka tsakanin mutum da al'umma.Babban abin da ya ɗauki hankalinsu shi ne yin jinkiri, wani lokaci ana ƙokarin tare canji (Sawadago, Duge, Rodirigez da Owaba, 19994)

### 1.2 Ilimin gargajiya da matsayin uwayen a Nijar

Ilimin gargajiyacikin al'ummomin Nijar yana cikin jerin ƙwaƙƙwaluwa amma, girmama uwayen yara a taƙaice da duk sauran samari yana tanada ƙa'idodi na tuni da yake sanya duk al'umma.Misali a Nijar «kowane samari bahaushe ba za ya bi ta gaban manyansa ba da suke zaune sai ya fitar da takalminsa », wannan shaida ce ta ladabi.Duk kamar ita ma yar budurwa ko duk kowace matar aure ma sai ta durƙusa idan za ta ba mijinta ruwa ko abinci ko a duk sauran manyan mutane don nuna girmamawa (Dauda, 1991, Shafi na 121). Kenan al'umma ce daga ƙarshe take gwada masu wannan halaye na ladabi da take bi sau-da-ƙafa (Mumuni, 1968). Kasawar jama'a ta zama don haka kamar kasawar al'umma duka ba uwayenmutunen kaɗai ba. Halayen jama'a suna ƙalƙashin tabi'a, ɗa'a wajen hausawa wannan ɗa'ar ta iya zama tabi'ar ƙwarai ko muguwar tabi'a dangance da halin mutum ta yadda ya kasance (Daouda, 1991, shafi na 121).

Duk da haka tsayayyun uwaye suna da maƙami na farkon tsari domin su ne suka gina tushen karantar da yara. Haka, uwa ita ce a farkon kawo goyon baya na yaro ta wannan take kula da tsabtarsa tun yana ƙarami kuma take ba shi gumin na masamman na waye

kai. Dangance da bambanci, ɗa na namiji, misalin al'umma ɗiya mace ya fi kusanta da uwa da take tattalinta sosai kuma take ba ta horo kaɗan-kaɗan don kai ta ga muƙaminta na mace. A bambance, a gargajiyance, matsayin uba ya shafi koyawa yaro sana'a da rayuwa cikin jama'a. Uba shi ne misali mai gudanar da sana'ar gaskiya (manomi, makiyayi, ɗan kasuwa). Ta hanyar kwaikwayo yaro yake koyon sana'ar ubansa cikin al'ummomin gargajiya na Nijar.

## 2. Bada horo a makarantar Nijar

### 2.1 Manufar ilimi

Washe garin bayan samunyancin kai, ƙasashen Afirika sun samu tsarin ilimi da horo wanda suka samu laƙamin suna tsare-tsaren koyar da ilimi na gabanin ikon mallaka. A yau Afirika ta dogara da tsarin ilimi da horo na mulkin mallaka guda shida (masu magana da ingilishi, faransanci, mutanen Espanya, Portugese, jamusanci da da Larabci).

Ta gadi mulkin mallaka daga Faransanci, makarantar Nijar kamar sauran na Afirika masu magana da Faransanci, tana ɗauke har yanzu dashaidar wannan mataki mai mahimmanci a cikin tarihinta. Tsarin ilimi da horo na Nijar yana har yanzu dogara da hanyar ƙungiyoyin na duniya da suke gudanar da zuba tallafin kuɗaɗɗe. **Meunier (2008)**yana kwatanta shiga shigi da tsarin ilimi da horo na Nijar ya tsundumu da ake magana kan « tsare-tsaren koyar da ilimi masu tafiya tare».

### 2.2 Dubarun sanya hannun uwayena yau da kullum a makaranta.

Acikin yanayin tsarin ilimi da horo a Nijar, sanya hannun iyali da uwaye ana yinshi ne ta hanyar shikashikan dokoki da manufar ilimi ta yi hasashe. Yinƙurin da makarantar ta ɗauka na faɗaɗa ilimin iyali ya bayyana irin rawar da ya kamata iyaye su taka wajen karatun yayansu. Saboda haka, uwayen yara suna da alhakin su**:**

- rubuta yara  a makaranta;
- kula da kyau zuwan yara a;
- san makaranta da matsayinta;
- san yadda ayyukan makaranta suke tafiya;
- nemi labarai sosai kan zaman yara a makaranta;
- bada cikakkin ra'ayoyi ga shugabannin makarantu bisa ga duk harkokin da suka shafi makarantar (makoma/ƙarshe, abun da suke cikinta, tafiyar da aikin koyarwa, kimanta/ƙintata, sauyi/juyi ) ;
- kawo tasu gudummuwar kuɗaɗe;
- shiga cikin tafiyar da gwamnatin makarantar.

Daga kafawarta a shekarar **1989**, ƙungiyar uwayen yan makaranta da ake kira APE ta saita waɗannan manufofin:

- gangama uwayen yan makaranta  saboda su jagoranci ayyukan da suka kewaye makaranta;


- girka tare da kiyaye tsakanin malamai, yan makaranta da shugabanni, yanayin gane wa juna;

- kawo gudummuwa wajen inganta halayen rayuwa da aiki a makaranta;

-sanar da uwaye harkokin koyo da koyarwa, bada ilimi da bada horo;

Bayan ƙungiyar uwayen yan makaranta (**APE),** an kafa ƙungiyar uwaye mata masu tarbiyantarwa **(AME)**a watan nobamba na shekara ta **2005.** Dangane da miƙa mulki ta fuskar bada yanci ga karkara, an kafa kwamitin kula da makarantu a matsayin tsari ingantacce cikin makarantun(COGES).

Bayan waɗannan siffofi na gwamnati, ya cancanta uwayen yara su tsara kansu dangane da kusacin karkara don su kawo gudumuwa ta kiyaye de ci-gaban ayyukan makaranta a misalance idan wata matsala ta taso ko wani bala'i na yanayi. Ana iya wakiltar mambobin dabam dabam da dubaru iri-iri na sa kai a gewaye da makaranta Nijar da wannan zanen:




**Tarifi** :

**: Mu'amala ta ƙut da ƙut tare da matsa lamba ga shugabanni daga al'umma.**
**: kaɗan ko rishin matsi amma yau da kullum tare da ƙarancin matsin lamba na zamantakewa**

Wannan hanyar ta sanyaa shirya shugabanni da suka shiga cikin gudanar da harkokin ɓangaren makaranta cikin ruƙunai biyu, daga dangantakarsu da makaranta. Haka nan, waɗansu suna da sauƙin gyarawa domin halinsu na garí (Gwamnati da ƙungiyoyin farar hula). Waɗannan suna da hulɗa da makaranta ta halin yau-da- kullun amma da ɗan matsi kaɗan. Matsawarsu zuwa ga makaranta ta zama ragagga. Waɗansu sassan (ma'aikatu masu zaman kansu,puruje da ƙungiyoyi) suna iya kalkasuwa cikin ruƙunin ma'aikan masu kawo yar ƙaramar gudumuwa. Kusa da waɗannan ma'aikatan farko, ana samun wasu kuma kamar iyali (uwaye) tare da hulɗar yau –da – kullum, mai ƙarfi, matsattsu da masu wuya da game da makaranta. Zanen ya

bayyana ƙayyadaddun ƙokarin iyaye (ma'aifa ko uwayen gida) na ɗan makarantar a cikin aikinsa na neman ilimi. A taƙaice dai, kibiyoyi suna nuna matsattsinuwaye game da makaranta, ko kan malamai kobisa yan makarantar, kobisa duka biyu don ba na farkon damar gudanar da ayyukansu da kyau da kuma na biyun su ci nasara da kyau bisa kan neman iliminsu. A zamanin da wani ƙalubalai ya ɓullo kai a makarantar, a samu labari daga malamai ko a'a,uwayen yara ko wakilan ne za su ɗauki matakai da bin hayoyin shawo kansa. Da dama, dangance da iren ƙalubalen, za su juya wajen sassan dabam dabam (APE, AME, COGES) da waɗansu rassan gargajiya (Maigari) ko na addini(Iimam).

### 3. Wakillan al'umma a gewayen makaranta

A Nijar, mutane yan kaɗan ne suke da damar shiga makaranta kuma iyalai dayawa; duk da ƙoƙarin masu kulawa da harkokin, suna yin shakka wajen rubuta yaransu a makarantar. Uwaye da dama cikinsu suna ganin kamar makarantar ta annasaru ce kawai, ba su ganin wata ribar da za su samu haɗe da tunaninsu a fuskar makarantar, suna guje wa wannan salon neman ilimin.Ta wani halin sun fi gane wa makarantar karatun Kur'aniga duk sassan al'umommin Nijar kuma suna zamahalayen nanuna ƙin yardada makarantar faransanci **(Barreteau &Tiné, 1999).**

...matsalar makarantarmu ita ce baƙuwa ce. Wannan ba makarantar Nijar ba ce….Idan har tsare-tsaren/ jaddawalan ba su danganta ba da haƙiƙanin gaskiya ba, al'adun ƙasar, tarifin ƙasar,wayewar ƙasar, manufofin da ƙasar ta sanya gaba, gaskiya, ƙasar da yanayin,to tabbas za su watsi da su.Allal misali ɗan ƙaramin Bature da yake cikin makarantar paramari da wuriyana tunanin abin da za ya yi. Muna ganin ƙananan yara suna ƙera abubuwan shawa saboda tsarinsu ya riga ya ba su damar aiwatar da kansu a nan gaba. A nan, kammala karatun jami'a wani kolaci yana nufin zuwa zaman kashe-wando. Ya kamata Jami'a, ta horar da mutane masu ra'ayi da daidai da haƙiƙanin gaskiya, mahangar ƙasa.

**Pr Djibo Hamani, Historien, AIR INFO, 26 septembre 2018.**

A yanayin da al'ummar Nijar take ciki a halin yanzu, bambancin al'amuran zamantakewar al'adu sune mayan dalilan da suke haɗe da rishinshawar uwaye dangance da makarantar boko. Makarantar boko ta Nijar, wadda ta yi gadodaga makarantar turawan mulkin mallaka ta Faransa, tahadasa da ɓaraka tsakanin yaro da kewayen iyali, al'ummomi da addini **(Moumouni, 1968).**Bisa wannan ma kasawar ilimi ya ƙaru ganin haka ɗin su ne dalilan da aka kwatanta don a bada bayani bisa kan rishin shawar makarantar boko:

« Makarantar boko tana haifar da alfadarai.Kangayen tanunuwa. Amma na aminci da duk muna da laifi. Gwamnati yana da nasa babban laifi, gaskiya ne, ammababban kashin yana gare mu a matsyinmu na uwaye! ».**(Shugaban komitin gudanarwa na wata makaranta a Agadas).**

«Bayan shekaru uku na yin makaranta, ina jin ciwo a game da matakin karatun ɗiyata.Ba ta kama da yar makaranta. Ba ta iya

karatu ko rubutu ba. Ban san abun da za na yi ba », a faɗin Fatuma, wata matashiya uwar iyali. Kamar don ya goya mata baya Alhaji Ama, uban wani ɗan makaranta yananata: "makarantar yanzu ba kamar ta da ba ce. Muna ja da baya kuma babu wanda ya san yadda za a meƙe sandar makarantar da ta kifewa ».

Wani sabon dalilin makarantar duk da haka an lura da shi a ɓangaren al'umma a Afirika kuma ya riga ya zama bata mahawara mai inganci wadda aka bayyana shi cikin littafin **Cheick Hamidou Kane (L'aventure ambiguë)**:sake haɗuwa da muƙamin ilimin gargajiya,da ilimin Kur'ani, da makarantar turawa da kuma alƙawalin wannan gaba da za a yi hasashe kuma a gina. Domin mafi yawancin masana, uwayen sun tsorata da wannan makarantar da ba ta cika alƙwarinta yawancin lokaci, amma a lokaci guda kamar wata hanya ce da ba za a kauce mata ba.

Dagane da fahimtar zamantakewar, malamai sun fitar da abubuwan da aka lura da su:

-yawanci malamai suna magana da kaucewar uwayen yara ko rishin ƙoƙari wajen bada gudummuwa(Ba su amsa kira ko su zo taron makarantar);

- malamai suna jiran kama - jiki daga uwayen wanda ya dace cikakken halin neman ilimi mai nuna shawarar uwayen don cin nasararilimi: uwayen yara;

-dole uwaye su kasance a cikin hanyar taimakawa, masu maye gurbin aiki cikin aji ba tare da yin gasa tare da su a kan matsayi na aiki ba yayin da suke bada shawar koyo ga yayansu;

-malamai sukan soki uwaye kan rashin tantance aikin sosai, sabodasauke wannan aikin kulawa akan karatun aikin gida.

#### 4. Matsayin uwaye a tsarin ilmantarwa na yara

Anabayyana gaskiyar iyalai a cikin maganganu irin su: faɗaɗɗayan uwanci, tashin hankalin rabuwar aure, rashin iyakoki na uwaye, yawan kariya ta uwaye mata, «yaran da aka bari su kula da kansu». Waɗansu halayen sukan haifar wa iyaye da iyalai fitattun ko mayar da su baƙi **(Thin, da Asdih ya yi Zancen shi, 2012; Turney da Kao, 2009).**

A Afirika,rassan iyalai suna da rikitarwakuma suna daƙarfi ƙwarai. **Aldegheri (2010)**yana nunaiyali yana fuskantar sauye-sauye dayawa a game da ci-gaban yanayin zamantakewar tattalin arziki da halin da yake da tasiri mai zurfi akan dangantakar aureta hanyar juya matsayin uwaye masu kulu da aikin.

A cikin halin Afirika ta yamma, ire-iren iyalai suna daidai da ƙa'idar dankantaka mai faɗi kuma laƙanin dangantaka ba ma'aifan yaro ba kaɗai ya shafa (Cisse,fall, Adjamagbo da Attame, 2017).

Abun dayake ƙarfafabayyanawar waɗansu siffofin iyalai kamar zama da mace ɗaya, zama da mata dayawa cikin gidaje dabam-dabam, rabuwar aure, haife –haife ba cikin aure ba, bada amana (Marcoux da

Antoine,2014). Cikin irin wannan halin, wani lokaci makamancin yana da wuya cikin jarabawar dangantaka masamman ma a cikinfannin ilimintar da yara.

A game da hulɗa tsakanin makaranta da uwayen yara, mafi kyawan yanayi an iyakance su ne kawai ga cikakkun bayyanai daga makaranta zuwa ga uwaye. Malamai da shugabanin makarantu suna ɗauka cewa wannan bayanin ya dace da tsammanin uwaye kuma uwaye suna ɗauka cewa wannan bayanin shi ne kawai bayanin da za a iya ba su. Wannan hanyarwatsa labaru mai yiwuwa ne ta sanya uwayen yara su ɗauki alhakin muhallin ilimintar da ɗan makaranta (tallafin makaranta, salon rayuwa, dasauransu.) kuma yana ba su ikon gudanar da aikin aji ko tsarin darussan. Har wa yau, uwayen yara ba su san cewa suna da yancin kula da ababan da aka koyawa yaransu ba da kuma tsarin ilmantarwa da aka sanya gaba. Dayawa daga cikinsu, hatta ma hamshaƙan masu cikakken ilimi suna zaton cewa jaddawalai da ayyukan koyarwa su ne naƙwarewar makarantu. Ta bakin wani shugaban ƙungiyar uwayen yara da ɗalibai (APE/E) na Nijar, «A matsayin muƙaminmu na uwayen yara shi ne na rakiyar Gwamnati ta hanyar tabattar da bi sau-da-ƙafa yaranmu kai a kai. Muna kiranuwayen yara da su bi sau-da –ƙafa yaransu bayan wata ɗaya ko biyu da fara karatun yan makaranta da neman labaru ga shugabannin makarantar» (tattaunawar da aka zana cikin jaridar "Air Info na 26 ga watan satumba 2018.

Dangantaka tsakanin iyali da makaranta tana da wuya kuma tana bambanta dangance da sashe kamar matakin ilimin uwayen yara, wurin zama (karkara/birni). A Nijar iyalai suna tsammanin komai daga makaranta ga yaransu. Ana tantance wata ɗabi'ar uwaye ta barin tabiyar yaransu.« Kullum muna tsammanin malamin makaranta ya aikata komi a madadinmu. Zai aikata abun da ya iya kawai. Ya rage ga mu uwayen yara mu aikata sauran musamman a gida! »(faɗar wani uban ɗan makaranta). Wannan rishen amincewar ba ya nufin yin watsi,barin gaba ɗaya da tarbiyar yara saboda a mafi yawan lokuta, uwayen yara suna zama kambacin malaman ilimintar da ɗa'a da zamantakewar yaransu.

Dangance da makaranta, mafi yawan lokuta uwayekawai suna masu tattara kayan aikidon ɗaukar nauyin buƙatun yaransu.

Waɗansu uwaye suna cewa tsarinda kanshi nematsayin raguwar ingacin koyarwa/koyo. Ta bakin wani uban yaro «tsarinmu na ilimantarwa ya faɗi gajar a ƙasa. A yau ana buƙatar fanni mai kyau na koyarwa da koyo don ana tsamanin samun sauyi mai armashi a cikintsarin. »

A gefe guda kuma, waɗansu uwayen suna zargin yaransudonmatsalolin karatunsu.Ta ra'ayin wani uban yara da wata jarida ta wurin ta yi hira da shi « ba su da ƙoƙari ɗaukan lokaci su koyi darusa a gida a yayinda Gwamnati a nasa gefe yake ƙoƙarin ganin yaran nan sun samu nasara».Don hakarawar da uwayen yaran suke takawa na taimakawa,a cewar su ta taƙaita ne ga tabbatar da cewa yara suna zuwa makaranta akai-akai. Wannan ya fito ne ta bakin wani uban yara da ya ce « dangance da uwayen yara, ya kamaya su tsaya daidai saboda yaransu su tafi karatu».

**5. Gagaggundubarun tabiyya uwayen yara na Nijar**

Wani bincike da aka gudanar a Nijar ya nuna cewa, yayin da mafi yawan yan makarantar da aka yi nazari a kansu suna cin ribar ƙwaringwiwa ta baki kawai daga wajen uwayensu (Daouda, Abdourahamane & Chékaraou, 2015).

Wani binciken kuma na Nijar ya mayar da hankali kan ayyukan gyara amakarantun paramari. A cikin wannan bincikenan bayyana matsayin uwaye saboda su ne suke ɗaukan yaunin gyarankuma yawancin uwayen da aka bincika sun yi imanin cewa gyaran yana hadasa rishin daidaito tsakanin yara (Abdourahamane, 2015 shafi na 213). Da yake yaran ba su da hakkin iyalai iri ɗaya, ba za su iya samun damar yin ayyukan gyara cikin adalci ba. Uwayen da aka yi binciken kansu sunbayyana a fili da yaran da aka rubuta don gyaransuna samun wasu gatanci idan aka danganta su da sauran.

**6.Kaƙa za a sanya uwayen yara cikin harkokin makaranta?**

**6.1 Sanin halayen uwayen yara dangance da ilmantar da yara.**

Hakalin uwaye ya rabu a tsakanin ilimin cikin iyali a gida da darajanta al'adun makaranta. Kullum ba su da hazaƙar da zu taimakawa makarantaryaransu,wataƙila, ko domin ba su san yadda za su yi ba, ko kuma ba su da halin yin shi ne (Fotinos, 2014a).

Ana iya lura da fanni kashi-kashi na halayen uwaye dangance da makaranta:

-yan ba ruwa na da suke nufin karatunyaransu ya rataya kaɗai kan makaranta ;

- iyalai masu aniyar kirki amma ba su da iko, suna maimaita wa yayansu gargaɗin malamai kullum da kuma wanda duniyar makaranta ta kasance a waje ;

- iyalan da ba su san yadda za su yi kuma suka ce rishin jagorori ko matakai masu amfani don fasara gargaɗin malamai zuwa gaskiya ;

- uwaye « sanannun cikin ilimi», galibi daga babban matakin zamantakewa da al'adun, waɗanda duka biyun za su iya daidaita gargaɗin a aikace amma waɗanda suke warware gargaɗin daga malamai.

Rishincancantar da uwayen yara suke ji yana da sakamakon cewa «haɗin gwiwar uwaye zaiiya faruwa ne kawai idanakwai gayyatar shiga daga malamai, kuma da fahimtaraikin uwayen» (Feyfan da Rey, 2006). Uwaye suna buƙatar fahimtar dangantakar yaransuda makaranta da aikin makaranta. Magana ce ta faɗa da munanan fifikon uwaye ga makaranta, tare bayyana musu abubuwan da suke faruwa a makaranta ta hanyar ba su labarin.

**6.2 Zabarnau'in shigar uwayen yara a cikin makaranta**

Shawar haɗin gwiwatare da uwayen yara sau da yawa yana nuna cewa sun dace da ƙa'idodi, da tsare-tsare, da matsayin da makarantar ta tilasa masu. Duk wata kasawar uwayen yara don su daidaita yana ƙarfafajin rishin adalci da buƙatar ja da baya (Périer, 2012). Sanya hannun uwayen yara yana iya ɗaukar nau'ika iri-iri. A cikin wannan mahangar ne rubutun da Epstein ya gabatar (2010) yana nuni ne da shigarda makaranta a kan yanayin zamantakewa da tattalin arzikina uwayen yara. Wannan jan hakalin yana iya ɗaukar sigar:

-bin yara sau-da ƙafa a gida;

- kula da tsarin iyali na buriga ilimi da darajar jama'a;

- haɗuwa da malamai saboda fahimtardokikin makaranta da ƙoƙarin yara ;

- shiga cikin ayyukan makaranta;

- taimako iri-iri, na yau da kullum ko na lokaci-lokaci a makaranta;

- bada hannu na gyare-gyare da kuma gudanar datsarin tafiyar makaranta.

**6.3Yin aiki tare dauwayen**

A yau, sa hannu na uwayen yara yana zama dole a cikin bayanan malamai a matsayin hanya mai mahimmanci ta sababbin abubuwa. Saboda, makaranta da iyali sun kasance masu haɗin kai kuma dole ne su shiga cikin waninau'ina yin aiki tare da yake da shawar ƙwarewar gama kai. Tun da an san makaranta a matsayin guri na masamman na ilimantar da yara; duk abubuwan zamantakewa suna dacewa da cin nasarar ilimi ta zama babbarmatsala ga yaransu (Durning, 2006). Don haka, buƙatar haɗin kai tsakanin uwayen yara da malamai ba sai an nuna ba. Tambaya ce ta samar da tabbataccen yanayi don gane ta. Yawancin bincike bisa dangantakar uwayen yara da makaranta sun nuna cewa yana tasiri ga cin nasarar ilimi(feyfant, 2011). Kenan,uwayen yara sunada mahimmancia cikin ayyukan makaranta.

Ya kamata makaranta ta nemo cikakken goyan bayan uwayen yara. Lallai haɗin kai da haɗa gwiwa tare da iyalai suna cikin kwarewar da dole ne malamai su zama ƙwarari. A waɗansukalmomi, malamai ba za su iya yin aiki tare da yara kaɗai ba a cikin aji, amma har ma bayan iyalai don su fitar da wani salo tsakanin makaranta da gida. Akwai buƙatar zama wata hanya madaidaiciya tadubarun na haɗin kai.Ka'idar haɗin kai tana nuna matsayi da ɗabi'a wanda ya ƙumshi amincewa da uwayen yara a matsayin masu ilimantar da yara na fari: tabiyyar ba tare da koyarwa ba amma ba tarbiyyar iyali ba ne, yana ginawa tare da su (Asdih, 2017; Rayna da Rubio, 2010; Humbeeck et Al.,2006). Tarbiyantar da juna tana nufin «bada kayan aiki , aikata, tattara uwayen yara ta yadda za su kasancewabatutuwan masu iya ɗaukan nauyi makarantu (Giuliani & Payet, 2014).

Duk- da- haka, ya kamata a lura cewa ba za a iya kafa wannan dangantakar ba tare da cikas ba. Waɗannan na ƙarshen suna iya yin tasiri, mai kyau ko maras kyau mahimmancin wannan dagantakar, danganta da ra'ayi da tsammanin game da matsayin kowa.Don haka, malami da uwayeda suke da kamannin wannan fahimtar juna sun fi dacewa su kasance a bisa tsayi iri ɗaya kuma su ƙulla dangantaka mai jituwa fiye da na baya. A ɗaya ɓangaren kuma, tsoron hukuncin wanicikas ne mai girma. Uwayen yara dayawasuna jin tsoro, allal misali, kada a fahimciko a yi masu la'akari da rashin dacewadaga ma'aikatan makarantar (Ouedarago, 2016) kuma haka lamarin yake ga malamai a wajen uwayen yara, masamman a yanayin shigar uwayen yara a cikin aji.

Wajen tattaunawa tare da uwayen yara saboda a kafa kuma a riƙe dangantaka jituwa, yunƙurin ɗaya ne don a samu wannan ci-gaban (Uyedarago, 2016.) Ya kamata,daga cikin wasu abubuwa, a hanna matsaloli ta hanyar barin halaye su gurɓace ko su ɓace samsam. Don haka, zama mai tarba da gayyata uwayen yara zuwa cikin aji ko makaranta da wani dalili cikakke (annashuwa, abincin dare na karkara, baje-koli, ɗasauransu.) hanyoyi nena kyautata dangantaka harma da kasancewar uwayen yara a makaranta (Hoover-Dempsey & Sandler, 1997). Bugu da ƙari, yana da kyau a sanya makarantar ta samu sauƙin zuwa ga uwayen yara, masamman ta hanyar yin mu'amala da malamai ko shugaba mai kulawa damakarantar, wannan shi za ya ba uwayen yara ƙarfin gwiwa su shiga cikin ayyukan makaranta. Ya kamata

a ƙirkira ɗabi'a mai goyon bayan zamantakewa (a kasance mai tarbo) don a ƙarfafa sa hannun uwaye.

**6.4 Halin ayyuka na shigar da uwayen yara cikintsarin tafiyar da halayen makaranta.**

Ya kasance wani matashin ɗan makaranta kuma mai hazaƙa, Hasan Bubakar (aji na biyar) wanda yake da hazaƙoƙin da za su sa shi ya ci galabar karatunsa. Ya kasance mai himma mai kula da tafiya makaranta kullum a kan lokaci kuma yana mayar da hankalinsa kan aikinsa. Lokacin mizantawa, kullum yana samun manyan sakamako. Amma, tun a wani lokaci, al'amarin Hasan ya dagule. Yana nuna wani sabon hali a makaranta: mafi yawa, idan ba ya na, ya yi lati. Har ila yau, lokacin da muke koyarwa, ya fi shagala fiye da maida hankali. Kwata-kwata ba shi da shawar karatunsa. Makinsa kaɗan-kaɗan yana raguwa sosai.

Amma, ta ƙaƙa za a ciwo kan wannan matsalar? Wane tsarin tafiyar da aiki za a a gudanar wa? Waɗanne shugabannin na masamman za a taɓowada gaggawa? Kuma wanɗanne sauran shugabannin harila yau?

Bayan an gano taɓarɓarewar halin matashin Hasan Bubakar, malaminsa ya shaida wa shugaban makarantar dalla-dalla wanda yatuntuɓi iyalin yana gayyatar uban makaranta.

-**Bubakar (**uban yaron**):**«Assalam - alaikum, malam shugaban makaranta!

- **Shugaban makarantar**: (Bayan ya tashi kaɗan) Wa'alaikum -assalam! To, malam Bubakar ne! (ya nuna masa wata kujera).Ku zauna … Ku zauna …

Bayan wasu gashe-gaishen ban girma, sai shugaban makarantar ya gaya masa dalilin wannan gayyatar.

-**Shugaban makaranta**: "game dayaronku ne Hasan. Ya sauya gaba ɗaya sosai har ma malaminsa haka ma ya koka da shi. Tare da malaminsa na tambaye shi saboda in gane inda matsalar take amma ina! Wataƙila ku, za ku iya taimakamana mu warware lamarin.

**Bubaka**r (babanyaron): na gode malam shugaban makaranta. Na yi mamakin jin wannan labarin. Da gaske, akwai wani dalili!Ko ni ma na damu sosai da karatunsa, ganin haka ɗin, ba za ni iya yarda ba da irin wannan halin. Amma, ina roƙonka ka bar mu, mu ɗan tattauna da marecen wannan. »

Da marece, jim kaɗan, bayan sallah, sai uban ya yi kiran Hasan don ya tambaye shi gaban uwarsa.

**-Uba**: « Mene ne ya rage maka a makaranta? Littattafai? Kayayyakin aiki ko kuɗin cin abinci lokacin shan iska? Kana da wata matsala tare da malaminka?

**-Ɗan**: A'a, ba ni da kowace matsala a makaranta.

-**Uba**: I, an kira ni makaranta saboda kai. Har ma an gwada mani daftarinka na kacici-kacici da rajistan rashin zuwa makaranta na yau da kullum. Babu komai ciki sai munanan sakamako da rashin zuwa makaranta so da yawa. Malaminka ya gabatar da halayenka. Mene ne ya faru, Hasan? Mene ne ya same ka?

**-**(Hasan ya yi shiru da ɗan lokaci kuma ya kwatanta ya fanshi kansa da fujja). Baba aji na shidda yana da yar wahala.

**-Uba**: Ba a nan matsalar take ba. Ko da haka nan ne ma, don me kake yin lati, rashinzuwa makarantar tare da shaƙiyanci a cikin aji? Ba ka da waɗannan halayen a da. Ka iya karatu; kana

da hankali kuma kana da duka kayayyakin aikin da za ka yi karatu da kyau. Kana da halayen da za ka samu nasarar karatunka a makaranta. Me ya sanya kake son jefa ruyuwarka cikin hatsari? Har ka manta da ka ɗauki arwashin yin karatu ƙwarai saboda ka zama minista watarana?
Tunda Hasan ba shi da alamar bada datattun anshoshi, babansa ya ƙara ja masa kunnuwa kuma ya hane shi hutar da ba ta da amfani. Ya yi amfani da wannan dammar ya yi masa gargaɗi da kyau kuma ya ce masa da kar da ya koma yin fashi da sake zuwa makaranta da latti. Kuma ya ba shi umurnin zuwa yin tilawar darussansa kuma da yin haka ɗin kowace rana. Ya ba uwar yaron umurni da ta dube shi in ba ya nan.
Washe gari, Bubakar ya koma wajen shugaban makaranta don yi masa bayani. Tabbas, Hasan ya ɗauki alƙawarin sauya halinsa, amma uban ya ga cewayana da amfani don tura binciken don gane abubuwan da suke tabbatar da waɗannan sabin halayen yaron. Daga bincike zuwa bincike na tsawon kwanaki, Bubakar ya gano cewa ashe wani tsofon ɗan makaranta ne da ya dawo daga yawon ta-buraɗaya hana wa yara karatu dangance da galabar da ya samu a ƙasar waje. Sai tsofon ya faɗa wa shugaban makarantar da Maigari. Ta haka ne Bubakar ya buƙaci shugaban makarantar ya tattara shugaban ƙungiyar uwaye (APE), uwaye mata (AME), da komiti mai kula da tafiyar da harkokin makaranta (COGES) a gidan Maigari saboda a ƙalubalanci tare da bayar da gargaɗi ga wannan ɗan ta-baraɗan. Shi ɗin ya so yin gardama amma ban tsoronda Maigari da shugaban makaranta suka yi masa ya sanya shi faɗar gaskiya sannan ya nemi gafara.
Daga ƙarshe, bayan taron, Bubakar ya yi ta zana ayyukan da ba a ci nasara ba da kuma waɗansu yan ta-buraɗar da suka mutu, ya bayyana wa ɗansa mugayen labarun yan ta-buraɗa. Yana aminta maganarsa ta hanyar bada wasu misallai na gaskiya, amfanin makaranta. Tun daga wannan lokacin, matashin Hasan ya kama jikinsa kuma ya dawo bisa kan hali na gari.
Daga wannan ƙwarewar ta Hasan, ana iya ganin an ciyo kan matsalar da farko, saboda kulawar malaminsa da ya yi magana da shugaban makaranta a kan lamarin. Sa'anan kuma dole ne mu jinjina wa shugaban makarantar da hali mai kyau (wayayye, mai tarbo da kyau, milmishi,) da yake jawo hankalin baban yaron cikin sani da gwaninta. Daga ƙarshe dai, tsinkayar da yake yi wa makaranta da kuma nuna damuwarsa da ɗansa ya samu nasara Bubakar, uban yaron ya mayar da niyar kuma ya sanya sauran shikashikan neman hanyoyin da za a ciyo kan wannan annoba da ta dungo kai wanda ya kusan taɓarɓare karatun Hasan da kuma wanda zaiiya jawo sauran yaran gari dayawa.

**Kammalawa**

A Nijar kamar sauran ƙungiyoyi dayawa na Afirika, an ɗauki makarantar boko tamkar maƙirƙira yan zaman kashe – wando kuma waɗanda al'adarsu ta tumbuƙe. Wannan hoton da ake jawo cece-kuce yana haifar ta canza ra'ayoyin uwayen yara su ƙara sanya hannuwansu dangance ilimin yaransu. Tare da wannan al'amarin akwai tsarin bambancin bada ilimiwanda aka jima ana yin shi a cikin tsarin makarantu.Ta hanyar rakiya, sai mu ce gargajiya da alama ba ta da kwaɗaitar da uwaye wajen kulawa kai-tsaye da tarbiyar yaransu. Babban ra'ayin shi ne cewa dole uwaye su samar da halayen da yara za su iya koyan ɗauka darasi a gida saɓanin yadda ake yi a Turai inda uwaye ma suke taimaka wa yaransuda aikin gida.Ingataccen matsayin

uwaye wajen koyo na yaransu a duk duniya. Duk da haka, wannan matsayinyar yanzu yana nan daram kuma yana wanzuwa ta hanya dabam-dabam a cikin ayyukan shika-shikan da abun ya shafa.Haƙika, idan a cikin jawabai a koyaushe a na kiyaye cewa uwaye suna da alhakin taimakawa yaransu a makaranta, wannan ba ya bayyana a cikin ƙa'idodi.

**Références bibliographiques**


**Abdourahamane M.M. (2015). «** Remédiation formelle à l'Ecole Mission garçons de Niamey au Niger : renforcement de capacités ou d'inégalités sociales des élèves ? », *Nazari*, revue africaine de philosophie et de sciences sociales, Numéro 001, novembre.

**Aldegheri, M. (2010**). *Représentation sociale de la parentalité chez les travailleurs sociaux chargés de la protection de l'enfance : impact sur les mesures de prévention*. Mémoire de recherche. Deis, Toulouse.

**Asdih, C. (2012).** « Collaborer avec les parents pour accompagner la scolarité ? Représentations des enseignants et pratiques professionnelles ». *Enfances, familles, générations*, n° 16, p. 34-52

**Asdih, C. (2017).** Coéducation, compétences parentales et professionnelles. *Administration & Éducation,* 153, 31-36.

**Barreteau, D., et Tiné, Y. (1999).** « Les écoles de Téra au Niger : Choix des parents et politique scolaire ». *Les Cahiers c1I~e.,* N°1, 86-99.

**Cissé, R., Fall, A., Adjamagbo, A., et Attané, A. (2017).***La parentalité en Afrique de l'Ouest et du Centre. Vidal Laurent (coord.). Renforcement de la recherche en sciences sociales en appui des priorités régionales du bureau Régional Afrique de l'Ouest et du centre de l'Unicef: analyses thématiques, Dakar (SEN).* Dakar: IRD Unicef, 2017, pp. 37-59. hal-01791432.

**Daouda, A. (1991).***Education et Développement au Niger : Pour une contribution à l'amélioration des rendements scolaires et à la réinsertion des jeunes déscolarisés au processus du développement rural a Maradi*. Thèse de doctorat en sociologie de l'éducation, Université nationale de Côte d'Ivoire.

**Daouda A., Abdourahamane, M.M. et Chékaraou, N. (2015).** « Stratégies parentales et orientations scolaires au Niger: analyse sociologique des déterminants du choix de la formation en Agent de Santé de Base à l'Ecole Nationale de Santé Publique (ENSP) de Niamey au Niger », in *Annales de l'Université Abdou Moumouni*, Tome XIV-B, pp. 12-23, 2ème semestre.

**Durning, P. (2006).***Éducation familiale. Acteurs, processus, enjeux.*Paris: L'Harmattan.

**Epstein, J.(2010).** « School/Family/Community Partnerships: Caring for the Children We Share ». *Phi Delta Kappan, vol. 92*(n° 3), 81–96.

**Feyfant, A. (2011).** « Les effets de l'éducation familiale sur la réussite scolaire ». *Dossier d'actualité Veille & Analyses IFÉ, n° 63*, juin. Lyon : ENS de Lyon.

**Feyfant, A. et Rey, O. (2006).** « Les parents et l'école ». *Lettre d'information de la VST*, n° 22, Lyon : Institut national de recherche pédagogique.

**Fotinos, G. (2014).***Face à face entre confiance et méfiance : lycée-collège et parents d'élève : une enquête quantitative auprès des directeurs d'école maternelle et élémentaire*. Noisiel : Casden.

**Giuliani, F., et Payet, J-P. (2014).** « Introduction. Les logiques scolaires de la proximité aux familles ». *Éducation et sociétés, n° 34*, p. 5-21.

**Hoover-Dempsey, K., V. & Sandler, H.,M. (1997).** Why do parents become involved in their children's education? *Review of Educational Research, 67*, (1), 3-42.

**Humbeeck, B., Lahaye, W., Balsamo, A. & Pourtois, J., P. (2006).**Les relations école-famille, de la confrontation à la coéducation. *Revue des sciences de l'éducation, 32*(3), 649-664.

**Lorcerie, F. et Carvalo, D. (2002).** Les relations entre familles populaires et école. *Les cahiers millénaires 3, Communauté urbaine. Direction de la prospective et du dialogue public.* Lyon : Éducation et mode de vie, 3 (24), pp.5-24. hal-01526634

**Marcoux, R. & Antoine, P. (2014).***Le Mariage En Afrique : Pluralité Des Formes Et Des modèles Matrimoniaux. 1st ed, vol. 1*. Québec : Presses De l'Université Du Québec.

**Maubant, P. & Leclec, C. (2008).** « Le partenariat famille-école : à la recherche de l'improbable partenariat famille-école, origines d'un malentendu ». *In Pithon Gérard, Asdih Carole & Larrivée Serge (dir.). Construire une communauté éducative, un partenariat famille-école-association*. Bruxelles : De Boeck, 24-36.

**Meunier, J. A. (2008).** Un nouveau genre et une nouvelle espèce de Cerrambycidae Plectogasterini du Cameroun (Coleoptera). *Bulletin de la société entomologique de France.*

**Moumouni, A. (1968).***Education en Afrique*. Paris : Maspero.

**Ouédraogo, F. (2016).***Étude des liens corrélationnels entre la collaboration école-famille, l'implication parentale, les styles éducatifs des parents et la réussite scolaire des élèves du primaire au Burkina Faso.* Thèse de doctorat en Psychopédagogie et andragogie, Université de Montréal : Montréal.

**Périer, P. (2005).** *Ecole et familles populaires : sociologie d'un différend/ postface de Jean-Manuel Queiroz.* Rennes : Presses universitaires de Rennes « Le sens social », 221 p.

**Périer, P. (2012).** « De quelques principes de justice dans les rapports entre les parents et l'école ». *Éducation et didactique, vol. 6*(n° 1), 85-95.

**Périer, P. (2012).** Familles des classes populaires : décrochage parental. *L'école des parents*, vol. 6(599), pp. 26-28.

**Rayna, S. & Rubio, M., N. (2010).** Coéduquer, participer, faire alliance. *In S. Rayna, M.-N. Rubio & H. Scheu (éds), Parents-professionnels: la coéducation en questions.* Toulouse : Érès, 15-25.

**Sawadogo, I., Dugué, P., Rodriguez, L. et Ouaba, B. (1994).***Techniques d'amélioration de la production agricole en zone soudano-sahélienne : manuel à l'usage des techniciens du développementrural, élaboré au Yatenga, Burkina Faso.* Montpellier : CIRAD6SAR, 209 p.

**Thin, D. (1999).** Quartiers populaires – L'école et les familles. *Revue française de pédagogie*, 128, pp. 160-163.

**Turney, K. & Kao, G.(2009).** « Barriers to school involvement: Are immigrant parents disadvantaged? ». *The Journal of Educational Research, vol. 102(n° 4),* 257-271.
**Verba, D. (2006).***Échec scolaire : Travailler avec les familles*. Paris : Dunod.

.

**Babi na 4**

# Tabi'un tarbiyar gargajiya na Afirika a matsayin sanin share-fagen koyo a makarantun boko

**Goza Nana Aicha**

**Taiƙaicewa**

Yaro ɗan Nijar na karkara yana samu tarbiyar gida kafin ya shiga fagen makarantar boko. Duk da yake wasu al'adu da tabi'u suna ɓacewa, akwai har kullum tabi'u na horo ko tarbiya da suke nan. Wannan nazari mai bada bayani, bayan an zagaya tabi'u na tarbiyar gargajiya da na zamani, za ta tattance alaƙa da ake akwai tsakanin sani na share-fagen makaranta da aka samu daga tarbiya ta gida da ilimi na makarantar boko. Nazarin takardar tafiyar da darasi na ɗa'a a babbar tsangayar share-fagen karatu cewa da « jardan » da faransancibisan ladabi ya ba mu damar tattance cikin dubaru na gida, gatana/tatsuniya a matsayin madogaran koyarwar da suka dace da darasin ɗa'ar.Lalle, gurirrikan da ake son cimma daga wannan darasi sun yi daidai da ƙwarewar da ake son girka ta hanyar gatana a galibi : saurare, lura, ban dariya/nishaɗi, hankali da ƙarfin tunani, kuma da ƙarfafa bunƙasar ɗan Adam ds. Aikin malamin shi ne ƙarfafawar sani na baya da aka laƙanta ta hanyar gatana, bayani na nishaɗi da darasi da gatana take ƙunshe da su misali, duk da ya halaye nagari suna cikin tabi'u na farko da aka koyarwa a gida.

**Mahimman kalmomi :** tabi'u na tarbiya, sani na share-fagen makarantar boko, koyo na zamani, Nijar

**Gabatarwa :**

Tarbiyar gargajiya a Afirika ta ƙunshi halaye na zama cikin al'umma. An tsara tarbiyar don a kawo amsa ga yanayi na al'umomi, siyasar zamantakewa da tattalin arziki. Moumouni (1998, 24) na cewa : ko ta yi aiki da dukan alamomi na mutunci yaro da matashi ko gurin bunƙasa lafiyar jiki, hali, laƙantar tabi'u na ɗa'a, samar da ilimin fusa'a na zahiri ko sani ta hanyar aikin hannu ko da ilimi. Tana shafar kowane fanni kuma tare gaba ɗaya.».Ana yin koyo na laƙantar halayen rayuwa a wajen yaro ta hanyar wasanni daga gatana, almara, kacici-kacici, karin magana, guje-guje, wasannin motsa jiki da raye-raye. Ba fusa'ar koyarwa ba ce dabam da wasa.. Tana cike da arzikin al'adu da sani da yaro za ya goga da su a makarantar boko ta hanyar wani tsari na koyarwa da ya sha bamban.

Manufar wannan bincike shi ne na bada bayani kan tabi'un tarbiya na gargajiya. A taƙaice, binciken zai gwaɗi yadda makarantar boko za ta iya amfani da sanin da yaro ya samu a tarbiyar gida wajen gina wasu halaye, a ba koyarwa manufarta kuma a ƙayatar da tsarin koyarwa.

## I. Ire-iren ra'ayoyi na iyali da tabi'u na tarbiya

Cikin wannan ɓangare, za a yi nazarin ra'ayoyi dabam-dabam na garjiya da na zamani na makaranta. Ra'ayoyin biyu da suka bambanta amma da ya kamata a ce suna halaƙa ta cuɗayya kuma su tabbatar da ɗorewa da ci-gaba mai inganci na yaro.

### 1.1.Ra'ayin gargajiya ta iyali da tabi'u na tarbiya

Kafofin watsa labarai, fitilu da suke haske manya birane suna son su ɓoye wata gaskiya ta zahiri da bujera wa yunƙurin zamani cewa da ra'ayoyi na gargajiya na iyali a Nijar. Yaro ɗan Nijar ɗan makaranata, ko wandan ya bar makaranta ko wandan bai je ba ma, yana fuskanta kodayaushe wannan matsalar ta bambanci tsakanin zamani da gargajiya.

### 1.1.1 Shiga cikin da'irar iyali

Mafi yawa al'ummar Nijar tana rayuwa a karkara kuma ta ƙumshi sama da 84% na al'umomin ƙasar UNICEF (2018).Duk da yake tana gwada alamu na zamani, al'ummar Nijar ba ta yadda al'adunta ba kuma ta ƙoƙari kare su daga barazanar tabi'u na zamani da su zo muna daga ƙasashen waje.Iyali ginshiƙin tsarin al'umma ya riƙe al'adarshi ta haɗuwa wuri ɗaya musamman a karkara. Galibi zuri'a tana rayuwa mazamni ɗaya da ake ce wa « gida ». Daƙuna dayawa, ƙananan gidaje suna kewaye da ɗakin uban iyali. Waɗannan iyalan suna noma gona ɗaya ta gado. Wani lokaci waɗanda aka yi wa aure suna iya cin moriyar ɗan fili da aka yanka musu a cikin gonar, amma cikakken yanci da girma yana ga uban iyalin babba.Cikin wannan tsari, yaro yana da wuri na musamman. Wasu marubuta kamar su Moumouni A (1964) Salifou A(1977) sun bada bayani kan babban matsayi da aka yi wa yaro cikin da'irar iyali da kuma cikin al'umma. Al'umma ce gaba ɗaya ta take ɗaukan ɗayauniyar aifuwa. Ana iya yin komi don a samu yara.Mata suna iya ɓata dukiyarsu don su samu magaji. Su ko maza suna yin aure da yawa don sumu wanda zai gaje su bayan rayuwarsu. Samun yaro yana kewaye da mamaki da wasu canhe-canhe. Yana zuwa da wasu al'adu na gargajiya tunda ga aifuwa har zuwa yaye kai har tsawon rayuwa. Sirrin shi ne kare shi da mugun ido, mugun baki da kuma iskoki da dukan wani baki da ake iya masa. Mace mai juna biyu tana yin amfani dukan wasu dubaru na ɓoye kamaninta, hali da saɓawa ziyarar likita don awo kamar yaddama'aikatar kiwo lafiya ta tsaida. Zauwar yaro a duniya tana tare jin daɗi iri-iri. Tun daga nan za a tarbi yaro cikin babban iyali kuma a nan ne za a ba shi tarbiya. Babbar yaya, ɗiyar maƙwabta da ba ta wuce shekaru 3 ko 4 (za su kula da tsaronshi, ko su riƙe idan yana koyon zama) kakanni, ƙannen uwaye ko wasu manya da zu kula da jikinsa da abincinsa, wasa na tawai. Kowane da cikin waɗannan mutane yana da nashi kirari da yake taɗa yaro.

Can kuma uwar da ba ta san komi a kan yaro za ta dogara wannan gudummawar don samar yaron nata ƙauna da kulawa da za ya tamaika wajen bunƙasarsa. Yaro yana rayuwa tare da ma'aifiyar, ko ya kasance yana tsotsar nono ko a goye a bayanta ko a rungume da ita.A fannin halayar ɗan adam, wannan kulawar daga al'ummagaba ɗaya tana da mahimmacin cewar Rive (1969) kamar yadda Sandi ya kawo a cikin bayaninsa (1993 p.36), tasiri ko rinjaye na musamman na saƙwarta farko da take tsakanin jariri da kewayensa, a wasu kalamai alaƙa ta farko da take a bayyane kuma mai ƙarfi suna dogara da sharuɗɗa, tsayayyu kuma sahihu daga bunƙasar halaye ».

### 1.1.2. Shiga cikin sahun manya L'intégration dans le monde des adultes :

Iyalin karkara a Nijar na da manufar samar ɗan ƙasa da za ya samu shiga ko karɓuwa cikin a al'umma da kuma a fannin tattalin arziki. Fusa'ar da aka fi amfani da ita ce kwaikwayo. Samar da wani hali, ta hanyar maimaitawa, da jaddawa, yaro yana ganewa kuma ya riƙe halaye na ɗa'a, na jiki ko na ilimi da kuma al'adu na al'ummarsa.Ta hanyar koyo a duk tsayon rayuwa za

a ƙarfafa ƙwarewa da yaro yake buƙata don bunƙasar kansa da kansa. Ana yaba masa halaye nagari, halaye na banza ko za ya amsa laifinsu.

Kuma umurni da tarbiya suna tafiya tare, ƙa'ida da zahiri su ma suna haɗe, don haka ne Moumouni (1964) yake cewa « ingancin wannan tarbiya ya dogara da alaƙarsa da rayuwa, lalle, daga wasu halaye a cikin al'umma da kuma hulɗoɗi (rayuwar iyali, sabgogi na jama'a) ake samar da tarbiya yara da matasa. » Tun daga nan ra'ayin matsayin yarinya da yaro cikin rayuwa za ta fara taka rawa cikin manufar tarbiyarsu.

**1.1.3. Yarinya cikin muhalinta**

Mahimmin guri na tarbiyar yarinya shi ta samu horo na samun matsayi na mace a cikin al'umma wato matsayi na uwa da mata. Amma cikin da'ira mata za ta girma. Wannan tarbiya fa shafi addini da farko, za ta tauye ƙa'idoji dayawa (hakkoki) bada damar bunƙasar ya mace. Tarbiyar za ta karkata wajen abubuwa da suka rataya kan mace a ƙasa miji da matsayinta na uwa. Tun daga nan da'irar mata da ta ƙunshi uwaye za su maida hankali wajen tabbatar da wannan tarbiya. Tun da wuri, wato cikin ƙuruciya, gani tsarin koyon ta hanyar kwaikwayo, ana koya wa yar yarinya ayukkan gida ; Matsayinta na yar koyo, zai fara sannu-sannu zuwa ga matsayi na musamman. A zahiri, za ta lanƙanci dukkan wasu kyakkyawun halaye na mai girki. Tarbiyar kama-kai da kulawa da wani ɓangare na jikin ɗiya mace ba ta yi ƙarfi ba don ana ganin batun kamar abun kunya ne. Aiki ne da shafi mata da maroƙa da suke iya faɗin maganar ba kunya a kowane hali. Wasu batutuwa ana bayani a kansu a cikin wa'azi. A bayyane ne babu wata hanya ta horo a kan kama-kai ko kulawa da wani ɓangare na jiki. Don haka tsarin tarbiyar kama-kai da kulawa da wani ɓangare na jikin ɗiya mace ba ya samu shiga ba yadda ake so cikin makarantun boko kuma malaman addini suke magana a kai shi ya sa ba su goyi bayan wannan batu ba.Sai dai matsayi mace yana sawaya lokacin za ta kai wasu shekaru inda ake ganin ta « tsufa », wani matsayi na lattijantaka, za a ba ta wata daraja da girma. Wato, yawan shekaru wanimahimmin abu a cikin wasu al'umomi, ana ɗauka mata masu yawan shekaru tamkar tsarkakakkun saboda sun tsaida al'ada/haila. Da yake suna da ƙwarewa ta ruyuwa, suke ba uwaye shawarwari kuma a wani lokaci suna kula da renon jikokinsu. Yarin matashiya, yan mata za ta zauna cikin da'irar mata inda za a lura da hankalinta da bunƙasarta daga kusa kuma ana yi mata aure da wuri.

**1.1.4. Yaro cikin muhallinsa:**

Da farko yana tashi cikin da'irar uwa inda kamar yar yariyar, yake samu tabi'u na farko masu mahimanci da suka haɗa da ladabi, biyayya, girmamawa, zumunci, gaskiya, taimakakkeniya. Duk wannan cikin ra'ayi ta bambace-bambance tsakanin maza da mata. Misali mostin rai yana da manufa, ana kwatanta mishi namiji ba ya kuka, kuma yana kuzari ds. Ba a sa shi wasu ƙananan ayukka na gida kamar yar yarinya.

Tun da wuri ya komawa rukunin maza yan uwanshi, inda zai sani, iyawa, da sani na zamantakewa ɗan adam a rayuwa ta hanyar ayukkan nishaɗi da wasanni. Wajen shakara 6, idan ya yi ƙwari kaɗan zai koma cikin da'irar maza inda za a ba shi tarbiyar ta « namiji ». Za a kowa mishi mazakuta, kuzari, ƙoƙari, gaskiya, jimiri, ta hanyar ayukka na yau da kullum (farauta, su, kiwo, noma da wasanni ds.)

A cikin muhalli ko, yaro yana laƙantar amfani ganye itatuwa, nazarin muhalli. Yana rayuwa tare jama'a inda a wasu yankuna yara suna da wani ɗaki na hutu da bada bayanai tare sa'anni ko tsaraye, Ana yi koyon ya hanyar wasanni (ƙere-ƙere kayan wasa da abubuwan da aka bar amfani da su, kwamɓalar kuje-kuje…)
Ana yi yaron horona samun matsayi na namiji cikin al'umma ta hanya wahalhalu da gargaɗi. Yaron za ya yi haƙuri da jimirin wannan makaranta.

**Ra'ayin iyali daga makarantar boko da tabi'u na tarbiya :**

Duk da yake ra'ayin iyali a gargajiyanceyana nan a karkara da wasu anguwowi na cikin birane, akwai wani ra'ayi na iyali da yake haɓɓaka a cikin birane da yake ɗauke tabi'u na tarbiya na musamman. Haɗuwa da wasu al'umomi musamman ta hanyar makarantar boko sun ƙarfafa wata manufa ta iyali. Keita (1988) a cikin wani bayani da Sandi ya kawo (1993 P. 58) yana cewa : « makaranta boko tana raba yaro da iyalinsa,inda take hana mishi wasu tabi'u nasa da aƙidarsa, al'adunsa da tattalin arzikinsa ta hanyar koya masu wani sani da iyalai ba su da wani iko a kai…Dangance da abun da sanin ya ƙunsa, haƙiƙa, in dai lalle makarantar boko na kawo ƙarin sabon sani, to kenan ta yin shi ta hanyar lalata al 'adu da tsare-tsaren gargajiya »
Duk da jan ƙoƙari da ake yi don gani an daidaita usular koyo da yanayi na zahiri na ƙasa, an yi shakaru da dama ana amfani da kayan aikin koyarwa da suke bayyana aƙidu da suka sha bamban da waɗanda a tanada cikin iyalai Littattafai a misali, « La famille Boda », littafin koya karatu da aka daɗe ana amfani shi cikin makarantu ƙasar Nijar, yana gabatar wani , duk da yake a Afirika ne, da ya haɗa da uba Malam Boda, uwa mata Boda, da yara biyu Rene da Mina da dabbobinsu na gida : kare Miro da mussa Miki. Yara yan Nijar nawa su fuskanci irin wannan rayuwar da ta sha bamban da rayuwarsu ta yau da kullum.Bayan tabi'a ta makarantar boko, birnanci da hanyoyi na sadarwa suna yaɗa halaye da tabi'u , ƙa'idoji da imani da suka bambanta da abubuwan da muka sani cikin rayuwar iyali a Nijar tun uwaye da kakanni . Kullum iyalai masu yawa suna ragewa zuwa ga iyalai ƙanana. Gida yana ragewa yana komawa daga kai sai matarka da yayanka biyu wato cewa da ƙaramin iyali Tarbiyar yara da aka sani can da a hannun kakanni ko dangi, ta koma ga hannun matasa, yan reno da ba su da gogewa. Yan renon kamar yadda sunansu ya bayyana ba sun san komai ba in ba shayar da yaro madara da wasu yan wanke-wanke jiki. Duk wani jin daɗi da walwala da aka san yaro yana ciki, sun gama hanyar ɓacewa.Yaro yana alfari da iyalinsa na kusa kawai saboda wuraren haɗuwa da dandalai sun fara ɓacewa. Tsari na tarbiyar gaba ɗaya wandan duk babban yana da alhakin ɗaukan yaunin tarbiyar kowane yaro ta hanyar gargaɗi, ladabtarwa, a yau babu shi saboda ba ka isa bugi yaro wani, kai-tsaye za ya maida maka cewa « kai ba ubana ne ba ». Babban iyali ya fara ɓace kuma ya zamanto kamar iyali ne nesa da ba yan uwa ba ko dangi. Girmamawa, taimakakkeniya zumunci, ladabi kai dukan wasu tabi'u nagari na cikin ra'ayi na iyali babba da aka sani, sun taɓarɓare kuma an karkata wajen ƙaranin iyali. Makaranta ba hanya ba ce ta koyar tabi'u na gargajiya.
Tun 1960 Ki-Zerbo ya ja hankalin al'umma dangance jadawalin karatu. A tsawon rayuwarsa ya yi ta bayyana rishin tasirin karatun boko masumman matsaloli da rishin daidaito na yanayi na makarantar bokoMasanin yana nuna rishin inganci makarantar dangance nesasawa da tabi'u da al'adu na gida da ta maida gehe. Harshen da ake amfani da shi amakarantar, ba ya ba yaro

damar shiga cikin muhallinsa na zamantakewa da al'adunsa. Shi ko an ce shiga makaranta, sanya ƙafa ne cikin sani, koyo da laƙantar halaye.Don kusantar tabi'u na makarantar boko, cikin wasu iyalai da faranci kawai ake magana, har an kai inda yara sun tashi ba su laƙanci harsunan gida ba. Yaro ya zamanto wato baƙo a cikin ƙasarsa.

**Riƙo, misali na tabu'u na tarbiya**

Wannan tabi'a ta gargajiya ta yaɗu sosai kuma ana ci gaba da ita cikin wani hali cikin iyalai na Nijar kan hujjoji da suka bambata. Dalilan gargajiya da aka gano suna da yawa : doguwar rishinlafiya, rasuwa, rabuwar aure, rabuwar uwaye, taimakakkeniya tsakanin iyalai, tarbiyantarwa, ƙarfafawar zuminci cikin iyali (dangantaka ko zumuta). Tabi 'ar tana tabbatar da rarrabe-rarrabe mambobin cikin iyali. Galibi, kakanni suke cin moriyar riƙo saboda gogewarsu ko shekarunsu. Su ake ba riƙon yara musamman yaya na fari. Su suke ɗaukan ɗayauniyarsu. Akan ce wa da waɗannan yaran suna da wayo sosai kuma sun laƙanci harshe. Haƙiƙa, suna da gogewa da kuma sihiri na uwaye da kakanni da suka tashi da shi. Yayan fari kuma suna iya riƙe ƙananan ƙannensu. A ƙalla akwai shekaru 20 zuwa 25 a tsakaninsu. Har ya yau akwai zumuncin tsakanin yayan uwa ɗaya.

Wannan tabi'ar kuma, ta bada damar a bai wa uwaye da ba su samu aifuwa ko da suka rasa yayansu a dalilin cuta ko wata alloba da ta kashe yara dayawa. Ana yin wannan rarrabe-rarrabe yaran har cikin iyali masu mata fiye da ɗaya. Don ganin an rage kewar yara kuma da jin daɗin riƙo na yaro ake ba su riƙon yara daga iyalinsu na kusa ko na nesa. Wannan tabi'ar ta ba ma'aurata da ba samu yara ba damar rage raɗaɗin ciwon rishin aifuwa. Wani lokaci waɗannan iyalai suna samun « ɗa » da ya fiye masu ma mutanen da suka zo su taimaka. Zumunci yana da ƙarfi, kuma yaro bai damu da matsayinsa ba. Wani lokacin kuma iyalai masu rufin aziri na arziki suna karɓar riƙon yaran danginsu don su sama masu makoma mai kyau da tarbiya. Marayu ma a bada su riƙo ga yan uwansu ko matane da aka san suna da adalci.

A yi kuma la'akari da ɓullowar wani sabon salo na riƙo da ya karkata wajen samun abun duniya.Kariyar tattalin arziki da ta hadassa talauci ta ɓullo da wani riƙo na ƙetara iyaka da yara. Ana bada yaran riƙo ga mutane da suke ƙetara iyakokin ƙasa da su inda ake sa su ayukkan gida ko yin sana'a. Waɗannan ubannin gidajen nasu suke kula da su kuma su yi tattali dukiyar da za a samu a kan waɗannan bayun Yara ba su san hawa ba sun sabka ba. Waɗansu daga cikinsu, suna iya yin shekaru ba su goma cikin iyalinsu ba, kuma suna rayuwa mai ƙunci da ba a fata. Irin wannan riƙo ana ɗaukan shi kamar bautar yara, da Hukumomin ƙasashen suke hukuntawa, amma rariyar iyakoki na bada damar hakan.A cikin al'umma, uwaye, suna ci gaba bada riƙon yayansu mata zuwa birane don su taimaka wa ƙanan uwaye da aiki ya yi masu yawa ko ma'aikatan bariki, wajen ayukkan na gida. Samun yaro na gida ya fi ɗaukan yan aiki da suka shigo daga ƙasashe maƙwabta. Kambacin riƙo ana ba uwayen da aka ɗauko yaran nasu wani ɗan taimako duk da yake hanyar zumunci aka ba ƙarfi wajen bada yaron. Bincike da dama a Afirika ta Yamma musamman ma Pilon (2005) ya nuna cewa irin wannan riƙo yana nisasa yan mata ƙwarai da makaranta kuma ya bada ƙarin bayani bisa ƙaramci zuwa makaranta.

Riƙo na karatu shi ma wata tabi'a ce da ƙarfafa, da yawanci yan makarantar sakandire sun san shi a lokacinmu. Haƙiƙa kamar yadda Pilon (2205) ya ayyana « In da babu taɓi'ar riƙo ko tashe-tashe, da yara da yawa na Afirika ta Kudu da Sahara, ba sun cimma gurinsu na zuwa makaranta

ba saboda ƙaramcin ɗakunan karatun musamman ma yara na karkara da suke son ci gaba da karantunsu na sakandare da mafi yawa makarantun suna cikin birane. » Rufewar makarantu masu ɗakunan kwana, ƙarancin makarantu masu wurin cin abincin a cikin yankunan makiyaya, ƙaruwar buƙatu na zuwa makaranta ( 3,9 % na kaso na ƙaruwar al'umma a shekara), ƙaramcin makarantu da kayan aiki sun janyo wani sabon salo na riƙo wajen uwan gida. Wannan uban gida yana iya zama wani ɗan uwa, ko kawai sani na haka. Zumunci, taimako da hali na tarbiyar gaba ɗaya suna da ƙarfi kuma zaman riƙo na da daɗi. Yaron da aka riƙe yana riƙe amana ku ba ya mantawa da taimakon da aka masa da gabaya shi ma yana gwada ɗiyauci.Mamba kamar kowa a cikin iyali, yaran riƙo suna samu tarbiya da kulawa guda da sauran yara na cikin gidan.. Sai dai zumunci na gargajiya, da ake yi har a yau, yana son ya kawo ƙarshenshi. Haƙiƙa talaucewar al'umma, shekarun yara (matasa), ƙaruwar buƙatu sun haddasa lalacewar wannan zumunci na tun uwaye da kakanni. Iyalai masu rufin asiri na dukiya sun rage yawan iyali kuma sun rage ƙoƙari da taimakon juna ; iyalai masu ɗan ƙarfi ba su da halin kai yaransu cin yanayi mai inganci na karatu. Matasa da suke fama da zamani nan mai wuya suna wahala wajen sabawa da sabbin sharuɗɗa da matakai na iyalan da za su karɓe su a matsayin yan riƙo. Ana samun matsaloli da suke sanya yara sake ubannin gidaje, wasu suna ma komawa gida su yi watsi da karatu. Al'amarin ta taɓarɓare kwata-kwata har yadda a cikin wani bincke da Sandi (1993) yana gudanar, yana nuna cewa da wasu yan makarantar sakandire da ba suda ubunnin gidaje suna hayar ɗakin kuma su ɗauki ɗayauniyar kansu da kansu. Kuma idan aka yi masu tambaya ko kana ruyawa a gidan uwayenka, uban gida ko wasu, masu bada amsa suna faɗin « nan ina cida kaina ». An bar waɗannan matasan su kaɗai, wannan shi ne sakamoko, taɓarɓarewa zumincin cikin iyalai. Kuma yawan yara ba su iya cigaba da karatun zuwa sakandire, su ko yan mata kai tsaye a korar su domin suna shakkun zaman gidan riƙo da wannan lalacewar tabi'u a birni.

## II. Tabi'u na tarbiya

### 2.1. Dubarar koyo ta gargajiy

Tarbiyar gargajiya da ta danganta da yanayi na tattalin arziki da zamantakewa ta da manufar horar da mayaƙa da su kare al'umma, manoma da makiya masu aikin hannu da su ƙera abubuwan amfanin da al'umma ta buƙata don ta rayu.Umurni da tarbiaya, har kullum a haɗe su. Moumouni (1964) na cewa*« inganci wannan tarbiya ya danganta da alaƙa da take haɗa shi da rayuwa, lalle, daga halaye na al'umma da kuma alaƙar al'umomi (rayuwar iyali, sabgogi iri-iri na jama'a) ake gudanar da tarbiya yara da ta matasa ».*

Ɗaya daga cikin alamomi na tarbiya gargajiya shi ne tsari na gaba ɗaya, tana kan kowane mutum na cikin al'umma. Ana yin ta ta hanyar nishaɗi.

Dukkan manya da suke cikin al'umma suna da hakki da nauyin bada tarbiya ga yaro a cikin muhallinsa. Ko bada gargaɗi ko hukunta laifi ga kowane yaro a kowane lokaci kuma a ko'ina. Babban da ba ya girmama waɗannan sharuɗɗa ba ya da wuri a cikin da'irar lattijawa na gari kuma ba ya bin waɗannan ka'aidoji za a ɗauke shi a matsayi maras tarbiya.

A zahiri waɗannan aike-aiken sun maida yaro wani karan ɗori tsakanin ma'aifiyarsa da kewayensa, kuma da ya fara iya magana da kyau, misilan yana shekaru ukku. Waɗannan

ayukka suna zamemasa kacicansa na maimaitawa da riƙewa saboda ana son maimaita daidai saƙon ga wanda za ya karɓa. Yana koyon girmama na gabansa, daga nan ne yake fara amfani horo da ya samu a fanni ladabi.
Dubarar da aka fi sani a Afirika ta dogara da gargajiyar baka inda gatana, almara, kacici-kacici, waƙa da karin magana suke taimakawa wajen horo na ɗan adam. Salifou (1977), zanawar Sandi (1993p. 34), ya rubuta :

> *Labaranmu na tarifi da almarai sun bayyana al'amura na jama'a da suka yi tasiri kuma sun ɗaukaka jan ƙoƙari gorzaye, jarumai mazan jiya (…). Su kuma gatanananoninmu suna ƙumshe da ɗumbun arziki da bai da iyaka,da halin ruyawa ta ɗan Adam da ban dariya (…). Ita ko ɗa'aana fiddo ta daga wani hukunci da aka yanke a kan wani laifi, jin daɗi bayan wani takaici, taɗa kai kuma da bisani wasa, tausayi, gaskiya, yarda, kirki da mazakuta.*

Bayan aikin al'umma wajen bada tarbiya, ana so manya su gwadi halayen da yara za su yi koyi da su. Duk babban da ya bujerawa wannan yarjejinya, za a hukuntar da shi.A titi, ana koyo daga hanyoyi na nishaɗi, kodayaushe ta hanyar tarin ɗumbun bayanai na karin magana, gatana da kacici-kacici..

**2 .2. Koyo na zamani**

Tarbiyar zamantakewa ta yaro na Afirika tana gudana cikin da'irorin iyali da al'umma ta hanyar matakai na koyarwa da suka dace. A sharen wannan hukuma ta uwaye da kakannin sai aka girka makaranta boko, ita ma da nata wuri na ginshiƙin ilimi kuma da tarbiyar zamantakewa. Idan iyali ko al'umma ta bada ƙarfi wajen bunƙasa tabi'u na ɗa'a, ƙaƙa makarantar boko za ta tunkari wannan ɓangare na usalar koyarwa ?

A ƙasar, an kawo zancen wannan matsalar inda cikin sunan minstan ilimi na ƙananan makarantu aka yi amfani da laƙanin horo kan yanƙasanci da ɗa'a. Tun tuni jadawalan koyarwa na piramari (1987) ya ƙumshi darasin horo kan yanƙanci. Karantu horo kan yanƙasanci ya dogara « da sani da tabi'a ta hanyar koyi da al'umma ta yarda da ita kuma horon yana da manufar ganin yaro ya laƙanci halaye nagari da lura da aikatawa ta muhimman tabi'u na zamantakewar al'umma. Horon yana ba yara damar laƙantar iya-zama cikin al'umma. Gurirrika da ake so a cimma ta hanyar darasin ɗa'a kamar yadda cikakken jadawali ya ayyana su ne :
- laƙantar halaye nagari a aji na ɗaya da na biyu
- Aiwatar tabi'u nagari da sani na halaye na zamantakewa a aji na 3 da na 4 ;
- Ganar da yara fahinta da kuma aiwatar da halaye na zamantakewa a aji na 5 da na 6.

Jadawalin ɗa'a yana bada ƙarfi wajen manufar abu mai kyau da maras kyau da mai amfani; taimako da haɗin kai, gafartawa, aminci da danganta dukkan wasu halaye da za su taimakawa yaro ya girku cikin al'umma.
Bayan wannan mahimmancin na wannan darasi, bincke-bincike dayawa kamar su Chétima (1989) ; Souleymane (2015) ; Issa (2018) sun nuna cewa ba a koyar da tabiya kan yanƙasanci

da ɗa’a kamar yadda ya kamata. Waɗannan marubuta sun alaƙanta wannan hali na zahiri a wani ɓangare a rishin laƙantar abubuwan da darasin ya ƙumsa, a wani ɓangare kuwa da dubaru da ake amfani da su.Don haka ƙaƙa malamin makaranta za ya iya haɗa fusa’o’i dabam-dabam da ake aiki da su cikin iyali na gargajiya don cimma gurirrika tabiyar yaro ?
Haƙiƙa, horon na hali da laƙantar ingantattar ɗa’a yana ga iyali. Daga iyali ne ake gina mahimmanan tabi’u. Uwaye suke kula da shigar tufafi na yaro, ladabi, gaskiya. A gehen da’irar iyali,al’umma, wasanni, tsaraye su ma makarantu ne na samar hali : zaman tare, gaskiya, ƙoƙari, jimiri, sanin ya kamata, ɗiyauci.
Horo na ilimi yana bada damar samu matsayi na laƙantar harshe (salo na magani, gatana, almara, zurfin tunani da misalai na musamman : karin magana, kacici-kacici, tattaunawa a kan matsala dabam-dabam). Waɗansu wasanni ma suna kama da kacici-kacicin ilimin lissafi. Idan ana son a cimma manufa tsarin ilimi da horo,to sai an gadanar da ayukkan ta hanyar wani tsari da ya ƙunshi fusa’o’i dayawa da za su ba yaro damar laƙantar sani, ƙwarewa da ƙarfafa bunƙasarsa. Mahimman fusa’o’i na koyarwa da ake amfani da su, su ne : gatana, kacici, almara, karin magana, tsoro, hira, al’adu, ds.
**Shawarwari :** ɗa’ada tarbiya kan yanƙasanci darussa biyu ne masu mahimmanci wajen tattalin tabi’u da al’adu da ba a kula da su ba kuma da ba a koya su da kyau kamar yadda marubuta da muka zana suka rubuto da kuma misalan da za mu bada nan gaba. Muna ba malaman makaranta shawarar dogara da karin magana, kacici-kacici, tattaunawa, almara a matsayi halaye na koyarwa.
A babbar tsangayar makarantar share-fagen karantu (Shekaru 5-6) jigo na farko na darasin ɗa shi ne ladabi da za a gudanar a zaman aiki 4 : Ina kwana, ina wuni, na gode da sai an jima. Dukkan zaman ayukkan suna gudana cikin wannan tsari da za ya biyo baya :
**Takardar darasin wata malamar makaranta a 2020 /2021**
Jigi : ladabi
Tsawon lokaci na zaman aiki : minti 10
Babban guri : Ya kamata yaro ya zama mai ladabi (ya ƙarfafa halayen nagari)

Guri na zaman aiki na ƙarshe: Ya kyautu yaro ya iya faɗi « ina kwana » ba tare da wata tangarɗa ba
Gurirrika zaman aiki na tsakar darasi : Ya kyautu Yaro ya iya :
Sauraren malama cikin natuswa
Gano kalmar « ina kwana »
Maimaita kalma
Bada amsar ƙananan tambayoyi
Karfafa halaye nagari
Jan hankali : malama ta tambayi yara : Da safe idan kun zo makaranta mi kuke ce wa tanti (malamar reno) ? Su bada amsa, « lafiya lau, yaron da yake yin haka, ƙaƙa yake ?Gano kalmar ladabi.
Tafiyar da aiki ta hanyar jerin tambayoyi :
Tunawar jan hankali. Da ka shigo aji mi su tanti suke faɗa muku ? « Ina kwana da ina wuni ? » Ina kwana. Don mi kuke gaida tanti ? A makaranta kawai ake gaida mutane ? A’a, a gida, bisan

hanya. Don mi ya kamata a gaida mutane ? Ladabi ne, kenan mutane masu yin haka ana cewa suna da ladabi kuma muna son mu yi koyi da su.
Saƙo na musamman : ya kamata kullum in gaida mutane
Maimaitawar gaba ɗaya kafin mutum ɗaya.
Bayan sati ɗaya a maimaita darasin da kalmar « ina kwana », da kuma « sai an jima » da « na gode ».
Wannan jigo ya fara 9 ga watan 10 na 2021 har zuwa 2 ga watan 12 na 2921 tare da maimaita darasin ba canji a cikin zaman ayukkan dayawa. Ba tare da an kula da halin koyawar ba, ana iya ganin canjin na zahiri da wannan koyon ya kawo wa yaro. Wannan darasin kamar yadda ya gudana yana yi girka wata tabi'a da ake so ? Tun da yaro ya san waɗannan tabi'un na gaisuwa tun cikin iyalinsa. Hakan bai isa ba, ya kamata malam ya gabatar da ayukkan da za su ƙarfafa wannan sani saboda al'adunmu suna ƙunshe ɗumbin arziki na tabi'u da malamai za su iya amfani da su wajen tsara ayukkansu na koyarwa kamar su gantana da ta ƙunshe da hayen : saurare, lura, walwala, ƙarfin tunini ds.
Mu ɗauki misali bisan « Binta marainiya » wata gatana da aka sani sosai a Nijar da akan iya amfani da ita wajen jan hankali na tafiyar da darussa dayawa na ɗa'a. « Don tabbatarwa da yarsa tarbiya, ma'aifin Binta ya sake yin aure bayan rasuwar matarsa, uwar Binta ». Amma matar ba ta da kirki ko kaɗan. Yunwa, ayukkan gida masu wahala su kaɗai take sa Binta.
.
Wata rana, matar ta ba Binta kashi lokacin da ta sanya wanke ƙwarya har ta kai da hancinta yana jini.

- Muguwar yarinya ! tashi ki wanke ƙwarya a « tabkin aljanna ! »

Yarinya ta aikata umurnin duk da ta san da « tabkin aljanna » yana da nisa, nisa ƙwarai…kuma bisan hanya akwai matsaloli. Da ta gaji sai ta nemi wani icce ta futa. A nan ta haɗu da wani tsofo da farfarun tufafi ya yi mata gargaɗi kamar haka :

- « yan mata, na tausaya miki ; na samu labarin rishin adalci da kike fuskanta. Ki aje hankalinki, ki yi haƙuri. Ki ƙarfafa kirkinki. Kar ki fasa tabi'arki ta ladabi ;
- Ki yi amfani da ita cikin wannan wahalar taki wata rana za ki ji daɗi cikin wannan tafiya. »

Ta saurari jawaban tsofon kuma ta yi aiki da su, hakan ya sa ta fidda tsoro cikin tafiyar tata. Can sai ta iso « tabkin aljanna », an bata ƙwarai guda huɗu da aka umurce ta da fasa a wusu wurare bisan hanyarta ta komawa.
Bisan hanyar ladabinta (gaisuwa da godiya) sun sanya ta samu ɗumbin arziki.
Ta dawo garinsu da duk arizikinta, Biyamaradai, sarakuna suna zuwa suna neman aurenta a wurin babanta. Ta zaɓi yin aure da sarki garinsu.
Muguwar macen ta mutu da baƙin cikin
Cikin wata ganatar ko an ce muguwar matar ta haukace, tana ba yar cikinta kashi tana tilasa ta tafi « tabkin aljanna » amma rishi ladabinta, bala'i ya cimmata kuma ta komo da mugun abu.
Malaman makaranta suna iya cin moriyar wannan gatana wajen koyarda ɗa'a da ladabi cikin jigunansu na jadawalinsu na karatu, tsawon shekara guda ko fiye da haka. A taƙaice, gatana

madogarar koyar ce mai jan hankali cikin koyar da halayar ɗan adam da ɗa'a. Banda nishaɗi na gatana, ana a yin amfani da ita wajen sosa wa yaro rai. Gatana tana bayyana :

- Tabi'u na ɗa'a da suka ƙunshi badawa, haɗin kai, kuzari, ko kuma miyagun tabi'u (ƙeta, rishin godiya, cin amana, sata, rowa, maƙo, ds.) ;
- Kuma, tabi'u da halayen na ɗan Adam, tushe wannan al'umma, al'ada, mi ya sa aka hana abu.

Ingancin gatana, karin magana da kacici, ya dogara da dubaru na bada su. Halayensu na maimaitawa yana da mahimmanci wajen shimfiɗa tabi'u da ake son ƙarfafawa. Kenan gatana tana ƙarfafa hali kuma tana canza wasu tabi'u na ɗan adama, tana ƙarfafa ilimi, da maimaitawa da koyon harshe. Ganata tana iya zama wata madogarar koyarwa a makarantar boko.

**Kammalawa :**

Ra'ayin gargajiya na iyali a Nijar kamar dukkan ƙasashe na Afirika ya dogara da haɗin kai. Manufofin da ake son su ne na bunƙasa haɗin kai, hulɗa da kuma dukkan wasu tabi'u da za su taimaka wajen cimma gurirrika da ake so a cimma. Banda tabi'u na addini, ana koyar da tabi'u na ɗa'a ta hanyar fusa'o'i na nishaɗi da suke da ma'ana a wuri yaro. Wannan koyo ana yin shi ta hanyar maimaitawa da horarwa. Yana aiki da sani na ilimi da na zahiri, hakan yana sauƙaƙa girkuwa. Fusa'o'in koyarwa suna da sauƙi kuma ana iya amfani da su kamar sani na share-fagen makarantar boko. Nazarin takardar darasin ɗa'a yana ba mu damar gani yadda wata gatana da aka sani sosai ta zama madogarar koyarwa ta jigunan dayawa na koyar da ladabi da ɗa'a a mataki dabam-dabam. Taga kowane hali, gatana na cika aikin ta hanyar nishaɗi ( hali na wasanni),hali na tarbiya ( darasin ɗaya) da hali na koyo ( kai saɓo na tabi'u).

**Madogarai na littattafai da ake yi amfani da su wajen bincike**


Amani, A. (2003). *Causes de la Négligence de l'Enseignement de la morale*, (mémoire de fin D'année d'inspectorat), ENS Niamey, 43 pages.

Moumouni, A. (1964). *L'éducation en Afrique*. Paris Maspero édit., 1964, 399 p. (II, C, 1).

Chétima, M. (1989). *Instruction civique et morale au cours moyen*. (Mémoire de fin d'études pour l'obtention du diplôme d'inspecteur primaire) Faculté de Pédagogie Niamey.52pages

Erny, P. (1988). *Famille, enfant et développement en Afrique*.Paris, UNESCO, Weva, pages. 22-38.

Farad, M. (2015). « *Éducation à la citoyenneté et aux droits de l'homme* », Manuel pour les Jeunes au Maroc, page 43.

INDRAP, (1990). *Programmes de l'enseignement du premier degré : instructions*. Niger. Ministère de l'éducation nationale. Maison d'Edition et de Diffusion du Sahel, pages 111

Issa, M. (2018).*Analyse de l'enseignement de l'éducation civique et morale au Cours Moyen 2ème année dans l'inspection de l'enseignement primaire de Maradi1.* (Mémoire de fin d'études pour l'obtention du diplôme d'inspecteur primaire). ENS, Niamey.Pages 56

MEN/A/PLN, (2002). *Recommandations N° 12 et N° 13 du rapport de l'atelier tenu à Niamey sur l'éducation civique et l'éducation à la citoyenneté*.

Sandi N. A. (1993). *Analyse théorique de quelques déterminants du décrochage scolaire dans l'enseignement secondaire au Niger*. Thèse de Doctorat Université de Mons Hainaut.

Souleymane, F. (2016). *Impact de la négligence de l'enseignement de la morale sur les élèves de l'école primaire : cas de l'IEP de Kollo* (Mémoire de fin d'études pour l'obtention du diplôme d'inspecteur primaire). ENS, Niamey

Pilon, M. (2005). *Confiage et scolarisation en Afrique de l'ouest : éclairages à partir des sourcesdes données démographiques.*https://horizon.documentation.ird.fr/exl-doc/pleins_textes/divers13-11/010050067.pdf

UNICEF (2018). Aperçu du pays Niger https://reliefweb.int/report/niger/aper-u-du-pays-niger-july-2018

Roger J. (2010). *Comment enseigner l'éducation civique et morale à l'école*, Bruxelles, De Boeck.

**Babi na 5**

## Koyarwa-koyon zance na almara na Afirika ta yamma : daga makarantar gargajiya zuwa makarantar zamani

**Abdu Mumuni Issufu**

**Taƙaicewa** A Afirika, Almara tana ɗaya daga cikin mahimman jinsina na adabin baka. Kuma almara wani abu ne na koyarwa a makaranta gargajiya ta maroƙa. Zubin labarin almara yana buƙatar ƙwarewa da mai koyon da za ya laƙanta a tsawon lokaci mai yawa na horo a ƙarƙashin manyan masana na gargajiyar baka. Da yake ya dogara da fusa'ar koyarwa, wannan binciken yana ɗora ayar tambaya a tsarin koyarwa-koyo na zancen almara a Afirika ta yawwa a makarantar gargajiya da kuma yiwuwar koyar da almarar a makarantar boko. Wajen tafiyar da bincike na gudanarwa, hanyar da aka amince da ita za ta bayyana dubaru na sadarwa da masu bada bayanai, ta ƙayyade wuri da al'umma za a yi nazarin a kanta, tana nuna fusa'o'i na tattara bayanai ta hanyar tattaunawa, ɗaukan rahoto da kuma yadda za tace bayanan da nazarinsu. A wani ɓangare ko binciken na kammala cewa horo na koyon aiki na mai koyon roƙo da ake yi ta hanyar makaranta ya dogara da wasu matakai da sharuɗɗa, dubaru da mizantawar koyon, da daidaitar da shi da yanayi na jinsi da kuma matsayi dabam-dabam. A wance ɓangare kuwa, binciken yana gwada wasu hanyoyin na koyar da shi a makarantar boko.

.

**Mahimman kalmomi :**Koyarwa-koyo, labarin almara, Afirika ta yamma, makarantar gargajiya, makarantar zamani

### Gabatarwa da gurirrika na babi

Wannan babi yana kawo bayani a kan koyarwa-koyo na wani jinsi mahimmi na adabin baka na Afirika. Wannan jinsi na adabi, shi ne almara da aka koyo ta hanyar faɗi da saurare kafin a fara rubuta ta bayan an yi ayukkan tattara bayanai, na rubutawa da na yaɗawa daga masana da dama, turawa, amurkawa, asiyawa, afirikawa ds. A Afirika ta yamma, ana a yin almara musamman ma ta hanyar wani hayi na matsayi a cikin al'umma, na maroƙa. Cikin wannan hayi, idan ana son a zama mai bada labarin almara, wato ƙwararre na iya almara, maroƙi za ya tafi makaranatr gargajiyar baka a ƙarƙashin manya-manya masu zubin labarin baka.Ya zaman tilas, masu koyon su iya ƙirƙirawa, bada labarin da kuma iya koyar da irin wannan salo na magana. Horon yaran maroƙa ya dogara da wani hali, na zuriya cikin wata hanya bayyananna. Horo na gargajiya, yana ƙarfafa bunƙasar iya magana a wurin masu koyon. Hanyar koyar da almara a makarantar gargajiya ta maroƙa da ake bayaninta a cikin wannan babi, ta dogara da gogewa ta koyarwa da cibiyoyi ukku na horo na mutanen da suka laƙanci magana (Camara 1992). Waɗannan cibiyoyi suna a ƙasar Nijar da Mali. Wajen tattara bayanan, mun yi aiki da dubaru na sadawa da masu bada bayanai, ta ƙayyade wuri da al'umma za a yi nazarin a kanta, tana nuna fusa'o'i na tattara bayanai ta hanyar tattaunawa, ɗaukan rahoto da kuma yadda za tace bayanan da nazarinsu ( a cikin binciken ba za ɓata lokaci ba wajen hanyar da aka bi). A fanni

na biyu na lamari, hanyar bin ta dogara da wani tsari bayananne na koyarwa-koyo, wannan fanni shi ne makarantar zamani ta hanyar wasu manufofi na koyarwa. .

Wannan binciken zai bada da farko ma'anar labarin almara, ya bayyana siffofin bambancinta, da matsayinta da amfaninta a cikin al'umomi na gargajiya na Afirika ta yamma. Daga nan, binciken zai yi nazarin tsarin koyarwa a makarantar gargajiya a Afirka ta yamma ta maroƙa kafin ya bada hanyoyin na koyar da almarar a makarantar boko. Guririkan da ake so a cimma cikin wannan babi sune :

1. Bada ma'anar jawabin almara;
2. Sani matsayi da amfanin al'mara cikin al'umomi na gargajiya na Afirika ta yamma ;
3. Gano tsarin koyarda almarar Afirika ta yamma a makarantar gargajiya ta maroƙa ;
4. Bada shawara a kan hanyoyi na koyar da almara Afirika ta yamma a makarantar boko/zamani

**Ma'anar labarin almara**

A Afirika ta Yamma, labarin almara wata tabi'a ce ta al'umma, ta aiki da ta samo tushe da daga mutanen da suka laƙanci magana (Dérive, 2012) kuma da suka samu horo don gunadar da wannan aiki na bada labarin almara. Al'mara wani « jawabi ne na gargajiyar baka » Bornand, 2005, p.14). Kirƙira ce ta baka da maroƙa a cikin wasu halaye ma musamman suke badawa a bayyane, ayukkan masu kyau na mayaƙa, na tarihi da suka kasance jarumai a can da.Zubin labarin ya danganta da masu saurare da aƙidar labarin da mutanen almarar suka zo da shi. Cikin tsari bada labarin almara, mai bada labarin yana amfani da fusa'o'i, da dubaru na yin jawabai, da hikimomi na bada labari don ƙara daɗin salo na labari. Labari na baka, zubin labari na almara daga maroƙa yana son a yi amfani da dukkan halaye da ake aiki da su cikin magana (motsin jiki, gatsine, dariya, kallo da murya, canji karan sauti, daga murya, sabka da hawan murya ds)

Gurin mai riƙe da gargajiya ta hanyar bada labarin almara shi ne a wani ɓangare ya janyo hankalin masu saurare da suke jin daɗin mazakuta da jan ƙoƙarin da mutanen suka bada. A wani ɓangare kuwa don labarin ya zamna cikin kawunan mutane kuma ya zama abun tarifi » (Saibou Adamou & Issoufou, 2020). Almara a matsayin tabi'a ta jawabi ta bambanta da sauran labarai daga wasu alamomi na bambantawa.

**Wasu alamomi na bambanci na jawabin almara ta Afirika ta Yamma**

Almara ta Afirika ta Yamma cikin jawabanta ta bambata da salo dabam-dabam na jawabin baka da kowa yake iya faɗi, kuma a kowane lokaci da kowane hali. Cikin bada labarinta, almara ta bayyana wurin bada ta. Galibi ana bada labarin almara da wasu wurare na musamman da aka shirya da hakan : dandali, da'irar cika dare, ƙofar fada sarki, lokacin naɗin sarauta, ko wasu shagulgula ma musamman cikin zamantekewar al'umma. Cikin wani hali, ana yi wasu girke-girke na tsahi a wurin da za bada almarar. Ana :

> Gudanar da ita a wani dandali da a ƙayyade, a keɓe ko aka binne wasu sihirai na kariyar kewayen wandan za ya bada labarin almarar- kamar yadda yake da shigar tufafi ta musamman da kuma aiwatar da wasu ƙa'idoji na halaye-kariya

da iskoki na magana da labarin ya ƙunsa da shi maroƙi yake rike da.(Seydou, 2008, p.152)

Ana aiki da iskoki na karayi don ganin a gudanar almara cikin lamin lafiya. Gurin shi ne na ganin an kare mai bada labrin almarar da jama'ar da take sauraren shi da kuma ganin a gudanar da tsarin bada almara ba tare da wata matsala ba. Amma yau, da ake fuskantar ɓacewar dare na bada almara, a ƙirƙiro wani shafi na zamani na bada almara. Kafofin watsa labarai na jama'a da kuma masu zaman kansu da suka zama hanyoyi ma fi inganci na yaɗa jinsi na labari.

Wata alama ta almara a Afirika ta yamma shi ne lokaci na bada labarin. Idan aka bambata da wasu jinsina na labarun baka da aka fi sani, ba a bada labrin almara a kowane lokaci, ana yi almara a wasu dalilai na musamman na rayuwa ta zamantakewa kamar misalin, al'adu na gargajiya na tsarance. Cikin waɗannan shagulgulan maroƙa suna bada jinsi almara da wani salo na magana. Lokacin da aka sa wajen aiwatar da labarin yana tsawo (Biebuyck, 2004). Yana iya kaiwa awoyi biyu zuwa kwanikkai. A ganin (Seydou, 2008), ana bada labarin almara ta ainafi ta Soudjiata wajen shagulgulan gyaran wani wuri na ibada da ake yi dukkan shekaru bakwai da ake ce wa kama-blon a Kangaba a Mali. Banda lokacin almara na musamman, ana kuma aiki da jama'a da ake yi wa almara. Masu sauraren sun haɗa da mutane masudaraja da lattijawa kuma nutsattsu. Misali, kamar yadda (Seydou, *Ibid*) ya ce, sanannar almarar ta manding ana yi wa maroƙa gargajiya da suka shafi gidajen sarauta. Saɓanin hanka alamra da ta danganta da wata jarumtaka, ana yin ta ne a gaban waɗanda suke yin irin wannan jarumtaka don tunatar musu da ƙoƙarin da aka cikin wannan fannin har zuwa yau..

Daga cikin dukkan jinsuna na baka, na waƙe, kirari ko na bada labari, almara ta sha bamban, soboda tana tafiya da kiɗa. Da maganar da kiɗan suna tafiya tare don su ƙara armashi ga labarin da maroƙin yake badawa. « Aikin kiɗin », (FobahEblin, 2006, p.447) yana bada wani daɗin sauti kuma yana taimakawa wajen tsara jawabi. A ganin Kesteloot da Dieng (2009, pp. 30-31) « idan babu sauti [kiɗa] matanin almara yana ɓadda tashinshi shi kuma maroƙi yana ɓadda basirarsa ». Maganar almara tana da mahimmanci cikin dukkan mahallai na gargajiya, inda ta ɗauko tushe.

**Jawabi na almara : matsayi da amfani cikin al'umomi na gargajiyar Afirika ta yamma**

Cikin al'ummomi na gargajiyar Afirika ta yamma, jawabi na almara yana mahimmin matsayi cikin hanyoyi na horo da na nishatantarwa al'ummomi. Cikin fasalin jinsina na labarin baka, almara tana cikin manyan jinsina na labari. Almara ita ce adon labarin baka na nahiya Afirika a saɓanin ƙananan jinsina na labarai. Ana ganin mahimmancinta daga amfaninta a cikin al'adu na mafi yawan jama'a. Da farko, almara tana taka rawar gani wajen nishatantarwa. Bada bayani lokaci na jin daɗi da fara'a a wajen al'umomi. Hanya ce wadda take ba su damar walwala. Sauraren jawabi na almara yana sa a yi dariya ga mutanen da suke shan wahalar aikin gona kamar yadda mutane na zamani suke cikin sakata ta aikin yau da kullum. Ta hanyar kawo amsa ga buƙatu na yawa, buƙatu na « saurare da bada tarihi » (Chevrier 2005, p.25), yana cika ayukka na tsarkakewa da na waraka. A wani wuri kuma, labarin almaarar yana tada tsime da jin ƙarfi daga masu saurare saboda abubuwa ake faɗi. Wannan jawabin yana sa a ji wani daɗi saboda magana da ta tafiya tare da kiɗin. Almara ta sanya ji daɗin matani cewar

Barthes (1973), daɗin da ake sanyaal'umma ta rikice. A wani sa'i, ana ma iya cewa « jin daɗi » na jama'a a lokacin da ake bada labarin almarar.

A wani lokaci, jawabin na almara yana taka rawar gani a fannin siyasar ɗan Adam da ra'ayi inda za a haskaka mutumen cikin almarar da ya ɗauka wasu halaye a lokacinsa. Ta hanyar girmama wasu manyan tabi'u, za su zama abun koyi ga mutane na zamani a cikin al'umma. Saƙo na almara yana sa mutane su tashi tsaye a ƙarƙashin wata hukuma da take ɗauke da wani ra'ayi na gaba ɗaya inda kowa zai kawo ƙoƙarinsa. Kuma ana ganin almara za ta iya bada damar haɗin kan al'umma. Maganar almara tana gwada musu yadda ya kamata su yi halayen da ake jira a gare su, yadda al'amura na rayuwada suka wakana, addinansu da kuma abubuwa na koyi da ya kyautu a ce sun yi haka. Jawabi na ainafi, almara tana gwadin hanyar ƙirƙira wasu « sabbin samfarirrika na al'umma » (Vettorato, 2017, s.p). Jinsi na almarayana bada misali na tafiyar da al'umma, jagora na jama'a inda mahimmin aiki almarar shi ne na siyasa, aƙida, zamantakewa (Camara, 1996).

Idan jawabin almara yana sanya walwala kuma yana haɗa kan al'umma, to yana kuma tabiyantarwa. Yana da amafanin wajen koyarwa da aka gano wajen yaɗa halaye da ɗa'a da kuma tabi'u na zaman tare. Almara wani karatu na koyar da ƙoƙari da kuzari da jarumtaka ko da mutun ya fuskanci wata matsala ko rishin adalci. Jinsi na almara yana koyar da kishin ƙasa da amincewa da hali na girmamawa da kuma hukunta miyagun halaye.Almarata Afirika ta yamma na cika matsayi dabam-dabam da ya haɗa nishanɗantarwa da koyarwa da kuma janyo hankalin al'umma ta siyasa wajen wannan mutum na almara. Dukkan waɗannan wujjoji suna bayyanamahimmancin koyar da almara a makarantar gargajiya na maroƙa

**Tsarin koyar da jawabin almara Afirika ta Yamma a makarantar gargajiya maroƙa**

A Afirika ta yamma, horon yaran maroƙa a kan jawabin almara yana gudana ta hanya biyu : cikin iyali, wuri da ya fi dace da wannan horo da kuma da cikin makaranta, fannin koyon aiki. Muhallin iyali shi ne da'ira da aka sani wajen horon yaro kamar yadda Ogandaga (2007, p.6) « Iyali ne wuri na farko inda ake koyon tabi'a ta biyayya, girmamawa da ladabi ga na gaba…waɗannan sune mahimman tabi'u cikin al'umma gargajiya. Iyali ne da'ira ta farko inda matashin maroƙi yake yin taki na farko na koyon magana a wurin ma'aifansa.

Kuma, koyo gadan-gaban ana ci gaba da shi cikin wani yanayi na zahiri « makarantar koyon aikin kai kaɗai [a fannin almara] » tana bada damar samar da sani da ƙwarewa da halaye da suka danganta da matsayi a cikin al'umma da matsayi na aiki » (Diouf, Mbaye &Nachtman, 2001, p.8). Wurin horo kan « aikin roƙo » ya shafi makarantun gargajiya na maroƙa (waɗanda aka yi binciken a kansu : Saga, Libore a Nijar da Kirina a Mali) Cikin waɗanda wurare ana koyar da jawabin almara ta hanyar wani tsari da yake buƙata wani tsari na koyarwa Camara, 1996, p.768) da matakai da sharuɗɗa.

A makarantar maroƙa, koyar da basirar almara ta gumshi wasu sharuɗɗa. A wajen samun horon, ya kamata a ce ɗan makaranta magadi ne na zuriyar maroƙa (Enkerli, 2004). Ko da kuɗi, ɗan gidan sarauta ba za samun irin wannan horo ba. Idan ana son fara koyarwar kamar yadda aka gaya muna, ya kamata a ce yaron yana da shekaru 7 ko 8, shekaru da suka cancanta a wajen koyon da kuma samun labarai. Wani amfani na shekarun shi ne yara ba su da wani

tunani a kansu a wannan shekaru da za ya hana su koyo. Kwalluwarsu ba ta cika «  cewar  wani mai bada bayanai.

Kafin a je makaranta gargajiya, za yi wa yaro mai samun horon wani shiri na musamman na tsari. Wannan shirin yana iya ɗaukan siffar wani tsari na al'ada da ake sha ko a yi wanka (Hall, 1990) da ruwan da aka wanke jariri da ya fito daga gidan sarauta ko gidajen na masu kuɗi. Wannan al'ada ita ce shaida bada sa'a cin nasarar wannan aiki na roƙo da kuma matsayin aikin a wurin maroƙa da cikin al'umma. Bayan wannan kuma akwai shiri na musamman na matashin. Za a aiki iskoki da magunguna iri-iri da layu da su ƙarfafa ilimin yaro da basirarsa ta saurere da maimaitawa. A ƙarshe sai kuma an tabbatar da ya laƙanci wasu abubuwa na musamman cikin harshe(Dolz & Schnewly 1998, p.16).

Koyarwa a makarantar maroƙa, a fanni na almara tana da sharuɗɗa. A matsayinta na aiki na ɗan Adam da na horo, koyarwa na dogara da abubuwa kamar haka :

- Saurare ;
- Haƙurin saurare ;
- Da kuma bada gaskiya.

Horo ana yin shi  da baka, mataki na farko shi ne saurare da kyau na duk abun da ubangijin horo ya faɗiDa farko akwai mataki na kafin saurare inda ake gyara halaye masu koyon da sanin da za su laƙanta da kuma iya shiga gaban magana. Mataki na saurare shi ne nutsuwa bisan abun koyon kafin mataki na bayan saurare.

Horo a kan jawabin almara ya ƙunshi wani adadi na matakai. A 2011, cikin wani rahoto na Garba, Djéliba Badjé[1]ya kawo zance mahimman sassa guda ukku :

> Da farko a shekara 7, yaro zai fara « ceeyan » (Kirari) ko « kaayi ceeyan » (kirari na kakannin-kakanni), cewa da kirari na sunaye kakanni na iyalin sarauta ko zuriyarsu. Bayan wannan sai koyon Deede, cewa da tarihi na mayaƙa ; a ƙarshe, sashe na ukku shi ne na koyon Moolo, kiɗa ma raƙa bada labarin (pp.17-18)

Sashen na farko yana dogara da koyon salsala cikin kalamai na washi da ake yi wa iyalai da suke da wani matsayi a cikin al'umma da ya danganta da arziki ko wani hali nagari. Daga nan a gayyaci mai koyon don ya bi badawar tarihi na jarumtakar al'umma. Sashe na ƙarshe shi ne koyon kiɗa. Amman wannan sashe sai in kana so tun da bai zama wajibi ba.

Tsari ne  zahiri da ake ganewa inda ake gudanar da ayukkan horo. Ana amfani da wasu buƙatu na makamashi kamar su icce na ƙuna, karan hatsi. Yaran maroƙan sune suke tattarawar waɗannan kayayyakin aiki. Don saboda cikin hasken wutar iccen ne ake bada horon, da ubangijin horon yake bayarwa. Wajen girka sanin, maroƙi mai bada horo yana amfani da fusa'o'i na koyarwa cikinsu mafi mahimmanci ita ce ta bada labarin almara gaba ɗaya ko ɓangare ɓangare (cewa wasu daga cikin sassan almarar. Cikin wannan mataki shi ne jarumi na aikin koyarwa suko yan koyo masu saurare. Bisan wannan akwai hikima ta maimaitawa  inda ake sake jaddada maganganu da aka faɗi.

---

[1] Djéliba Badjé wani babban maroƙi ne na salsala a Nijar. Ya jagoracin babbar ƙungiyar maroƙa ta ƙasa a tsawon shekara 5.

Dubarar da aka fi yawan amfani da ita wajen koyar da jawabin almara ita ce haɗin «  bayyanawa da maimaita » (Toulou, 2008, p.293). Maimaitawa ita ce yin bayani ɗaya bayan ɗaya daga wurin babban maroƙin mai bada horo. Bayan nan yaron maroƙi za ya maimaita dalla-dalla kamar yadda aka faɗi bayanan na farko. Wannan dubara ko wata alaƙa ce tsakanin yaro da maroƙi na koyar da shi. A nan, mai koyon yana yin ƙoƙari kuma yana wuce matsayi mai saurare kawaida yake da a matakin bada labari na galibi. Dubarun ukku da aka yi amfani da su da suka haɗa da bada labari, bayyanwa da maimaitawa ana iya amfani da su ɗaya ba ɗaya ku tare don cimma gurirrikan koyarwa.Cikin gudanarwar aiki na masu koyo, malamin koya roƙo yana amfani da tabi'u da suka danganta da aikin roƙon.  Farawa da iya, za ya bayyanawa yaran nasa sani na koyarwa da kuma sani na koyo. Malamin yana faɗa musu, misali, da aikin yana farawa da bada bayanin tarihi na salsala. A nan abun nufi shi malamin yana yi musu bayani dalla-dalla abubuwa da su koya. Bisan wannan, za ya gaya musu tsarin da koyarwar za ta bi da tilas ƙin koyarwar.

Wajen salon na aiki, maroƙin yana amfani da wata basira ta «  wata hanya ta ga inda yake tattara wasu fusa'o'i na musamman da za su ba yaran damar kula da kansu wajen koyon » (Sensevy, Mercier & Schubauer-Leoni, 2000, s.p).  A matakin na makarantun maroƙan da aka yi bincike a kansu, wannan sauyen ƙwarewar koyarwa yana gudana a matakai biyu. Da farko ana yin shi a farko sabon zaman aiki don binciken sanin ɗan makrantar. Wannan nauyi ya zama kamar wata tilawa ce ta abubuwan da aka karanta. Bayan nan, malamin yana ba yaran ragama inda za ya ba su damar  a wajen wata sabga  su bada labarin wani ɓangare na almarar. Yaran maroƙa suka aiwatar da wannan nauyi na koyarwa a gaban malamin nasu.

Salo na ƙarshe na aiki roƙo shi ne mizantawar koyon da yake ɗaukan suffar larwai na binciken sani. Wannan larwai yana iya kasancewa sake maimaita tarihin ko wasu ɓangarori na labarin da aka yi can baya. Irin wannan mizantawa tana ƙarfafa koyo. Salo na biyu na mizantawa shi ne ƙarshe horo. Ita ce mizantawar kammalawa ka ta gaba ɗaya da ake gudanar da ita a ƙarshe horo. A nan ne malam yake tsira wani babban bikin inda sabon maroƙin za ya gwada basirarsa ta bada labarin almara. Idan ya yi nasara «  jarrabawar » yana samun matsayi na maroƙi mai bada almara.

A yau, a Afirika ta yamma, makarantun gargajiyar baka inda maroƙa suke samun horo kan magana da kiɗa sun taɓarɓare. Ganin hakan ba za a maida koyar da bada labarin almara ga makarantun zamani na ?

1. **Jawabin almarar Afirikan ta Yamma : Fusa'o'i, darassu da dubaru, hanyoyi na koyarwa-koyo a makarantar gaba da sakandire**

Wannan shafi yana nazarin almara a Afirika ta Yamma tamkar wani jinsi ne labari da ake iya koyawa a makarantar boko. Wannan hanya tana iya zama wata madogarar koyar da faransanci a makarantar gaba da sakandire. Amma wannan manufa tana buƙatar a bayyana ma'anar darasi, fusa'o'i da dubaru. An san da cewa jawabin almara yana taka rawar gani a fannoni dayawa waɗanda ake iya koyar da su  a makarantar gaba da sakandire.  Tsarin koyarwa na wannan jawabin ya dogra da :

- Da farko, duk labari na almara yana zuwa da wasu halaye na ɗan Adam da yake cike da darussa ;
- Bayan haka, a fannin tarihi, jawabin almara yana sanya al'umma ta zamani ta gano tarihinsu da kakanninsu ;
- Har yau kuma, almara tana bayyana al'adun Afirika dangance da tabi'u na tushe da al'umomi ;
- A ƙarshe, almara jinsi ne na adabi mai ɗimbun arziki na harshe da salo na ƙarfafa ƙwarewa a fanni harsuna da adabai na yan makaranta.

  Cin moriya wannan gigunan na tarbiya da ake samu cikin almara yana ba makarantar boko damar zama « makarantar faransanci ta Afirika » amma ba « makarantar faransanci ba a Afirika » (Saibou Adamou & Hamidou, 2008, p.58). Manfuwar koyar da almara a Nijar, misali ta dogara da manufofi na jadawalan koyar da faransanci a Makarantar gaba da sakandire :

- Karfafa ƙwarewa ta tattaunawa da bayanin baka na rubutaccen bayani ;
- Bada ƙarfi wajen amincewa da dubaru da fusa'o'i da suke bada damar fahinta, da ƙarfin basira ;
- Amincewa da wata tabi'a da ta danganta da al'umma ta zamaninmu mai ƙofa buɗe ga duniya (jadawalan faransanci na makarantar gaba da sakandire, 2016, p 101)

Manufar farko da aka sa gaba ita ce wadda ta bada ƙarfi wajen bunƙasar « ƙwarewar tattaunawa da bayani na baka da rubutacce ». A wannan mataki, buƙatu na almara kamar wata tabi'a ce ta jawabi, ana iya amfani da su wajen sauƙaƙa bunƙasar ƙwarewa ta tattunawa a wajen yan makaranta. Cikin wannan tsari fusa'ar da aka amince da ita, ita ce fusa'ar harshe ta bayanin matani (Adal 1999). Idan aka dogara da wannan dubara, ana iya koyar da jinsin almara a makarantar gaba da sakandire kamar wani bangare na koyarwa wandan gudanarwarshi ta ƙunshi sassa dayawa. Misali a fanni na nazarin halaye, za ayi aiki da ɓangare na bada bayani mai sautin almara ta baka da rubutacciya

Gurirrika na musamman : ɗan makaranta ya iya :

- Bada tsarin matanin almara mai suffar zubin labari :
- Bada mahimman jaruman da masu biyo bayan su cikin jawabi na zubin labarin almara ;
- Tattance alamomin lokutta da wurare na cikin almara ;
- Wallafa wani zanen allon na bayanin almara.

Gudanar da ɓangare aiki na bada bayani yana tafiya ta hanyar zaman ayyuka da yawa da suka dogara da abubuwan da darasin ya ƙunsa : Cikin zaman aiki na farko, aikin koyarwar yana iya dogara a kan ganowar tsarin matanin almara da abubuwan da ya ƙunsa : nazarin sheɗaru, na mahaɗai da alaƙoƙi da suke bayyanawa don cimma gurin wallafa wata muhimmiyar hulɗa tsakanin ɓangarori dabam-dabam. A zaman aiki na biyu, aikin yana dogara a kan nazarin mutanen cikin almara. Ana cin moriyar abubuwan da darasin ya ƙunsa kamar tsarin matanin almara, mutane da matsayinsu da nazarin fa'ilai.

A kashi na ukku, ana yin nazarin tsarin na lokuttan da wuri na almarar ta hanyar dogara da alamomi na koyarwa kamar su : alamomi da ayukkan lokuttan da na yanayi na wurare, Zaman aiki na huɗu za ya dogara a kan bada labari na tarihi ta hanyar yin amfani da bayanan almara da suka danganta da ra'ayi dabam-dabam na mai bada labarin (ra'ayinsa, abin dogara). A zaman aiki na biyar za a yi aiki kan ƙirƙirar matanin bada bayani mai sautin almara.

Bayan wannan tafiya ta ɓangare aiki na zubin labari, za a ci gaba da nazarin ta wata hanya ta biyu da ake iya koyar da jawabin almara amakarantar gaba da sakandire. Tana dogara da manufa ta ukku ta jadawalan faransanci, ta laƙantar hali da ta danganta da tabi'u da almarar take ƙunshe da su da suka yi daidai da zamain da muke ciki mai buɗe ƙofa ga al'adu na duniya ». Ana son a nan a koyar da tabi'u da suke dogara da halayen da almarar ke bayyanawa saboda « koyarwa, sanar da al'adu ce » (Ourghanlian, 2006, s.p).Lalle, jinsin almara a Afirika ta ymmaa a matsayin wata hanya ta koyar da al'adu da tabi'u, yana ƙunshe da wasu halaye da suke tare da jaruman cikin almarar. Koyar da su a makarantar gaba da sakandire na iya dogara da fusa'ar tabi'a. Cin wannan hanyar koyarwar, gurirrikan da ake so a cimma sune :

- Gano halayen da tabi'u na ɗan Adam da al'adu na gani a zahiri cikin almarorina da ;
- Amincewa da halaye da ake son don sauya hali. Manufar da ake son a cimma ta wannan hanyar shi ne na a gwada irin gudummawar da koyar da al'adu masu kyau a kan yan makarantar gaba da sakandire.

Abubuwan cikin darussa za a koya su ne ta hanyar jigunan na girmamawa, da na kyautatawa, da na bada-kai da yanƙasanci ko son al'umma. Ana iya koyar da cikinwani ɓangare na karutu ɗaya daga cikin ayukkan koyar da da faransanci a makarantar gaba da sakandiren. Dubarar ita ce wata fusa'a kan wani batu. Cikin wannan hanya, dubarar da ta fi dacewa ita ce ta karutu mai matakai kamar yadda jadawalin makarantar gaba da sakandire ya ayyana.

Ma'anar girmamawa ta yaɗu sosai cikin labarai na almara kuma gwarzaye sun yi aminna da ita dangance da amfanin wannan tabi'a ta ɗa'a, wadda take shaida ce ta farin cikin na mutum, mutunci. Mutumen da aka girmama, jarumi ko gwarzo yana nuna isa don samar wa kansa daraja. Ta ga koyarwar girmamawa da darajankawa na matasa ta hanyar bututun almara, makarantar zamani za ta ƙarfafa wani sabon hali na yara matasa, wannan shi ne biyayya da girmamawa. Idan aka samu hali na girmamwa ana iya zama jarumi mai haskakawa a idon al'umma. Tabi'a ta biyu da ake iya samu cikin almara da kuma ake iya koyar da ita a makarantar boko/zamani ita ce kyautatawa. Kyautatawa, tana mahimmanci cikin halayen na jarumai na almara. Wani hali ne da ake so inda mutane suke taimaka wa mutane masu buƙata. Daga anniyarsu ta bada suna, hana kansu da rowa da maƙo na abubuwan da suka mallaka da suke nuna na kowa ne. Makaranatar boko ta hanyar koyar da halaye na badawa zuwa ga yan makaranta ta hanyar jawabin almara, tana taimakawa wajen ƙarfafa danƙon zumunci tsakanin al'umomi don jin daɗin kowa. Hali na badawa yana nuƙushe tabi'ar maƙo da son kai. Tabi'ar kyautatawa tana iya ta sa yan makaranta su san ciwon kansu, manyan gobe da suka gurin ganin al'umma ta bunƙasa in da kowa zai kawo nashi ƙoƙari.

Ana iya amfani da Jinsin almara wajen aika saƙo na bada-kai da son ƙasa. Da haka ne jarumin almar yake shiga cikin ayukkan al'ummarsa. Cikin almara, ayukkan bada-kai da kishin ƙasa suna bayyana ne wajen kawo hari ko baraza ga al'umma, ƙwace garuruwa na kakanni ds. Cikin waɗannan halaye, ana son aka jarumin ya gwada wani hali na a-zo-a-gani don canza wusu halaye na mutanen cikin al'umma. Cikin tashin hankalin jarumin yana nuna wani bada-kai don kare al'ummarsa da ƙasarsa. Mahimmancin wannan horo kan bada-kai da kishin ƙasa a makarantar gaba da sakandire yana bada damar gina wani sabon ɗan ƙasa mai bada-kai da kishi wanda, ba ya da son kai, ko maƙo. Wannan ɗan kasa yana taimakawa wajen ƙarfafa al'amura na siyasar rayuwa, zamantakewa da kuma kare hakin al'umma. Koyar da ra'ayi almara cikin makarantu musamman makarantu na gaba da sakandire wani ci-gaba mai mahimmanci. Koyar da jawabin almara ga yan makaranta yana ƙarfafa ra'ayi na kishi da son ƙasa da kuma bada-kai na halarta.

Ta hanyar girka wasu halaye kamar tsarin girmamawa, taimakon juna, kare ƙasa, mahimmancin koyar da jawabin almara shi ne na ba yan makaranta damar laƙantar wasu halaye na yin koyi da su cikin al'umma. Lamari na koyar da halaye na zamantakewar al'umma da ɗa'a a makarantar gaba da sakandire, ta wannan hanyar yana ƙarfafa tabi'u da ake so da kuma watsi da mugayen tabi'u a cikin al'umma. Hali na koyar da almara yana nufin haɓɓaka tabi'u na koyi zuwa ga matasa. Cikin fusa'o'i biyu da kuma ake yi magana a kai wajen koyar da almara a makarantar zamani, cikin wannan babi, ya wajiba da malaman makaranta su bada ƙarfin kan dubaru na zamani na koyarwa. Malamin makaranta cikin tabi'unsa, yana bada ƙarfi ga ƙoƙarin da kuzarin yan makaranta da suke ma'amala cikin muhallinsu na zamantakewa, almara tana da mahimmanci. Malamin makaranta yana ƙirƙira wasu halaye na koyarwa waɗanda a cikinsu, babban aiki yana dogara da su, ta hanyar samar da kayan aiki da za su ba su damar samun nasarar koyo. Dubara ta zamani ta koyarwa tana buƙatar halartar kowane mutum shi ɗaya ko jama'a gaba daya wajen gina saninsu. Kenan, halaye na koyar da jawabin almara suna girkuwa ta hanyar ƙarfafa ayukkan cikin rukuni. Aikin malam cikin ajinsa shi ne bada damar kowane ɗan makaranta ya halarta wajen koyo ta hanyar fahintar da su al'adu da tabi'u na zahiri a cikin al'ummarsu da ake iya samu cikin almara. Idan aka amince da wannan dubarar da ta gundummawar kowa da kowa, malam :

> Yana sa ɗan makaranata ya lura da gaskiyar lamari ta hanyar halarta ; ta hanyar aiki ne mutum yake gina kansa. Amma amfanin al'umma ne yake sa ɗan makaranta ya halarci aikin. Ginshiƙin koyarwa ba tattaunawa ba ce tsakanin malam da ya makaranta ba kawai ne, akwai ayukkan rukuni na gaba ɗaya da malam ya aiwatarwa, hulɗa tsakanin yan makaranta. . (Altet, 1997, p.19)

Wajen girka ilimin almara, malamin makaranta yana gayyatar yan makaranta ta hanyar tattaunawa da ma'amala a tsakaninsu. Yana kasancewa wani jagora ne mai sasantawa na yan makaranta a wajen koyon.

A Afirika ta yamma, maroƙa suna koyar da yara matasa kiɗe-kiɗe da kuma jinsunan baka na almara. Cikin wannan tsari, an gano da cewa yaron maroƙi ya samu horo gida biyu. Na farko yana samun horo daga ma'aifansa da suka haɗa da tarbiyarsa. Na biyu ya samu horo na sana'a ko aiki na tsawon lokaci mai yawa cikin wata al'ada ta gado. Sai abubuwan masu

mahimmancin cikin wannan horo sune, shekaru na fara koyo, kariya, ƙwarewa ta harshe. Kamar yadda ake koyar da shi a kewayen *Dudal*koyarwar jawabin almara ya ƙunshi sassa, sharuɗɗa da fusa'o'i Nazari tsarin tafiyar da koyarwa ya zo da mahimmn dubaru ukku : bada labarin almara ; bayani dalla-dalla da maimaita. Bayan fusa'o'in koyarwa, maroƙi yana amfani wasu tabi'u da suka danganta da aikin kamar su bada ragama, mahimmancin aiki da mizantawa ta ƙoƙari da kammala ko ta ƙarshe.

A wani mataki ko, babi nan yana nuna da cewa, jawabin almara yana koyiwa a makarantar gaba da sakandire saboda ayukkanshi. Ana yin amafani da fusa'o'i biyu wajen koyar da jawabin almara, na ɗaya ya shafi harshe na magana, na biyu kuma al'ada. Cikin fusa'a ta farko, ana koya shi kamar ɓangarori na matani ta hanyar wallafawa da fasaltawar ɓangarori na koyarwa a kowane iri na almarar. Ana gudanar da ɓangaren aikin a cikin zaman ayukka dayawa da gurirrikansu, da abubuwan da suka ƙunsa da dubaru. Fusa'ar ta biyu, ta'aladu ta dogara da gabatarwar halaye na ɗa'a, na mutunci da zamantakewar al'umma cikin koyarwa-koyon Idan ana koyarwa da su, jawabai na almara yana bayyana hanyar koyi da wani mutun daga yaran da za su laƙanci halin(Van Zanten & Rayou, 2017, p.857).

**Shawarwari da kuma wasu ayukkan na zahiri zuwa ga malaman makaranata da malaman bada horo bisan koyar da jawabin almara**

Ana son malamai su yi larwan sani na yan makaranta bisan almara ta Afirika ta yamma, kuma su fahintar da su tsarin koyar da almarar a makarantar gargajiya da kuma yadda ake ganin za a iya gudanar da koyon a cikin makarantu na zamani. Ana iya binciken sanin da aka laƙanta ta hanyar ayukka na ilimi ko na zahiri.

**Aikin na 1 : Binciken sani na galibi na yan makarantar bisan jawabin almara**

1. Bada ma'anar jawabin almara ;
2. Bada wasu alamomi na bambance-bambance na jinsi almarar Afirika ta yamma ;
3. Tattance wuri da kuma bada bayani dalla-dalla na ayukkan dabam-dabam na almara cikin al'ummomin gargajiya na Afirikan ta yamma.

**Aiki na 2 : Gano tsarin koyarwa na jawabin almara a makarantar maroƙa**

1. Bada ayukka na share-fage, sharuɗɗa da sassa na koyar da jawabin almara a makaranta maroƙa.
2. Waɗanne fusa'o'i ne ake aiki da su a fanni makarantar gargajiya ?

**Aiki na 3 : Samar da wasu hanyoyin koyarwa-koyona jawabin almara a makarantar zamani**

1. Don mi, ya kyautu a koyar da jawabin almarar Afirika ta yamma a cikin makarantu na boko ?
2. Bada hanyoyi na koyarwa da ake iya amfani da su wajen koyar da jawabin almara a makarantar gaba sakandire.
3. Nazarin ɓangare aiki na zubin labarin mai dogara da matani na almara ta hanyar tattance zaman ayukka, gurirrikansu da abubuwan da suka ƙunsa

**Madogarai na littattafai da aka yi amfani da su a cikin wannan binciken**


Adam, J-M. (1999). *La linguistique textuelle*. Paris : Nathan.

Altet, M. (1997). *Les Pédagogies de l'apprentissage*. Paris : Presses Universitaires de France.

Barthes, R. (1973). *Le plaisir du texte*. Paris : Éditions du Seuil, collection Tel Quel.

Biebuyck, B. (2004). Bardes et épopées héroïques : un aperçu pour la République démocratique du Congo. *Griot rêvé et griot réel*, *Africultures*, (n°61), 109-120.

Bornand, S. (2005). *Le discours du griot généalogiste chez les Zarma du Niger*. Paris : Éditions Karthala.

Camara, S. (1996). La tradition orale en question. *Cahiers d'études africaines*, *36*(n°144), 763-790. https://doi.org/10.3406/cea

Chevrier, J. (2005). *L'arbre à palabre, essai sur les contes et récits traditionnels d'Afrique noire.* Paris : Hatier International.

Dérive, J. (2012). *L'art du verbe dans l'oralité africaine*. Paris : L'Harmattan.

Diouf, A., Mbaye M. & Nachtman, Y. (2001). L'éducation non formelle au Sénégal. Description, évaluation et perspectives. [En ligne]. Repéré à: http://unesdoc.unesco.org/images/0012/001238/123892f.pdf

Dolz, J. & Schneuwly, B. (1998). *Pour un enseignement de l'oral*, Issy-les-Moulineaux : ESF éditeur.

Enkerli, A. (2004). Yoro Sidibé, griot des chasseurs du Mali. *Griot rêvé, griot réel, Africultures*(n°61), 37-47.

Fobah Eblin, P. (2006). *Poétique et approche stylistique de la poésie africaine : étude à partir de quatre œuvres de l'Afrique de l'ouest francophone*. Thèse de doctorat, tome 2, Université Paris IV- Sorbonne.

Garba**,** Y.(2011). *L'épopée au Niger à travers quelques récits des Nyamkala Djéliba Badjé et Djado Sékou*. Mémoire de DEA, Université de Ouagadougou.

Hale, T. (1998). *Griots and Griottes of West-Africa*. Bloomington: Indiana University Press.

Kesteloot, L. & Dieng, B. (2009). *Les épopées d'Afrique noire*. Paris : Éditions Karthala et Unesco.

Mercier, A., Luisa Schubauer-Leoni, M.& Sensevy G. (2002). Vers une didactique comparée. *Revue française de pédagogie*, *141*, 5-16. doi :10.3406/rfp.2002.2910.

Ogandaga, G. (2007). Le respect de l'âge comme caractéristique du management des hommes: existe-t-il un modèle africain de GRH*? Lille Economie et Management (LEM)*. CNRS. [En ligne]. Repéré àhttp://lem.cnrs.fr/Portals/2/actus/DP_200722.pdf

Ourghanlian, P. (2006). Enseigner, transmettre, construire, les théories de l'apprentissage : enseigner / apprendre. [En ligne]. Repéré à http:// www.pearltrees.com.99176290-apprentissage-ourghanlian.

Saïbou Adamou, A. & Hamidou, I. (2008). *Le français au Niger, l'enseigner, l'apprendre*, Niamey : MEN-SOUTEBA.

Saibou Adamou, A. & Issoufou, A. M. (2020). L'hyperbole dans le discours épique de Djado Sékou : ornement discursif et mémorial identitaire. *Akofena Revue scientifique des sciences du langage, lettres, langues et communication*/ (n°4), 129-146.
Seydou, C. (2008). Genres littéraires de l'oralité : identification et classification.*Littératures orales africaines*, *perspectives théoriques et méthodologiques*. Paris : Karthala, 125-175.
Van Zanten, A. &Rayou, P. (2017). *Dictionnaire de l'éducation*, 2ème édition. Paris : PUF.

Vettorato, C. (2017). Les éléments épiques africains et la quête d'une épopée moderne : l'exemple du Blue Fasade Nathaniel Mackey.*Le Recueil Ouvert*. [En ligne].Repéré à : http://ouvroir-litt-arts.univ-grenoble-alpes.fr/revues/projet-epopee/267-les-elements-epiques-africains-et-la-quete-d-une-epopee-moderne-l-exemple-du-blue-fasa-de-nathaniel-mackey.

**Babi na 6**

**Ali Rufai**

# Darajar horo da ilimi na garagjiya a Afirika wajen makarantar boko a ƙarni na ashirin da ɗaya (ƙarni na 21)


## Taƙatawa

*Mabuɗin farfaɗowar ci-gaban ɗan adam, arziki, al'ummada al'adu, horo da ilimi a yau sun zama fanni mai cikakken canje-canje a Afirika. Suna da dalilin tattaunawa dayawa da tunani a tsakanin mahakunta, al'ummomin farar hula masu horarwa da malamai su da kansu da malaƙantan sani dabam dabam, a wurare dabam dabam. Ta ƙaƙa ne za a canja ta hanya mai daɗewa horoda ilimi da suke zama a hankali maras gwanincewa wannan ita ce ayar tambaya ta masamman da waɗansu suke yi wa kansu. Wannan takardar taimakon neman ansoshin wannan tambayar. An rubuta shi ne ta hanyar tushoshi, sanin rubuce-rubucen marubutan Afirika da baƙin nafiyar bisa harkokin horo da ilimi na gargajiya da na zamani, tattaunawa da jagorori, da shahararru da ma'aikata da namu sani na kanmu ta fannin. Husa'armu tana kwatantuwa. Bincike-bincike kan tushoshi, saɓawa da tattara labaru dabam dabam suna nuna akwai cikin horo da ilimi na gargajiya wasu mahimman tabi'u waɗanda za su iya taimakawa wajen kyautata makaranta ta zamani. Akwai dangantaka a tsakanin fannonin biyu na horo da ilimi, har da yanayin sauyi na gargajiya na ƙasashe da na makamantai. Malaman horo na makarantar horon malamai (ENI da faransanci) da tsangayar horo da ilimi kan yaƙi -da – jahilci (IFAENF da faransanci) da na malamai na sassa dabam dabam na horo da ilimi na masamman na paramari, na sakandare, ana iya buga ƙirji da su, na farin bisa koyar da darussa, na biyun ko bisa ayyukan cikin aji.*


***Mahimmankalmomi :*** *horo da ilimi na gargajiya ; horo da ilimi na zamani ; tsarin tafiayar da horo da ilimi, tabi'u nagari/mahimmanci/darajai*

## Gabatarwa

Bayan hutowa cikin duniya, ya yi sauran horo da ilimi abunda akan faɗa. Amma, to, mene ake kira horo da ilimi ? Yawanci fasarar Kalmar horo da ilimi suna da wuyar bada cikakkar fasarar. Amma, duk da wannan wuyar da yawan fasarar, ana iya ce wa dukansu suna nufin «rabawar sani». Daga wannan sanin ne da kowane ɗan makaranta za a iya koyar, za a kasance iya yi da iya kasancewa. Ta bakin Baba Musa, AR, Malam Musa, L § Rakotozafy,J-(2014,Shafi na 29). «Horo da ilimi » su ne tushen aikin bumƙasa tarin sani da darajar jiki, ɗa'a, ƙwaƙƙwaluwa, dangance da jiran halin zamantakewa da al'adu da aka mallaka». Nesa daga cikakkar halarta ta wajen rayuwar ruƙuninsa da yake mallaƙe, (horo da ilimi al'umma), horo da ilimi suna sanya mutum ya samu ƙoƙarin yin shara'a (shi da kansa da sauran), daga ƙarkashin darajoji na duniya (horo da ilimi na ƙabila).

Cikin yawancin ƙasashen Afirika, tsarin horo da ilimi ya ƙumshi kala biyu da kowanne ya shafi iren al'umma. Wani bi horo da ilimi na iyali da yake fuskantar mutum ta yanayin kuzari cikin al'ummar gargajiya daga wancen gefen, makarantar da ake kira ta zamani da turawan mulkin mallaka suka kawo ta mai manufar haƙiƙa ta hori ma'aikatan biro. Yaron Afirika da aka sanya shi makarantar zamani ya kasance a cikin wani hali na al'adu masu rigima a cakule da gargajiya da zamani. Wadda ba shi da rashi saratsi cikin tafiyar da horo da ilimi a kan rayuwa cikin al'umma.

Waɗannan salon biyu na horo da ilimi ba su saɓawa junansu; ba su hamayyar junansu duk da hamayyar da suke fuskanta, amma suna taimakar junansu. A taƙaice dai, horo da ilimi suna

farawa daga cikin gida kuma suna ci gaba zuwa ga al’umma. Shi ne,kamar yadda Abdul Mumuni Diyofo (2019) ta horo da ilimi masu kamanni dayawa da suka shafi huskoki da dama na mutuncin yaroko na matashin. Tana dangantuwa a taƙaice da bunƙasa hazaƙar jiki,da horon hali, da manyan darajojin ƙwaƙƙwaluwa da sanyawar sani na kai na fusaha kamar na sanin ayyuka, da yin ayyukan hannu kamar aikin ƙwaƙƙwaluwa da na zuciya.Tana kwatanta yaron, wani babban mutum mai tasowa, horon mutum, horo bisa al’adu da wanda ba na al’adu ba,horo kan ɗa’a, horo bisa darajar aiki, bisa girmama yannai, tsoffi da yan uwa, da na ainahi… Duka waɗannan horo dabam dabam an ba yaro su tun yana ƙanƙane kuma an yi su aji-aji dangance da shekara da iyawa ta jiki da ta ƙwaƙƙwaluwar yaron.Ta ɗora gindin da abun da ya kamata ya koya a makarantar zamani, ta shiryashi kuma ta ƙara mashi sani don ya zama cikakke.
Mene ne horo- da- ilimi na gargajiya ? Kulum tana da armashi a wajen makarantar yanzu, ta ganin halinta da mutane suke tsammani na dauri ne ? Ta wani hali ne za ta iya kawo agajinta cikakke cikin sauƙi na cimma gurin makarantar ƙarni na ashirin da ɗaya (21) ?

Wannan nazarin yana da hangen musamman na darasi. Da neman tsara dangantakar harshe tsakanin horo da ilimi na gargajiya da makarantar yanzu da take fuskantar matsloli da dama, ta shirin ba malamai da masu horonsu shawarar, ma’abuta na masamman na tsarin horo da ilimi, Mashinoni dan ganin kyautata ayyukan koyar da darussa na waɗansu, na hanyar koyo da koyarwa na sauran. Wannan dubarar da gaske ma, za a bar halaye masu kyau bisa tabi’u na gari ga yan makaranta, cikin duka fannonin koyo da koyarwa.

Cikin wannan babin, za mu tattauna kan mahimman fannonin tambayar waɗannan:1) tsarin koyo da koyarwa na gargajiya, da ganin hali na yanzu da karance-karance da ake da akwai bisa tambayar, ii), hujjojinsahalayensa ; iii) kamarsa iv ; darajarsa ta horo da ilimi ; v) tsare-tsaren horo da ilimi na zamani da vi) nanacin horo da ilimi na gargajiya na makarantar yanzu.

## 1. horo da ilimi na gargajiya a Afirika

Cikin duka kampanonin al’umma kuma masamman ma cikin Afirika, horo da ilimi gargajiya sun gaje wuri wadatacce na yaro. Da tsufanta kamar tsufan duniya,wannan horo da ilimi suna zama kuma su kasance abun kwaikwayo na al’umma.

### 1.1 Horo da ilimi na gargajiya, mene ne ma’ana ?

Matsala ta farko da ake fuskanta idan ana so a yi zancen horo da ilimi na gargajiya, ita ce babban ɗaurin kai wanda tushen ya ƙumsa. Waɗannan gewayayyeniyar ba su da cikakken *haske, abun da za a ɓatar da mai karatun. Saboda haka ne ma, ya dace a tambaye shi don a fasarce. Jorje s Snyders cikin wani littafinsa tsarin koyo da koyarwa mai ci gaba, horo da ilimi na zamani ya yi niyyar kawo wani haske na kirkirowa ta wannan manufa.Kalmar horo da ilimi na gargajiya, daga gare shi, yana nuna tare «wata hanyar horo da ilimi war kuma mafi yawa, jama’in maras ƙa’ida na abun da yake nan a yanzu, game da tsekoda kuskuren game da ƙaranci na gurin…» (Snyders, 1975,Shafi na 15).*
*Mu ɗan kwatanta auna wannan ra’ayin na Snyders. Manufa ta farkowani yanayin siffar horo da ilimi , ya shafi rubutun turawa na yamma kan harkokin horo da ilimi , kamar su Alain, da yake da son gaske* Emile-Auguste Chartier, Emile Durkheim, Jean-Yves Château ....
*A taƙaice, ta bakin waɗannan shahararrun marubutan, tushen horo da ilimi na gargajiya shi gurin kai yaro ko ɗan makarantar tagama shi da mayan ababben da ɗan Adam ya wallafa»(Snyders,1975, shafi na 15). Waɗannan ɗin suna da dammar aikata wa wajensa kamar misalin da aka nufata a jagora kuma a mayar da shi na farin cikin girmama mutuncinsa na kansa. Halin na biyu na kalmar makarantar gargajiya a wajen Snyders, ya kai shi ga*

*makarantar yanzu da duka nauyin da ta rataya na dabam dabam masu daɗewa, da yadda ya kamata a gyara.*

*Wajen Marcel Inne (1988, shafi na199), horo da ilimi na gargajiya an gina shi bisa laƙa wa matasa huzaƙar na gabaninsu». An gane wannan tsarin horon daga ire-iren tabi'o'i koyon wasu ayyukan hannu da take da daraja ƙwarai na al'ajabin tabi'o'in mutum, hali da iya zama cikin jama'a.* Halayen ne da al'ummomi matasa suka gudanar bisa kan waɗanda ba su taso ba har yanzu. Horo da ilimi na gargajiya yana da hali irin na kowa da kowa, na al'umma kuma yana aiki da iyawa da hawa na ganewa, na sani kuma da na ƙarfin ƙundu, na jikinyaro. Shi ne kafin a yi komai a ba yaro wani horo, horo da ya danganta da daraja kuma da za a ceci duk wata ɗaukakaka ƙara ko yin amfani da kada daraja.Ta shafi duka al'ummomi. A taƙaice, irin wannan salon horo da ilimi yana horar da matasa bisa kan ayyukan da za su ba su wurin da ya kamace su wajen tsarin amfanin al'umma. Koyo da koyarwa da yake goyon bayan horo da ilimi na gargajiya ba shi da tabtat, cewar ba a kawar da shi ba cikin azuzuwan tabtat.Yana yiwuwa ko'ina, in dai da hali ko samun dammar yin shi: Cikin fadamomi, wuraren kiyo ko kuma wuraren al'ummomi, watarana nesa ma da gida… Ya kasance na baki ko na aikatawa ne. Cikin ƙashen da suka musulunta kama Nijar, musulinci ya kawo rubutu. Horo da ilimi na gargajiya su samu ƙarfin cika aiki dangance da hulɗarsu da rayuwa. Kamar yadda Pare kabore Afsata shi da Nabalum- Bakyono Rasmat suka bayyana. (2014, shafi na 59), «*Zagayowar rayuwa cikin Afirika yana farawa tun farkon ƙirƙirar yaro (ko kuma kafin nan) har zuwa mutuwarsa. Kowane lokaci yana shirya na kusansa, da kamannun haka kenan suna liƙe da junansu daga waɗansu zuwa wasu ».*Horo da ilimi suna bin hanya ɗaya. Zaɓen matar ko mijin da za a aura a gaba, a misalince, yana cikin wannan ra'ayin zamantakewar al'adun Afirika. Haka zalika ma ana kulawa da taimakawa kan fannin lafiya tare da tattalin mace mai juna biyu, kuma da yaronta da za ya girmaa gabanta tare dayin hatarar iyalin kusa da na nesa gaba ɗaya kuma da al'ummomi ga baki ɗaya. Duka wannan taron dangin yana hararar yadda rayuwa da horo da ilimi r yaron za su kasance.Wannan horo da ilimi r suna ɗauke da sassa dayawa. Kamar yadda jagoran da suke tafiyar da su suke, su ma suna kama junansu daga waɗancan zuwa waɗanga. A taƙaice dai, horo da ilimi na gargajiya suna nesa da su zama na ƙwaraiduk da sakamakon masu ƙayatarwa da suke sanya wa a samu, kamar yadda Abdu Mumuni Diyoffo ya gano (1988ʃhafi na 201-202: *« wannan irin horo da ilimi ba su ba ko mayan ma'aikata, ko madogarar na masu ci gaba da ya shuɗetare da sanya kuma da halin abun da ya shafi hakan aji-aji na samun sabon cikakken horoda sani,suna da niyar ba kansu ɗaya bayan ɗaya, nesa da nesa ».*Horo da ilimi nagargajiya sun zarge kansu da su maimaita junansu kuma da su zauna, sabodayunƙurin al'ummomi.Ko da canjin siyasa mai mahimmanci da sukan jawo tashe-tashen hankulan al'ummomi. Cikin wani ƙudiri mai suna *horo da ilimi a Afirika da darajojinsu mihimmaiA S Mungalá1982) yana tabbatar da cewa horo da ilimi suna dogara ga al'adun masamman ma na Afirika kuma take isar daga yayi zuwa wani yayi cikin al'ummominmu, tun daga Afirika ta gabanin mulkin mallaka har zuwa yau***.** *Kuma***,** *horo da ilimi na gargajiya suna zaman tare a yau da horo da ilimi da ake cewa «na zamani »? Ba su laƙama tsayi ko kaɗan na lokaci zuwa lokaci kuma ba su dangane da ma'ana sunan da aka saba faɗa masu. Kuma ba ita ba ne horo da ilimi da suka ja da baya, tsofo ko wanda zamaninsa ya huce.Horo da ilimi na gargajiya horo ne da yake ɗauke da al'adun mahallin, da cewa al'adunsa da halayen abubuwan al'umma: halin da yake ganin duniya, ya wunƙura, ya ci, ya sha, ya tufatar, ds. Tana yi ta hanyar magana tare da rakiyar dube - dube da kwaikwayo, rawa, kaɗe - kaɗe, ƙirƙire -ƙirƙire, wasa, ds.*

1.2. Shin ya kamata a cin gaba da kawo batu horo da ilimi na gargajiya a hali na yau ?

*Ta hanyar wannan tambayar, muna so mu sani a yau in da akwai horo da ilimi na ainahin Afirika. In haka ne, tana tsarkake ta ? Ta waɗansu tsare-tsare, wannan horo da ilimin ba za su sauya ba ko an fitar masu da mafarinsu.*

*Da ganin ta wata sukuwar tarifi,Afirika ba tataɓa rayuwa ba cikin matsatsidon ta tilasa yin tattalin wata tsaptar ayyukanta gadonta na arzikin wajen horo da ilimi har ma na cikin sauran sassan rayuwa.Tun a ƙarni na bakwai (7) nafiyar ta shiga cikin hulɗa tare da musulunci da ta yin amfani da wannan damar yaɗa wannan addinin cikn duniya. Daga yankin ƙasar Larabawa, addinin islamiya ba ya samun matsaloli ba wajen kaiwa ƙasar Jidda, kuma yankin Arewa da Afirika ta yamma. Addini mafi ƙarfi a Afirika shi ne "wanda yake kowace halitta ta duniya suna,wani tsarin addini da yin aiki da ya ba nafiyar wayewar kai wajen ayyuka da zamantakewar al'ummomi.Cikin wannan cuɗuwar dagantaka mai ɗaurin kai ce islamiya ta girku sosai. Ta hakaɗin, Vincent Monteil yake yin shayin amincewar wannan zaman tamkar « kutsuwa sosai, idan har musulunci ba ya maidowannan tambaya addinin islamiya na gargajiya » (Monteil, 1964, shafi na65). Harkar addini tana nan har yanzu. Amma duk da wannan jan dagar, Afirika musulma, da so ko da ƙi, da hankali ko da hauka, a buɗe take kuma ta arzita da sabin darajoji na musumlunci mana. Akwai wani horo da ilimi na musumlunci dangance da darajojin islamiya, kuma dayake neman hanyar ta daidai muhallin.Bayan islamiya, mulkin mallaka na Turai, yana daga wajensa; sanya sabin darajoji dangance da koyo da koyarwa na ma'aikan matsirin duniya kuma da rungumar addinin kirista daga al'ummomi dayawa na Afirika.Yau, bisa wannan nafiyar, Islam da Kirista, waɗanda su ne addinai sannanu da yawancin al'ummomin Afirika suka fi runguma da aikata wa, kuma da suke yin faɗi-a-ji cikin mutane dangance da horo da ilimi. Ana iya yin batun horo da ilimi na islam, horo da ilimina kirista da kuma horo da ilimi na dauri/ fil'azal na Afirika ko na gargajiya.Kowane ɗaya daga cikin waɗannan ƙa'idodin horo da ilimisuna gina gaskiya dabam, kuma abun da ake gani a yau, ko'ina bisa nafiyar, wani siffar …., da horoda ilimi …… Ayyukan horo da ilimi suna kira bisa darajīojin Afirika da baƙi. A wannan halin, ba za a iya zancen horo da ilimi na dauri cikin Afirika, har idan dai wagga ta arzinta da dangantakar waɗansu darajoji,na yamma da na musulman larabawa a taƙaice.Duk da zaton da ake yi lokaci zuwa lokaci da ya fito daga alaƙar islam da kirista tare da bunƙatar da ba a kara ta da makarantar mulkin mallaka ko ta zamani, horo da ilimi r Afirika ta galgajiya ya sake rayuwa na haƙiƙa kuma ya shiga har zuwa zamaninmu.*

2. ***Tushoshi da halayen horo da ilimi na gargajiya***

Tushoshinhoro da ilimia Afirika ta gargajiya bisa kan koyo da koyawar da darajoji. Daraja ɗaya, cewar Munga (1982) na dogare da duk abun aka yi na jama'a ko na al'ada da yake da alaƙa ta gaskiya, ta halin ɗan Adam kuma da yake ansa wa daidai da buƙatun na ainahi na yawan mambobin al'ummar mutane . Su ne wakilan na ainahi da suke goya wa halayen al'ummomi baya tare da nuna abun ƙwarai da na banza.Darajojin ba su da siffaguda, ba su danganu ba amma masu ƙwazo ne. Su ne suke sanya mutum ya rayu daidai na haɗin kai da shi sosai ko da sauran. Irin darajojin kashi biyu ne : darajoji na wuce-lokaci da darajoji na fatara. Dangance da darajojin wuce –lokaci ko abun samu na tarihi, su ne galabar haɗaɗɗa na hazaƙar al'adu dabam dabam na shekaru ɗaya da suke biye da junansu da zagayowar tarihi. Ba su gushe wa kuma na game da mutm. Su kuma darajojin fatara, su ne waɗanda ba haɗa ba da hazaƙar tarihi; su na laƙe ga abubuwan kai-tsaye kuma ababensu ba ya huce halinsu ba ko ba su sauya halinsu na kewaye al'umma ba, na lokaci zuwa lokaci na al'ada don ganin wannandarajar ɓadda dukan wa'adinsu, dukan ma 'anarsu (Munga, 1982).

Horo da ilim na gargajiya yana da halaye na kansa. Daga bakin Abdu Mumuni (2019) shi da Mungala (1982), na jama'a kai ne suke, da yake ba na wakilcin iyalin kaɗai ba ne, amma ba na zuri'a kaɗai ba ne da gari, da na ƙabila. Ai cikin ruƙunin al'umma ne yaro yake koyo, daga dogararsa kan darasinjama'a. horo da ilimi na gargajiyayana da halayensa na kansa da ake gani a dangane da kan tsarin tafiyar da abun da ya rayu;ta aiki domin ta tafiya bisa sani mai amfania game da rayuwar yau-da- kullum dabaka, dangance da sawar na kaitsaye sani , daga rishinduk wani rubutu. Ta kasance tahe take da tana ci gaba, saboda zoke daga mafi wuya zuwa mai wuya cikin jeri, cewa babu wani rami balantana katsawa tsakanin sassan iri-iri na ci-gaban yaro, tsakanin iyali, zuri'a da al'umma, tsakanin nazaridaaikatawa, mamaki, don tana yin kira ga siran da addini, kuma har- wa- yau ɗauke da abu iri-iri da kama- ɗaya, na halayen horo da ilimi da ya shafi jama'a. Kuma horo da ilimi na gargajiya cikakke ne da kuma ayyukan dabam dabam domintsinkayar horo gaba- ɗaya na ɗan Adam daga ƙarshe sanyayya, domin ƙarshensa inganta haɗin kai da kuma sani na juna tsakanin ɗan Adam da jama'a.

### 3. Tsarin horo da ilimi na gargajiya

**Horo da ilimi** na gargajiya a Afirika yana da aiki bisa kan cikakken horon yaro don ya sa shi ya zama mutum cikekke a matsayin nufin kalmar. Saboda haka ne ma, ba ya keɓe fuskar rayuwa ko ɗaya, ba wani sashen ɗan Adam.

Iyali da yake shi ƙaramin sashe ne na al'umma yana da mahimmancin rayuwa cikin harkokin ci-gaban mutum a matsayin mambobina al'ummar.Tunda an san mutunci, hali, yadda mutum yake zama cikin al'umma darajojin kowane mutum daga iyali suke fita da fari, kuma zuri'a daga ƙarshe na al'umma? Uwaye suna da hankali mai haske na muƙaminsu ba kaɗai ba dangance da yaransu ba, amma har ma da na al'umma a taƙaice da suke matsayin mamba.Horar da yaronsa, horar da shi kawai, aiki ne, tambaya ce ta mutuncida soyayyya mai kyau.

Cikin iyali, matsayin farko ilimi r da yaro yana rataye da fari ga uwa.Wagga tana da matsayi wadatacce cikin shekaru shida zuwa bakwai har ma takwas na farin rayuwar yaro.Ita ce take ɗauke da nauyin nuna masa takin ƙafarsa na farko cikin rayuwa. Bayan matsayinta ta mai tattali, ita ce kuma take kula da kiwon lafiyar yaron da kuma wayewar kansa. Uwa ita ce har wa yau ta farkon malamar harshensa saboda kusa da ita ce yaron za ya koyi faɗar kalmomi na farko; ita ce komai nasa; ita ce tsakiyar sararin duniyarsa.Dalilin wannan shaidar ce ma Abdu Mumuni Diyoffo ya rubuta wannan (2019, shafi na 10)«duk waɗanda suka lura da uwa ta Afirika sun yi laka'ari so duba, ƙananan abubuwan dubu masu nuna tattalin da take kewaye na yaronta....».

Banyan wannan kashin na farko ilimi r da saya yaronta cikin jama'a, ilimi yana ɗaukan yaunin jinsi, cewar, dangance da jinsinsa, yaro yana tsudumuwa cikin sabon yanayi na ilimi rsa a zaune kusa da uwarsa idan ya shafi yarinya shi ko kusa da babansa idon namiji ne. Nan suna da alaƙa ta kai-tsaye da ayyukan wannan ko waccen. Daga bakin nan ne ƙididdiga ta farko tsakanin ilimi da sani da horo ta ɓullo. Aro yana kambacin babansa ko uwarsaga ayyukansa cikin gida da na yau- da- kullum na wani zamani ma. Uba yana koya ma yaro aikinsa na namiji lokacin da uwa ita ko take koya wa yarinya matsayi da duk abun da ya shafi matsayinta namace.Wannan ba ya shahi ba ko kaɗan aikin yara da doka ta haramta saboda ba su fuskanci yancin yaro ba. Horo ne dai na sanya shi cikin al'umma da arziki; guri na ainahi shi na ƙirƙira wa yaro manufar aiki, da mutunci kuma da na gabata.

Bayan iyalin yaro, ana iya ganewa da duk al'umma ma tana taimakawa har-wa-yau wajen horo-da- ilimi rsa. Wannan bayan takin shirye-shirye na farko da uwar masamman ma take kulawa da shi. Yannaiduka kamar magabata suna magantawa don bayar da ra'ayinsu na kowa ko na jama'a saboda su kawo nasu ƙoƙari cikin horo da ilimi na yaro wanda za ya zama a gabannan harkokin kowakamaryadda Abdu Mumuni (20,19): ya bambantaaji biyu a daidai wannan takin ƙarshen:« ajin ƙungiyoyi »da ajin koyo. Waɗannan lokutta ne na wajen cikon horo dailimi cikin tafiyar aikin koyarwada horo da ilimi na gargajiya.« Ajin ƙungiyoyi »da ajin koyo. Waɗannan suna a matsayin sashe daga gare shi ne yaro yake da hazaƙar da za a yi amfani da shi wajen gudanar da ayyuka ire-ire na wuce gona da iri: Ana iya aika shi don ya faɗi saƙonni ga wani mutum da ake gaya masako ya kawo ansar da ta dace, a kai samunsa wani abu ko ya kawo shi, etc. Shi ko lokacin koyo shi ne na haɗa ayoyin jarabawa ƙwaƙƙwaluwa da na jiki da suka shirya sosai ma cikin sahun samari. Ana gudanar da koyon kullum a ƙarƙashin jagorancin mutanen da al'umma ta walkilta kuma da suka fito daga cikinta saboda wannan aikin. Cikin farin ciki komai yana tafiya daidai cikin haɗin kai da bunƙasar yaron kamar yada Abdu Diyoffo ya kwatanta (2019ʃhafi na 12): «*duk tsawon bunƙasar jikinsa da ci-gaban ƙwaƙƙwaluwarsa da saninsa, yaron, kuma matashi, yana biye daga al'ummar gaba-ɗaya, daga kai-tsaye ko ta shingiɗe».* Na horoda ilimi na Afirika ta gargajiya, «*makaranta darayuwa abu ɗaya ne*» (Mungala, 1982 shafi na 10). Dangance da halaye na halaliyarsa, ta hanyardatatta abakin ƙarshe da yanayin tattalin arziki, da na siyasa da na al'umma ya tilasta masa, horo da ilimi na Afirika ta gargajiya ya ƙarfafa a hori mazaje,cikin manufa mai yawa kuma mafi cikakkar kalma.

Cikin tsarin gargajiya na horo da limi a Afirika, madogaran koyo da koyarwa da yawa suke, da ƙauracewar rubutu. Horo kan sanina yaro da na samari, ya keɓe wurin daga na naƙaltar harshe ta hanyar madogarai kamar su gatannoni, tarihi, alma'arori, zanteku, wasanni, tsaro, wasanni kwaikwayo (Abdu MumuniDiyoff, 2019, Unesko, 2016, Mungula, 1982, Caille, 2005). Wane matsayi ne wannan horo da ilimi na gargajiya ya kai?

#### 4. Darajar ilimin horo da ilimi na gargajiya

Duk da wannan kasawar (rashin rubutu, rashin kimtsin mai ƙa'ida na koyo kamar makarantu da azuzuwa, rashin jaddawalai, ds), horo da ilimi na Afirika ta gargajiya yana da darajoji na gaske.Ya kasance na wani iri kamar horo da ilimi r da ma'aikaci mai haɗa nazarori da aikatau, wanda ya ba shi wani hali aikatacce da mai amfani. Tana riƙe har yau ta danganta da ci-gaba na ƙwaƙƙwaluwa da na jikin yaro, har da jinsi, kowa tare da halaye na kansa, da buƙatunsa da matsalarsa. Kowane yaron da za a ba horo da ilimi yana cin ribar koyo da koyarwa na malamai dayawa (iyali, al'umma), inda yake da babban fannin tafiyar da koyo da koyarwa.Wannan horo da ilimi an yi shi ta da kyau ga buƙatun zamantakewa da arzikin al'umma abun da ya maida ta bisa tsarin kashe kuɗi, horo da ilimi ne take halin kuɗi kaɗan ko ma babu shi, arzinki na mutane yana shiga ciki ta yin shi ta aiki na wajensu su kansu da na zaman jama'a da za su fitar da cin ribarsakenan ana iya gwada ta. Koyo da koyarwa suna sanya yaro cikin halaye, ba su ruhe ilimi a cikin aji ba. Bada horo da ilimi Afirika na gargajiya yana gudana kuma cikin:

- Tafarkin dimokaraɗiya, duk yara suna iya shiga ciki; tana da ma'ana tunda tana shirya mutum ya nemo gurinsa a cikin jama'a;
- Halaye na zamantewar al'umma saboda, a lokacin bada horo da ilimi na mutum yana da albarka;
- Hali na ƙirƙira da basira saboda daga na nan ne mutum yake ƙirƙira rayuwarsa ;

- Al'umma, saboda al'ummar ce za ta ɗaukar nauyin tarbiyar (iyali, jama'a, kullum tana nan saboda tana daɗewa tsawon rayuwarta, ba ta san da wani hargitsi makaranta ba.

Ire-irenwaɗanan tabi'u ne suka bambanta ta da tsare-tsaren horo da ilimi na zamani.

**5. Tsare-tsaren bada horo da ilimi na zamani**

Waye garin samun yancin kai na Afirika, sabin yankunan ƙasashe masu cin gashin kansu sun ɗaukawa kansu abin da ake faɗi yanzu a zamaninmu «tsarin horo-da ilimi ».Kowace ƙasa tana da nata tsari da yake canzawa dangance da gadon ƙasar mulkin mallaka da ta bari. Kenan Afirika ta ƙumshi tsare-rtsare dayawa na horo da ilimi na mallaka da aka san na farkon su ne tsarin turawan Faransa, tsarin Ingilishi da na tsarin Portuganci. Kowanne daga cikin waɗannan tsare-tsaren yana tarayya da tsarin horo da ilimi na gargajiya. Ta faɗar Tijani Amadu (2021), tsare-tsaren horo da ilimi na zamani da suka shahi mallaka suna da wasu ƙarshe kamar haka: tattalin ci-gaban mutum ta hanyar haɓakawar jikin mutum, sani da na ɗa'a; ƙarfafa halin koyoda kampani; haɓaka halin ɗanƙasanci ta hanyar son ƙasa; ƙirƙira wani halin ɗanƙasanci magabaci, ma'anar demokaraɗiya; haɗa kan yan ƙasa; bunƙasa wa mutum halin ɗan uwanci, son ƙasa, jagoranci, riƙon amana, halin darajoji na duniya kap da halin ƙarfin ƙundu na kowa saboda a sanya kowane ɗan makaranta ya iya kawo nasa ƙarhi, da hazaƙarsa, ga ci-gaban ƙasarsa; sanya wa kowa a kansa halin yin haƙuri da juna da zaman lahiya kuma da girmama wani, masamman ma yin gaskiya a tsakanin jinsina da shara'ar al'umma; haɓakar daraja iri-iri, yawaitarda harshuna, na addini da na al'adu daga ƙarshe a tabbatar da horo saboda mutumen ya nuna ɗa'a, ladabi da biyayya daga ƙarshe mutumen ya tabbatar da ƙwazo kan aiki kuma ya kasance mai amfanin kansa ne, kuma ya amfani jama'arsa. A Nijar kamar a cikin sauran ƙasashen Afirika, duka waɗannan ƙasashen sun ƙayyadu ne daga tsarin mulki, dokoki da ƙudurori, ds.

Dangance da saɓanin horo da ilimi na gargajiya, cikin tsare-tsaren horo da ilimi na yanzu, horo da ilimi yana gudanuwa cikin wani zagayo da aka shirya kuma ba ya ɗaukan yaunin kullum gaskiyar ɗan makarantar ana koyar da horon wani bi cikin wani harshen dabam da na ɗan makarantar, abun nan yana taimakawa wajen raba yaron da muhallinsa. Kenan horo- da-ilimi na zamani shi ne dalilin matsalolin sabawa da mahallin gargajiya, zaman kashe-wando, shashancin matasa.

Gurin haɗuwa tsakanin horo da ilmanta na gargajiya da horo da ilmi na zamani shi ne dukansu kamannun biyu sun gewaye mutum (yaro, matashi, babba) bisa kansa suke yin motsi saboda su ba shi sani, sanin zamantakewa da kuma sanin iya gwaninta dangane da buƙatun da ƙa'idodin al'umma. A wajen bambanci, suna zura idanu masamman ma wajen tsarin tafiyar da aikin koyo da koyarwa da tsarin darussa waɗansu zuwa wasu da halaye/kayan da aka yi amfani da su don cimma guri.

**6. Ingancinmakarantar gargajiya wajen makarantar boko ta ƙarni na 21, ayar nazari**

Masana masu hange, sakamakon makarantar gargajiya da ta zamani kamar yadda Abdu Mumuni, tun da wuri sun aza ƙudirorin yin nazari bisa yunƙurin makarantar gargajiya wajenƙarfafa makarantar zamani don cimma gurorinta. Wannan nazarin ba ya wuce na zamani ba a yanayin makarantar yau.

**6.1 Ginshiƙan nazari**

Horo da- ilimi na gargajiya, duk da halinsa na shekarar sama, yau ya zama kamar hazaƙar cin nasara a Afirika. Wannan cin nasarar ya kasance ga daidaita da halin yan makaranta kuma da muhallinsu, tsarin koyo da kayarwa, da buƙatun kuma da daidaton al'umma, ds. Ya kamata a ɗauki irin waɗannan ababen lokacin wallafawar siyasar horo da ilimi da kayayyakin

karantarwa da na tsarin tafiyar da karatun idan ana son a fitar da waɗansu saratsai na ci-gaban makaranta a yanzu. Wannan makarantar, mu tuna shi, tana fuskantar ƙalubalai dayawa da suke kawo cikas ga gwanintar ƙere-ƙere, kenan mai amfani.Don haka ne, ya kamata yau a sake yin tunani a wurin da horo da ilimi na galgajiya ya gaje cikin tsare-tsaren Hora da ilimidomin aƙididdige darajojinsa na karantarwa da na tsarin fiyar koyarwa don a ɗauki yaunin waɗannan ƙalubalan.Abdu Mumuni Diyoffo, da hankalin sanin wannan buƙatar, tuni ya tsara hanyoyin wannan shawarar.

«… Duk wani sabon rubuta littafi kuma da yake so ya zama mai amfani ga koyo da koyarwa da na horo da ilimi ta da yake daidai da halayen yanzu da kyakkyar makoma a gaba na ƙasashen Afirika baƙa don a rufe halin ƙasa da na al'umma na gaske, ta wata hanya a arawa horo da ilimi na gargajiya waɗansu daga cikin nasahalaye domin a sanya su manufa ta zamani kuma da ci-gabana horo da ilimi kuma ta sauran ko ta zaman tare da ita har tsawon wani lokaci da bada ƙarfin iza kanta.»Diyoff,2019, shafi na 21).

Shi ne na Abdu Mumuni a shirya ƙa'idodin biyu na horo da ilimi (gargajiya da zamani) saboda a ilimintarwa da horon halittu cukakku da shikashikan ci-gaban ƙasashensu. Haka ɗin cikin yanayin zamantakewa da tattalin arziki da siyasa mai ɗorewa sosai, cikin makaranta tsararra daga darussan makarantu, tare da cikakkun takardu wani gami suna can nesa da rayuwar yau-da-kullum. Zamantakewar da aka yi fata ta kamala daga, kowane ɗan Afirika na yanzu ta wani hali ko na waniya zama sakamakon horo da ilimi mai ruwa biyu (na gargajiya da na zamani).Su ko darajojin da aka yi aro, ya kamata a gano waɗanda aka fi so, waɗanda suka horo da ilimi a Afirika ta gargajiya fusahar da ta yi nasara.

### 6.2. Tabi'u nagarain na horo da ilimi na gargajiya wajen makarantar boko ta zamani

Tattaunawa dayawa a kewayen wannan tambayar yau suna bada damar cusa darajoji da aka ara wa makaranta ta gargajiya da suke iya kawo taimakonsu wajen gyaran foton makarantarmu. Ba mu iya banzata maƙamin marubutan jaddawalai da littattafan makarantu wajen cin nasarar wannan kacici-kacicin. Amma, a karo na ƙarshe, malaman horon malaman da malaman koyo da koyarwa wajen da ake neman agajin ƙarshe yauni ya rataya kansu da su ga ta wane hali ne za su iya shirya tare da darajojin aikin koyo da tsarin tafiyar da darasi da suka danganta da makarantar gargajiya tare da gwajin ayyukansu don su ci moriyar ta ƙwarai, saboda tafiyar da kyau don ci-gaban makarantar. Darajojin waɗannan su ne, ta aji-ajin aiki:

1. **Amfanin dubarun da hanyoyin koyarwa da suke sa ɗan makaranta ya kansance shi ne ginshiƙin horon kansa;**

A taƙaice ya cancanta yauni ya rataya kan malamai da horar da malaman makarantu bisa tafiyar da tsarin koyar da darussa da tsare-tsaren tafiyar da koyo da koyarwa cikin gidajen horo. Cikin wannan halin, ya kamata su gada masu ta hanyar jin ƙarfin tsare-tsaren tafiyar da koyo da koyarwa mafi inganci, waɗanda za su sanya ɗan makaranta ya zamajagoran horonsa da kansa. Malam a cikin yanayin ajiya amsa kiran na kyautata gyaran ayyukan ɗan makarantar da za ya ba ƙayadaddun ayyukan da za ya gudanar, a bambance da koyo da koyarwa na kai da

aka sani mai ƙayatarwa kaɗan da ake gani cikin yawan duka azuzuwan yanzu.Malamin makarantar ya zama matsari, jagora, mashawarci da za ya ja hankali inda ya kamata.

**2. Amfani da halaye na gida na ɗanmakaranta cikin abubuwan da darasin koyarwa ya ƙumsa;**

Hasken sani da za a koyar yana da mahimmanci ƙwarai na ainahin laƙantar sani na makaranta. Ya kamata mahorota su nanata da cewar malami bai kamata ba ya zamanto bawan jagoran malam ne ko na porfesssa ne. Duk da cikakken saninsa ya kamata ya san yadda za ya nesance shi da ƙarfafa ƙirƙira halayen ganin ƙop da ɗan makarantar ya saba da su. Waɗannan suna iya kasance wa abun mamaki na rayuwa ta yau-da-kullumda za ya zama shi nema'abuci, shaidu, ɗan kallo ko ma wanda abun ya shafa, bisa kanunsu za ya gabatar da ra'ayinsa ta yadda za ya iya koya cikin muhallin na ainahi wanda ba ya shirgintawa (ɓadda-kai).

**3. Alaƙa ta zahiri tsakanin horo da ilimi / bada sani da horo**

Hora da ilimiyana da matsayi uku, su ne (koyar sani); horon hali (horo kan ɗa'a da ɗanƙasanci), da horo/ fahintar ayyukan karkara (ta hanyar ayyukan hannu masu amfani), ziyartar ma'aikatu da wasu wurare na aikatan hannu, da wasu mutanen da suke da wani alawus, ds.Waɗannan matsayin yakamata a ɗauke su cikin lissafi idan ana so a ba ɗan makaranta horo cikakke.

**4. Amfani da harshunan gida na yan makaranta don su laƙanci sani da kyau ko su laƙanci harsuna biyu na koyo.**

Koyarwa cikin harshuna biyu daidai da daidai yana ba ɗan makaranta kuzari masamman ma wajen sauƙaƙa ɗaukaka sanin tun ba wanjen yaran da ba a sanya ba a cikin makaranta ba, yana sa wa cin babbar ribar lokaci kuma yana darajanta harsunan ƙasa da al'adu. Ya hi ba yan makaranta ribar cin nasarar karatunsu. Dubara ne wandasuka hi daraja an san ta.Ita ce malam ya kamata ya yi amfani da ita wajen kasawar harshe wanda ba ya wasa a gane sosai tambayoyin ga ɗan makaranta.Malamin makaranta ba zai yi shayin dogara ga harshen uwar yaron ba idan yana tsammanin ita ce ta hi sauƙin dangana sani, a sanya a gane da sauri ma'anar wata kalma, a ciyo kan wani lissahi, ds.Inda darajar amfanin da aka tsara nakoyo a harshuna biyu cikin tsare-tsare na makarantu.

5. Haɗawar aikin koda salon aiki da take ba koyo da koyarwa wani hali na gani da ido; kamata ya yi a kawo ƙarshen halin koyarwa na kai daga tsarin koyo da koyarwa da ake cewa na zamani. horo da ilimi da ake badawa ya ci a dubi ta halin ƙididdigar haɗe da horo/sanya aiki, dangance da nuna wa yan makaranta ayyukan hannu kuma da sanya masa sania haɗe da ayyukan muhallin.

Misali, cikin darasi bisa kan kasuwa, malam ba ya dogara ba kaɗai bisa hotunan gwaji na jagoran ko ta wata sahihin shiga fagen kwaikayo tare da yan makarantar don nuna kasuwa. Yawon buɗe ido cikin kasuwa na ajinya isa a nuna wa ɗan makaranta wannan muhallin, a taƙaice abubuwan da za su danganta da darasin (yin ciniki, saye, kayan kasuwa, mai saye, tarin kaya, ɗs). Bayan an dawo cikin aji, sai ya tambayi yan makaranta, dangance da iri-irin abubuwan da suka gani kuma suka tantance; su gabatar da kasuwar, su sake maimaita abun mamaki na tattaunawa da yan kasuwar, ds. Idan darasin ba ya yi katarin ba ranar

kasuwar, tsarin lokuttan aiki tunda ana iya birkita shi, malam yana iya maida darasin kuma ya gudanar da shi ranar kasuwar.

6. Rubutawar wani salon ɗan ƙasa da za a ba horo ta hanyar koyo da koyarwa adarajojin zamantakewa da tattalin arziki na al'ummar da ɗan makarantar ya huto daga ciki, kamar koyo da koyarwa demokraɗiya, da ɗanƙasanci, da al'adaɗa kiwon lahiya, da tattalin zaman lahiya tsakanin al'umma, da kawar da shaƙiyanci, da ɗiyauci, ɗaukaka kai, cikakken mutum, gafartawa, yahewa, wuce gona da iri, taimakon juna da ɗan uwanci, da dauriya, ds
Ya kamata malam ya tsara a hankali, darussa bisa horo kan ɗan ƙasanci da ɗa'a tunda wani bi ana yin banza dalilin wasu darussan. Dangance da horo kan ɗan ƙasanci, duk abin da ya shafi harakar ɗan ƙasanci, yakamata ya zaɓi tushoshin mai hazaƙa sosai daza a koyo da koyarwa kan darasin ladabi da biyayya.Haka zalika ma na koyo da koyarwada ɗa'a inda ake buƙatar tabi'o'i da halaye na gari ɗa darajojin al'ummomi, na mutane, ds.Waɗannan halayen biyu suna gina matsayi masu inganci na horo da ilimi dangance da matsayin bincike da jan hankali kan ayyuka kuma da ba za a banzata su ba. Makaranta tana ɗaukar gurin iyali cikin wannan horon.
Bayan rashin wuya na koyon sani, ɗaukan yaunin al'adun horo da ilimi na gargajiya cikin tsare-tsaren bada hora da ilimi yana iya kawo gudunmuwa wajen ɗaukan yaunin kasawa dayawa bisa tsarin zamantakewa da al'adu, arziki, da siyasa da ɗa'a.

**Kammalawa**

Horo da ilimi na Afirika ta gargajiya ya zama kamar na gwaji ne da ya samu nasaracikin horo na jiki, na ƙwalluwa da ɗa'ana Afirikawa. Wani irin salon bada horo da ilimi ne wanda ya ratsa shekaru kuma da yadda ya zauna cikin mataki a yau duk da faɗi-a-jina ƙasashen waje da ya yi ta bi tun ƙarnoni. Horo da ilimi na gargajiya yana da nasa iyawa/ gwaninta horo cikakke na ɗan Adam saboda ya kawo masa wajen buƙatunsa na kansa da na zaman jama'a.
Amma cikin duka kowace jama'a, wannan horo da ilimi na gargajiya shi ma yana da kasawarsa masamman ma gazawar ɗaukan yaunin hakin jama'a saboda idan ƙayukan ba za su iya gudanarwa bako kuma sanannu ne a ƙasashen ƙetare.Tsananinsa da tattalinsa suna sanya shi ya daure da juyyi, ga sabin manufofi zuwa ga sabin canje-canje. Horo da ilimi na gargajiya yana ɗauke da matsirin bambancinjama'a da na jinsi.Halinsa maras siffa, tsarinsa, waɗanda ake hana wa magana suna kewaye sashensa da rishinsa na mayar da ayyukansa dabam dabam bai ɗaya, na wajen abun da aka faɗa da abun da aka koya a tsakiyar wani ruƙuni da aka sani yana ƙera ƙarshensa. Amma, duka da waɗannan ƙarancin, horo da ilimi na Afirikata gargajiya yana nan a matsayinsa kullum na masani na makarantarmu. Ba ya shiga cikin saɓani da salon horo da ilimi na zamani, əmma daga bisani yana yi masa ciko. A halin yanzu makaranta tana ratsa wata mawuyaciyar matsala mai daɗewa duk da matakan da aka ɗauka saboda a kauda ta. Daidai ne a ƙara ƙarfingado na koyar da horo da tafiyar da aikin koyarwa ga waɗannan tarin matakkan na tsarin koyo da koyar da ilimin gargajiya.Kamar yadda mahoron masu horo da malaman makaranta suka ƙididdige da gaskiya kuma suka yi amfanisosai suna iya taimakawa don sake ba ma makarantar zamanitakardar yabo.

**Madogara**

Amadou, T. (2021). *Analyse conceptuelle des systèmes éducatifs en Afrique*. Module de formation (Niveau supérieur IFAENF).

Baba Moussa, A.R. Malam Moussa, L.& Rakotozafy, J. (2014). F*ondements philosophiques de l'éducation des adultes en Afrique*. UIL et presses universitaires d'Afrique.

Capelle, J. (1990). *L'éducation en Afrique noire à la veille des indépendances*. Paris. Karthala.

Dioffo, A.M. (2019). *L'éducation en Afrique* (Nouvelle édition). Québec. Editions Science et bien commun.

Frédéric, C. (2005). « Réflexions sur l'éducation en Afrique, Caractère polyvalent de l'éducation traditionnelle ». *Préface* à la nouvelle édition. http/scienceetbiencommun.press.pub, (xi)…(12), visité le 11/02/2021.

Inné, M. (1988). « Politique éducative du Niger ». *Pédagogie pratique pour l'Afrique*, volume1. Paris. Librairie intercontinentale.

Ki-Zerbo, J. (1990). (Ss dir). *Eduquer ou périr*. Unicef-Unesco. Paris, l'Harmattan.

Mungala, A. S. (1982) « L'éducation traditionnelle en Afrique et ses valeurs fondamentales ». *Ethiopiques*. Revue socialiste de cultures africaines. No 29. http/www.wathi.org.leducation.

Oumarou, F. (2006). *Education traditionnelle des enfants en milieu peulh*. Manuscrit. Bibliothèque IFAENF.

Paré Kaboré, A. & Rasmata Nabaloum-Bakyono, R. (2014). *Socio-psychologie de l'éducation des adultes en Afrique*. Presses universitaires d'Afrique.

Salifou, A. (1974). *L'éducation africaine traditionnelle*. Présence africaine. Nouvelle série. No 89 (1er trimestre). PP 3-14. https :www.jstor.org/stale/24349702.

Snyders, G. (1975). *Pédagogie progressiste*. Presses universitaires de France.

**Babi na 7**

**Tsarin gargajiya na koyo da kimantawar sanin da aka laƙanta : Yayaza a iya daidaita su da tabi'u na koyarwa na zamani a cikin aji a Afirika.**

**Mohamed Sagayar Moussa**

**Taƙaicewa**

Mataninyana tattaunawa a kan tsarin gargajiya na abubuwan koyo wanda yake tattare da al'amuran zamantakewa na yau da kullum a Afirika gaba ɗaya da kuma musamman a Nijar. An aiwatar da yanayinkoyo don ba wa yara dama a cikin wani nau'i na tsarin al'umma su gina ilimi a fannonin rayuwa da yawa. Yana tafiya da cewa a cikin halaye na koyo, al'umma tana taka rawar gani na zama mai tsaron al'adu kuma tana amfanin da wani tsarin kimantawar ƙoƙarin yaro don haɓɓaka fahimtarsa. Matani yana taƙaice bayani da yake bada shawarar nazari akan batutuwan koyo da mizantawar sani dabam-dabam da aka laƙanta da aka samu a Afirika, tare da maida hankali kan nazarin muhalli na tsarin abubuwan koyo a cikin ilmantarwa ta gargajiya da yuwuwar sauye-sauye da gyaran fuskar da suka dace a zamanin yau.Matanin ya nuna yadda albarkatun da za aiya samu daga ayyukan koyarwa na gargajiya za su iya bada damar ƙirƙira halaye na dubarun koyarwa a cikin makarantar zamani.

**Mahimman kalmomi :** Ilimi da horo na gargajiya, tsarinkimantawa/mizantawa, tsarin koyo, tabi'u na zamantakewa da gargajiya.

**Gabatarwa**

A Afirika, halayen koyorwa da koyoyana bada dama dabam-dabam na yinhulɗa tsakanin malammai da ƴan makaranta da kuma tsakanin ƴan makarantarwaɗanda, ta hanyar su ne ake gane rawar da kowa yake takawa cikin aikin ilimi : malammai suna nan don koyar da wani ɓangare na ilimi su kuma ƴan makaranta suna nan don su koye shi. Yanayin ajin don haka yana taka muhimmiyar rawa wajen koyon ɗan makaranta da kuma inganta abubuwan da ya koya. Aji ba kawai wuri ne inda ɗan makaranta za ya ɗaukar bayanai ba don daga baya ya yi amfani da su a gida, amma wuri ne na aiki da koyo.

Halin koyo a cikin muhallin makaranta wani mataki ne da malam ya shirya inda za ya bada wani sani, da zai riƙa ma'amala da ƴan makaranta a lokacin bada darussa.A cikin wannan halin koyon, muna da abin koyo/sani, malam, ƴan makaranta da kuma kayan aiki. Wannan shi ne dalilin da ya sanya dubarar koyarwa take buƙatar:

- Yadda ake maida ilimi sanin da ake iya koyarwa, abin nufi shi ne yaya za a sanya wannan ilimin a hannun ƴan makaranta don sauƙaƙe aikinsu na ƴan koyo;
- Yaya za a samun kyakkyawan yanayi don girka ilimi;
- Yaya za a tabbatar da cewa ingancin abin da aka faɗa yana da mahimmanci ga ingancin abin da aka samu, fahimta.

A cikin halayenjama'a na gargajiyada waɗanda suka samo asuli daga cikinsu a Afirika gaba ɗaya,musamman a Nijar, al'ummomi suna tsara kansu tare da kafa al'adun koyo waɗanda lokuta ne na bainin jama'a masu nuna canje-canjen matsayi (na zamantakewa, addini) na wani ɗan Adam. Ɗan adma ƙinyana rubuta shi cikin tsarin tabbatar da iyawarsu da kuma ƙwarewarsu na aiwatar da ayyukan jama'a da na karkara.

A yankin kudu da hamadar SaharanaAfirika, watsa da koyon tabi'u, yana nufin yin aiki ta hanyar al'umma masu halaya iri ɗaya, don samun ilimi cikin tsarin sadarwa da mutunta tabi'u da al'adu. Wannan nau'i na tsarin al'umma ya dogara ne kan ƙa'idoji da ƙayyadaddun al'adun da suka jadadda koyo daga abokan aiki (Chan, C, *et al.*, 2019) da kuma dattawa(kalmar da ya kamata a fahimta a nan kamar wani gungun mutane masu shekaruɗaya masu hikima da ake

ɗauka a matsayin abin koyi kuma wanda shawararsu da yardarsu sun zama tilas a cikin duk mahimmanci niyar jama'a.)
Babinmu yana magana ne kan batutuwan koyo da na kimantawa abubuwa da aka koyaa Afirika, tare da maida hankali kan nazarin mahalli da tsarin abubuwan koyo a cikin koyarwa ta gargajiya da kuma yiwuwar sauye-sauye da gyaran fuskar masu dacewa ga ayyukan azuzuwa.

Sashe na farko na babinantsaida da shi don kimantakoyarwa ta gargajiya a Afirika. Irin wannan nau'in bada horongalibina gamayya ne kuma yana barin babban wuri ga rarraba, haɗin kai da taimakon juna.

Sashe na biyu yana nazarin alaƙoƙin da suke tsakanin bayar da horo na gargajiya da kimanta abubuwan da aka koya a cikin yanayin Afirika mai riƙo da abubuwan da suka samo asuli daga cikinsu. Ana nufin a tambayi darajojin ayyukan kimantawar da kuma hulɗarsu tarebunƙasarmakarantar zamani (Yerly, 2017).
Cikin sashe na uku kuma kashin ƙarshe, muna nazarinyiwuwar mizantawadatatta cikin azuzuwa masu yawa da kuma yadda za a jagoranci kimantawata lokacin horo kamar wata hanya mai gamsarwa wadda ta danganta da kimantawa ta al'adun gargajiya.

## I. Ilimi da horon gargajiya, halaye da suka samo asali daga al'adu na gida

Mumuni (1967, p. 13-14) ya nuna gaba ɗaya waɗannan alamun na bada horo na gargajiya a Afirika ta baƙar fata waɗanda suke nuna al'umma mai riƙe da al'adu:

- An bata babban matsayi a cikin iyali da cikin al'umma;
- Halina gamayya da zamantakewa;
- Shigowardukiya da addini a rayuwar jama'a;
- wani hali mai amfani dayawa;
- wani aikin ƙaruwa a cikin lokaci tare da bunƙasar jiki, hankali da tunanin yaro.

Al'ummomin Afirika da kowanelokaci suna aiki a cikin wani nau'i na haɗin kai wanda aka san su da rabo da taimakon juna. Wannan nau'in aiki na gargajiya yana bada haske game da ayyukan kakanni da suka dogara da imani da fatawowida aka rarraba kuma aka rubuta cikin ƙa'idojin mutunta ɗan adam. Wannan shi ne dalilin da ya sanya Caille(2019, p.7)ya ci gaba da wannan ra'ayi : « ta hanyar ire-iren ƙabilu na al'ummomin baƙar fata na Afirika, bambancin nau'o'in tsarin jama'a,yana nuna bambanci a matakin ci-gaban tattalin arziki, siyasa da zamantakewa da aka cimma kafin mulkin mallaka,a fagen bada horowani adadi na kamanni gaba ɗaya da na gamayya, abubuwan da ba za aiya musun su ba na wataal'ummar al'adun awajenmutanen Afirika. »

### 1.1 Ilimin da horo nagargajiya,ƙayyadaddunabubuwan da suke darajantar da tabi'u najama'a.

Bambance-bambancen ƙabiluda tsara al'ummomi na ainafi, ɓangarori ne guda biyuda suke bayyana ilimi da horo tamkar wani arziki sobda shi kaɗai neda kuma ya mutunta ra'ayin jama'a a tattakin neman ci-gaban al'umma.
Horo da ilimi na gargajiya a Afirika ya danganta da halaye na musamman guda huɗu, (Kaili 2019)waɗandasuke nuna hanyar cimma wani guri na al'umma da zamantakewa cikin daidaitona musamman.

Hali na farko yana bada haske wajenmahimmancin zaman tare na al'umma, kimar da take zama abin nuni a cikin kowace hulɗata ɗan adam da ke da nufin ɗorewa.

Halina biyu yana ɗaukarilimi da horonzamantakewa na gargajiya a matsayin ma'aunimai darajantadukiyoyi da alaƙarsu da imani na addini. Yan asilin ƙasar suna girmama abin bautarsu a cikin tunaninsu da kumacikin duniyarsu ta zahiri.

Dangance da haki na uku, yana tabbatar da yawancin tabi'u ko halaye na yau da kullum waɗanda suke nuna ƙwararewa dabam-dabam a cikin rayuwar al'umma.

Hali na huɗu kuma na ƙarshe ya shafi ci-gaban yaro a cikin da'irar iyali da jama'ar da take kewayensa. An yi la'akari da yaro a matsayinsa na mutum wajen hidimar al'umma a cikin bunƙasar tunani, jiki da hankali. Maida hankalin jama'a shi ne abin dogaro don nufinshigarsa cikinjama'ar da kuma ya zama najama'a, don haka ne ma yasa « muhimmancin da aka ba wa tarbiya kuma yana nuna yadda dukan jama'a suke ƙoƙarita hanyoyi dabam-dabam : sanya hannun wani babba cikin tarbiyar kowane yaro, ɗaukar nauyin wasu ayyuka na ilmantarwa, a cikin ƙayyadaddun halaye da suke iya zama dabam-dabam, ta hanyar wakilai ko waɗanda aka zaɓa, masu aiki da suna al'umma. » (Caille, 2019, p .8).

### 1.2 Yanayin iyali,matakin farko na wata hanyar bi ta gudun mawa kai ɗaya da ta jama'a

A afirika, iyali yana ba yaro matsayin na wani tsari inda ƙauna ta uwaye maza ko mata tamkar wata kariya da tarbiya, mai buɗe hanya zuwa koyon abubuwa masu yawa. Da farko yaron yana ƙarƙashin kulawar uwa,ya zama mace ko namiji. Lokaci ne na koyon zamanttakewar al'umma da za a sanya yaro bisan wata hanya in da :

« A cikin ƙurciya, mahaifiya ita ce take da alhakin kula da yaron : tana ciyar da shi, tana kula da lafiyarshi : ba ƙarya ba ne a ce yaronAfirika ya kasance wani ɓangare na jikin mahaifiyarsa kawai saboda, kamar duk kowace uwaye, macen Afirika tana jin duk wani abu da ya shafe shi sosai,amma kuma saboda ta shayar da shi nono, yau da kullum, ta kula da shi, ta sanya shi i kwana kusada ita, ta kai shi ko'ina a bayanta. »(Caille 2019, p : 9-10).

Ana bin wannan kulawarta musamman tare da rakiyar uba da yake shirya shigarsa cikin al'ummakuma, sama da haka, yana gayyatar al'umma da su bada gudunmuwarsuwajen tarbiyarsa ta fuskar cikakkun ayyuka da kuma ƙarfafa abubuwan da aka koya masa.Yaron yana biyayya a zahiri kuma ya bar wa malamai da masu riƙon al'adu su jagorance shi. A bayyane yake cewa iyaye suna ɗaukar mafi yawan tarbiyar yaron kuma suna ba shi wani ƴancin kai wanda zai yi amfani da shi tareda goyon bayan sauran jama'a. Don shi ne yada kyautu a fahimci hakan : « [...]abin nufi uba ko uwa suna cika ayyukan malam, shi kuma yaro na ɗalibi; biyayya a gare shi ba ta da bambanci da ɗaukar nauyi da kuma neman gudunmuwa wajen babba. Uba ko uwa suna da alhakinjagorantar yaro a cikin farkon shigarshi cikin aiki jama'a (ƙirƙirowa, alaƙoƙi na zamantakewa da sauransu) da sa shi ya amfana daga gogewarsu ta rayuwa da kuma abubuwa ta hanyar sa-hannu mai mahimmanci(da kuma yadda ya dace da abin da ya dace) zuwa ayyukan rayuwa na zamantakewa. Uba ne yake koya wa matashin yaro, sannan in ya balaga ya koya mishi sana'arsa/aikita namiji, kamar yadda uwa ta koya wa ƙaramar yarinya, sai kuma budurwa duk abin da ya shafi rayuwar ƴa mata da kuma tauwa. » (Caille, 2019, p.10).

### 1.3 Ilimin da horo na gargajiya : sauyi mai zurfi na na halaye ko tabi'u

Baya ga komi, ilimin da horongargajiya ya samu sauye-sauye masu zurfi daga mulkin mallaka, wani lokacin da ya janyo taɓarɓarewar tsarin zamantakewa da aka kafa ba tare da la'akari da al'adu na Afiriki ba (Ki-Zerbo, 1992). Mulkin mallakar ba wai kawai ya canza al'adu ba, har ila yau, ya ɓata dangantaka da sanin jama'a ƴan asali ɗaya, ta hanyar kawo wata al'adata aikin koyo da yake bin ƙa'idojin da aka tsaida a kan gaskiya.(Akkari & Dasen, 2004).Yan afirika sun ɗauki da cewa : « makaranta da rayuwa ɗaya ne a cikin al'ummomin afirika, waɗanda suke darajantaaifuwa, yarinta da ilimi fiye da komai, kuma sun hana rashin aure, son kai da son abin duniya » (Caille, 2019.PXiii). Yaro shi ne dukiyar dukan jama'a, a cikin al'umma wanda ya

bambanta, marubatan sun jadadda, tare da : « bayyanardukiya da al'adu na al'ummar zamani mai nuna son kai » (Caille, 2019, p.58), wanda zai ɗauki nauyin yaɗa koyarwa na mulkin mallaka. Kuma wannan shi ne dalilin da ya sa, a farkon lokacinsa, « yaron Afirika ya kasance a cikin inuwar mata (kamar a ce ƙarƙashin bishiya) (Caille, p. xiii). Kafin a yi « la'akari da shi cikin al'ummar Afirika ta gargajiya a matsayin abin da kowa za ya yi tattali »(Caille, p. xiii). Wannan imani da yake sa yaron ya zama mai amfani ga kowa ya zama tsofon yayi ga idon sabuwar cibiyar tarbiyarwa da ake kira makarantar boko.

## II. Makarantar boko a Afirika

Don haka, jami'an mulkin mallaka sun ƙirƙira wasu dubaru da sharuɗɗa don koyar da mutanen cikin al'umma na ainafi. Bayan samun ƴancin kai, buƙatar kafatsari na gudanar da aiki da ta biyo bayan mulkin mallaka cikin gaggawa ta zama wajibi cikin ƙasashen Afirika. Don tabbatar wannan anniya , ya zama dole a ci gaba da tsarewani aikida yake gudana don haɗin gwiwa mai fuska biyu wanda abubuwan da suke cikin kwantaragin suka goyi bayan wani ban girma da aka lulluɓe. YanAfirika da suka lura da lamarikuma suka yarda da wannan aikin, za su iya daidaita kansu ne kawai don nuna gowon baya ga wannan hatsaniya da haɗin gwiwar da ba ta dace ba wacce ke bada damar samar da sauye-sauye a cikin salon rayuwar ƴan asalin ƙasar.Yan mulkin mallaka za su kafa makarantu da cibiyoyi na horarwa gaba ɗaya da suka sadaukar da kai ga ƙasashen Turawa, tare da barin mutane su yi imani da cewa waɗannan kyawawan halaye ne da al'ummar Afirika za ta gano su kuma taaiwatar da su don jin daɗin rayuwarsu.
A cikin abin da za ya biyo baya, muna haɓɓaka ra'ayoyin tarihi don nuna yadda mulkin mallaka ya yi tasiri sosai kuma ya canza tsarin zamantakewa bisa ga imani da tabi'u na gargajiya.Muna nazarin aji inda bambancin al'adu da ba ƙabilu suka mamaye tsarin yanayiinda daidaikun mutane suke zuwa koyarwa wasu kuma waɗansu suna zuwa don koyo kawai.
Manufar malama gargajiyance ita ce koyarwa (wanda aka fahimta a nan a matasayin wani aiki wanda ya ƙumshi sanar da wani abu mai amfani don ƙarfafa ƙarfinsa da kuma sanya su cancanta a wani yanki na musamman).Don tabbatar da cewa an yi haka, malam ya yi amfani da aiki na uku na koyarwa wanda shi ne kimantawarabubuwan da aka koya (aiki na farko shi ne shirya darasi, na biyu kuma aiwatar da shi). A cikin aikin ajina zamani, ana tantance ɗalibbai dabam-dabam, yayin da a gargajiyancedattawan gari ne suke tantance su.

### II.1 Nazari na tarihi

Koyarwata zamaninmulkin mallaka tana da manufar horar da ƙananan ma'aikatan da ake buƙata don amfanin mulkin mallakar da abin da ya yi imani da shi. Wannan nau'i na mulkin mallaka mai manufa ɗaya yana nuna cewa ya kamata akoyar da ƴan asalin ƙasar bisa da al'adunTurawa da kuma cewa wani nau'i na mutane da ya kamata ailmantar da su daga ilimin zamani wanda aka fi girkawa da kuma karkata zuwa ga ci-gaban sana'a da fusa'a.
Shugabannin Afirika sun ɗaukiduk waɗannan jagororin a matsayin mafi kyan zaɓi don ilimin zamani na al'ummomin, waɗanda aka karkasa kuma aka tsara su bisa ga ingancin gargajiya da kuma imaninsu na addini. Bayan mulkin mallaka ya bada hanyar sauye-sauye, (dole a auna su) ta bada damar gyaran fuska (dole ne a ƙayyade su), ta tsaida abubuwa masu kasancewa (dole ne a bayyana su) kuma ta kafa yankewar rabuwa (dole a fahimce su) (Bancel et Blanchard, 2003). Kasancewar zamanin mulkin mallaka da kuma zamanin bayan mulkin mallaka, ilimi da horo gargajiya ya samu sauye-sauye. Mun mayar da hankalinmu da nazarinmu kan wani yanki wanda ya kasance fanni ne da ya zama dole a yi kula da filin, tantance dubarun da kuma yanke shawarar abin da ya fi dacewa ga ƴan Afirika. Ya kasance wani tunani da za ayi a cikin nufin wayar da kansu da kuma wayar yin hankali na cigaban yankunnansu a wannan lokacin, wanda yake da shedar tsarin zamantakewa ba tare da wani tushe na gaske ba. Yanayin rayuwar ƴan Afirika, yanayin tunaninsu, yanayin yanke shawararsu sune hanyoyin da ƴan mulkin

mallakasuka ɗauka kamar ba su dace da dubarun ci- gaba ba. Ɓangaren ilimi da horo ya bunƙasa tare da kafa makarantu na farko.

### II.11.**Fannoni biyu masu mahimmanci : ilimi da horona galibi da ilimin koyon sana'a a cikin tsarin ilimin da horon gargajiya**

Ana gudanar da ilimi da horo na galibi a fanni biyu(Caille, 2019) :
- Fanni na farko wanda ya ƙumshi ilmantarwa ta hanyar rayuwar iyali da zamantakewa mai tambarin wasannin gargajiya,sauraren dattawa, gano tsiro, ilimin addini da tsafe-tsafe ;
- Fanni na biyu wanda yake da tambarinibadodi na koyo waɗanda wani lokaci gwaje-gwaje ne da suka fito daga wata kimantawa gama-gari a ƙarƙashin rakiyar da sa-idona dattawa don cimma wani matsayi na zamantakewa na dabam (yarinta da balaga misali don da'awar ɗaukar nauyin jama'a).

An miƙa alƙibilar ilimin koyon sana'a zuwa ga :

- koyon ayyukan noma (koyon aikin noma tare da iyaye da/ ko magajinnai) da kuma kiwo (kai bisashe kiyo da tsaron su) ;
- koyon fusa'o'i da ayyukan koyon ƙira, aikin katako, badukanci da saƙa a misali.

### II.1.2.**Dubarun kimantawa a fannoni biyu na ilimi da horo na gargajiya**

Kar da mu mantada matsayin iyali, al'umma da jama'a a fannin ilimi da horo a Afirika. Waɗannan ƙungiyoyin uku suna da tsarin na gaba-ɗaya tare da tsarin biyayyagame da shiri wandan ya yidaidai gwargwadon da shekarunsa da matsayinsa a cikin al'umma. Gaba ɗaya, abubuwan da aka koya cikin tsarin ilimi da horo suna rubuce cikin yanayi na gaba ɗaya kumaan kimanta su (tabbatar da matsayi bayan wani abun cikin tsari na musamman) an rubuta su a cikin girgam na gargajiya. A halin makaranta ta zamani, ana kimanta kowane mutum.
Babu wani daidaitaccen jadawali da aka rubuta cikin wani bayani na gaskiya da aka gangama, ra'ayoyi da saninda aka tsaida kuma tabbatattu a cikin al'ummomin Afirika. (Akkari & Dasen, 2004). Amma a maimakon haka al'adar ci-gaban na sani na ainafimai dogara bisa darajojiba bisa ƙa'idojin da aka lissafa ba ko sharuɗɗa kamar a tsari bada horo da ilimi ta zamani.Don haka ana iya yin samfari kimantawar abubuwan daaka koya a cikin allon da yake ƙasa:

**Allo na 1 : Samfarin kimantawa**

| fannoni | Abubuwan da suke ciki |
|---|---|
| Tsarin al'umma | Tsarin biyayya da ayyukan sassan iyali da na mulkin ƙananan hukumomi |
| Yanayin tabi'u na al'umma | Jerin tabi'unal'umma da sanya hannuwansu cikin mulkin ƙananan hukumomi |
| Karkasa tabi'un al'umma na gargajiya | Jerin sani na tushe da sauƙaƙa abin da suka ƙumsa |
| Kayyadewar ibada na koyi | Tsarin ayyukan ibada da ƙa'idojin yaba darajoji (gwaninta) na matasan da akasanya koyo |
| Amincewa da abubuwan da aka koya | Sauƙaƙa ƙa'idojin kimantawa dangance da fannin da matakin koyona abubuwan da aka koya na tushe |
| Tsarin shagulgulan gargajiya da tabbatar da matsayi dabam-dabam | Darajanta da yarda gaba ɗaya ta wata ƙwarewa ko kuma na wani mataki na cigaba da aka samu. |

### II.1.3 **Aji a matsayin wuri na koyarwa**

Ajin shi ne wurin da ya dace inda mutane suke zuwa don neman bayanai, yin aiki da kuma koyo. A cikin wannan halin, ƴan Afirika sun samu kansu suna fuskantar wani sabon yanayi, mai rikita wanda ya shafi fannin ilimi da horo, samfarorin koyarwa, hulɗa da malam, tsarurunkan kimantawarabubuwan da aka koya, dukkan wanitsari da yake da buƙatar sadaukarwa da gaskiya da kuma canjin aƙida a matakin zamantakewa.
Wannan nau'in na tsari na yanayin koyarwa yana da dangantaka da fitowar sabbin wuraren (Perrenoud, 1999) da aka raba tare da tsaidadden shiri da kuma malamn da yake shirya yanayin kayan aiki maimakon gungun dattawa na gargajiya. Ajin ya zama wuri inda ake haɓɓaka canjin kayan aiki a kewayen waniabu na cikin sanin taƙamaiman(Chevallard, 1992).Wannan hangen nesa na canji yana cilasawa rukunin aji wata daidaitawa ga ayyukan masu tsara ayyukan koyarwa na malam, ƙwararru masu ilimin koyarwa da kuma halarta mai ƙarfi na ɗalibbai wajen aiwatar da ayyukan da aka ba su amanarsu. A kowane hali, gudanarwa da tsarin ajin a cikin makarantar zamani ya haifar da sauye-sauye masu zurfi da yunƙurin daidaitawa a ɓangaren masu bada gudunmuwa a fannin koyar da ilimi a Afirika. Komawa daga ilimin gargajiya zuwa naayyukan da aka sabunta waɗanda suka raba sashe-sashe da nuna manufar abubuwan koyo cikin makarantu sun zama abun da za a nazari don shiga sabon zamani na koyo. Don haka mun fahimci cewa: « ma'anar tsarin ya ƙara wani muhimmin girma kuma yana jadadda kafa wani yanani na aiki wanda ya rarraba sassa na ayyukan da kuma hulɗa tsakaninsu »(Perrenoud, 1999, p. 540). Bayan wannan sabon tsarin, yana da mahimmanci a yi tambaya ko:
« za a iya, daga dubarun koyarwa , la'akari da tsarin tafiyar da aikin aji ko duk wani lokaci na horo kamar wani abun da ake buƙata na aiki, wani sharaɗi da ake buƙata, wani tsari wanda yake da tushe kuma yake bada damar samar da halaye na koyarwa da koyoda kuma ya ba su damar bin juna tare da wani ci-gaba, ba tare da ɓata lokaci ba, ta hanyar gyaranci-gaba mai ma'ana a cikin abubuwan da aka koya (Perrenoud, Ibid., p. 541).
Matsayin tsarin tafiyar da aikin aji cikin ayyukan koyarwa namalamyana tsammanin ya kamata a yi tambaya a kan tsari da amfanin kimantawar abubuwan da aka koya.

## III. Kimanta abin da aka koya cikin halayen koyarwa da koyo a Afirika

A Afirika, maganar kimantawa ba tsaidadden aiki ne ba da ya samu tushe daga kimiya da kuma mai matsayin ƙungiya ta hukuma mai shiryayyun dokoki. A cikin ilimin gargajiya kimantawa tana nufin a tsaida wani tsari na karkara na rabo da sanin darajar ɗan adam. Ƙungiyoyin gargajiya na Afirika suna sanya halin haɗin kai da taimakon juna a gaba. Wannan al'adar ta iyaye da kakanni ta mamaye gaba ɗaya kimantawata ƙarshen koyo wadda ita ce dubarar koyarwa na uku a cikin yanayin koyarwa da koyo(bayan shiryawa da kuma tafiyar da aikin darasi). Muna yin kwantaccen nau'ikan kimantawa guda biyu a cikin allon da yake ƙasa don mu yi nazari kuma daga baya sassan masu yiwuwa.

**Allo na 2 : Nau'in kimantawa**

| **Kimantawa cikin ilimi da horoNngargajiya a Afirika** | **Kimantawa cikin ilimi da horo na zamani a Afirika** |
|---|---|
| **Matakai na farko** | |
| Ra'ayi da matsayi a cikin jama'a | Samun daidaitattun iya yi |
| **Abubuwan da suka girku** | |
| Darajojin jama'a | Tsarin ma'aikatu |
| **ƙa'idojin tsare-tsare** | |
| Hawa-hawa zuwa ga iyali da karkara | Hawa-hawa zuwa aji |
| Iyali da mambobin karkara dangance da tsarin jama'a | Malammai dagabayanai da ake aiki da su |
| **Mahimman matakan aiwatarwa** | |
| Kwamitin dattawa | Shirya darasi |

| Tsarin al'adu | Gudanarwar darasi |
|---|---|
| Bikin amincewa da yarda da abubuwan da aka koya | Kimantawarabubuwan da aka koya |

A cikin allon, akwai bambanci babba a cikin hanyar da kuma dubarun da aka yi amfani da su. A cikin yanayin ilimi d horo na gargajiya, al'ummomi sun fi son rabawa da amincewa da haɗin kai tare da yin aikin bayan an yi wani babban taro. Kimantawa a cikin ayyukan aji tana da alaƙa da wani batu da aka sama shaida a ƙarshe.

Ma'anar kimantawa mai kima da suna ta fito ne daga cewa malam dole ne ya jagoranci ɗan makaranta a cikin aikinsa na makaranta. Yana neman inda yake da matsaloli don ba shi damar gano hanyoyin masu inganci don ya ci gaba a cikin karatunsa. Kimantawa ce da take gudana a lokacin da kuma da ƙarshen kowane aikin koyo.

Daga wani hangen nesa, kimantawa tana ɗauke da darajoji(Perrenoud, 1999) :

-ga ɗan makaranta tana basa damar samun ilimi mai zurfi, ƙididdige iyawarsa da kasawarsa, maimaitawar wani aji (dawowa baya) fita daga tsarin (kora) kuma samun takardar shaida ko kammala karatun samun digiri;

-ga malam, dubarar koyarwa ne wanda ta hanyarshi, ake yanke shawarar zuwa zaman aiki na gaba, gabatar da sabbin ayyuka, sake duba dubarun koyarwarsa da kumaduba ƙa'idojin kimantawa. Ayyukan da malam ya gabatar sun fito daga ƙarƙashin yanayin dubarun koyor da karantu, waɗanda suke sanya ɗalib ya kamawani aiki. Kalmar aiki tana zuwatare da tunanin rubuta, idan ba wajibi ba ne ga ɗalibi ya aiwatar da ayyukan koyo;

-ga uwaye, wata dama ce da za a sanar da su ƙoƙari ko rishin ƙoƙarin yaro, da kuma samun labarin ci-gaba da aka samu cikin tafiyar karatunsa.

Bada horo na gargajiya yana sanya kimantawa a cikin tsarin da aka gina ta hanyar dubaru na haɗinkai wanda suke da alamun da suke jagorantar al'umma zuwa ga samun sakamakon wani tsari wanda dole ne a tabbatar da ci-gabanshi da nasarorinshi.Hukumace take da alhakin yanke shawara a kowane lamari ko wane yaro ya cancanci dawani canjin matsayi don bada gudunmuwar wajen ci-gaban zamantakewa da tattalin arziki na ƙauye. Ana ɗaukar yaro a matsayin yaron ƙauye amma ba ɗan cikin ƙauye ba. Wannan tafiyar ta al'umma ta tunatar da iyalai kai tsaye ga hakinsuna tarbiyyantar da ƴaƴansu cikin tsanani da mutunta kimar ɗan adam. Da wannan hangen ne a yanzu muke nazarin kimantawa a cikin azuzuwan masu cinkoso.

### III.1.Kimantawar abubuwan a koya, yaya za a iya daidaita su cikin azuzuwan makarantun boko naAfirika?

Kimantawa wani mataki mai mahimmanci a cikin dubarun koyarwa a fanni ilimi da horo .Ita ce aikinkoyarwa na uku bayan shiryawa da tafiyar da darasin. Tana kawo ƙarshen ayyukan koyarwa da koyo kuma tana bayyana sauyi da aka samu ko gurin da aka cimma. Don haka kimantawa ta zama babbar al'ada kuma ba za a iya kauce mata a cikin yanayin koyarwa da koyo. Tanazama abu mai ɗaukar hankalin malammai wanda ya zama wani nauyi da aiki mai mahimmanciwaɗanda za su iya zaman masu amfani ga aikinsu na koyarwa.

### III.2.Kimantawar ta bayan koyo a matsayin hanyar haɗa kimantawar al'adun Afirika

Akwai nau'oi kimantawa dayawa amma biyu suna nan a cikin yanayin koyarwa da koyoa cikin makarantu da cibiyoyin horo a Afirika. Ta farko ita ce aka fi yi ga abun da ya shafi kimantawa, ta koyo na ainafin, koyo daga ɗalibi ta hanyar sa ido ga abubuwan da suka sani wanda yake haifar da siffa ta alama, cancanta, wucewa zuwa aji na gaba. Ya yi daidai da lissafin ƙwararrun abubuwan da aka koyo.

Kimantawa ta bayan koyo tana nuna ɗalibi dangance da wata manufa da aka bada. Tana ba da damar ganin ko yana da mahimmancidon gyara tsarin ilmantarwa da yake ci gaba, don gaya wa ɗalibininda yake dangane da manufar. Har ila yau, tana ba wa ɗalibbai damar sanin inda a cikin tsarin koyarwa da koyo, kuma yana tsammanin cewa an haskaka sani don ɗalibi ya yi hankali da hanyoyin da ya sanya gaba wurin tafiyar da aiki, na waɗanda sukadace/masu tasiri da waɗanda ba su da kyau: Dan saita tunani mai mahimmanci akan aikinsa (Shahvali et Zarafshani, 2002).Ana aiwatar da kimantawa ta ƙarshen koyolokacin ayyukan koyo,. Manufarta ita ce sanar da ɗalibi gaba ɗaya kuma daidai gwargwado nisan da ya raba shi da manufar da kuma matsalolin da yakefuskanta; amma kuma a sanar da malam yadda ɗalibi suke karɓar koyarwarsa,da ba shi damar ya daidaita. Don haka muhimman ɓangare ne na koyo kuma tana zama wani bayani da yake ba ɗalibi damar ci gaba shi kuma malam ya inganta ayyukansa. Ainahin hanya ce ta mayar da martani, don haka, ba ta da kowane takunkumi kuma ba ta da wata ma'ana face ta koyarwa.
A cikin wannan hangen nesa, yana da mahimmanci a yi la'akari da kimantawa ta bayan koyo a matsayin hanya mai gamsarwa don haɓɓakakimantawar al'adun Afirika.
A Afirika, mun yi nuni da cewa kimantawa ta dogara ne kan tsarin rarrabawa, taimakon juna da haɗin kai na aiki. Wannanshi ne dalilin da ya sa kimantawa zai taiya dacewa da al'amuran zamantakewa da na gargajiya. A cikin allon mai zuwa, mun gabatar da halayen kimantawata bayan koyo a cikin ginshiƙi na farko, kuma a cikin shafi na biyu na dubarun amincewa masu alaƙa da ayyukan gargajiya.

**Allo na 3 : Fasaloli da dubarun shawo kan kimantawa**

| Fasalolin kimantawa ta bayan koyo | Dubarun daidaitawa masu yuwuwa zuwa yanayin Afirika (mai da makarantar ta zama cibiyar albarkatun ilimi) |
|---|---|
| Danganta ɗalibi da wata manufa da aka sanya gaba | Tsara da tallafa wa ɗalibbai wajen gudanar da bincike don gano ƙauyensu, tarihinsu, albarkatunsu kuma rawar da suke iya takawa don bada gudunmurwasu wajen ci-gabansu. Ana iya kimanta su ta hanyar ƙoƙarinsu na yin wani bincike da tattara sakamakon. |
| Sauya dubarun koyarwa da koyo | Darajanta ayyuka na gargajiya a cikin tsarin ilimin gida, kalamai na al'adu da na gargajiya. Ana iya tantance ɗalibbai bisa ƙididdige abubuwa na al'adun gargajiya da yin jerin kyawawan ayyuka na karkara. |
| Ana yin shi lokacin ayyukan koyo | Shirya sanin na gargajiya tare da haɗa shi a cikin manhaja ta amfani da harsunan ƙasa a zaman hanyar koyarwa : kimantawa ɗalibbai za ta maida hankali kan fitar da ilimi don jeranta sani na gargajiya wanda amfanin da aji zai biyo baya |
| Sanar da ɗalibbai ci gaba da matsalolin da suke fuskanta | Haɓɓaka ma'aunin don ƙwarewa da kimantawar ilimin gida. Kimantawar za ta mayar da hankali ne a kan wuraren ilimi da kuma abubuwan da ake tattare da su. |
| Sanar da malam kan yadda ɗalibbai suke karɓar koyarwarsa ta yadda zai tsara ta | Kafa tsarin rakiya da gyaran tarbiya. Malamman da suke cikin zauren koyarwa za |

| | |
|---|---|
| Fasalolin kimantawa ta bayan koyo | Dubarun daidaitawa masu yuwuwa zuwa yanayin Afirika (mai da makarantar ta zama cibiyar albarkatun ilimi) |
| | su yi tunanin hanyoyin tallafawa ɗalibban da suke cikin wahala. Za a iya tsara ɗalibbai a kwamati don gabatar wa malammai matsalolin da suke fuskanta. |
| Yana shiga cikin tsarin fahimtar sani a lokaci da kuma bayan aiwatar da wani aiki | Bada dama ga al'umma ta shigo cikin aikin gudanarwa da kuma jan ragamar makarantar. Shigar da iyaye zai zama wata dama don yin tunani a kan makaranta cibiyar albarkatun ilimi. Ɗalibbai za su iya tantance sa hannu da rawar da iyaye za su taka ta tsarin gudanar da ayyukan makaranta. |
| Maida ɗalibi ya zama mai kula da tsarin ilmantarwa ta hanyar ba shi damar sarrafa kurakuransa da kuma nasarorinsa. | Haɓɓaka ilimi da horo mai cin gashin kanta wanda aka riga aka samo asali a cikin ayyuka na gargajiya. Malammai suna shirya kayan aikin tattara bayanai. Ana kimanta ɗalibbai akan ƙwarewarsu a cikin tattara bayanai. Za a iya kimanta su akan sarrafa kuskure da gyarawa. |

Allon yana bada bayanai game da yadda za a iya daidaita kimantantwaabun da aka koya da yadda za a tsamo ayyukan ilimin gargajiya don inganta ayyukan yauda kullum a cikin aji. Yanayin zamantakewa da tattalin arziki da al'adu na Afirika yana buɗe hanyoyin koyo masu yawa da inganta ayyuka. Ana gani da kyau akwai hanyoyi da dubaru.Dole ne a yi amfani da su a cikin yanayin tsaka-tsakin da yake gabatar da malamai, hukumomin ilimi, iyayen ƴan makaranta da ɗalibbai a kewaye da abubuwan da suke cikin yanki kuma su yi la'akari da shirye-shiryen koyarwa haɗa tarbiya da aiki mai albarka. Wannan zai zama wata dama ta mayar da martani ga buƙatar ci-gaban zamantakewa da tattalin arziki na muhalli ta hanyar jagorantar malam zuwa horar da ma'aikatan da ake buƙata a fannin noma da kiyo don ba da gudummuwa ga ci-gaban albarkatun da suka shafi muhalli. A cikin hangen nesa, yana da kyau a jagoranci tsare-tsaren koyarwa don sake canza tunanin da buɗe hankalin yaro ta hanyar haɓɓaka kasuwancin hannu. Sa'an nan kuma za a iya samar da tsarin karatu wanda yake nuna albarkaku da yuwuwar. Ana iya gabatar da waɗannan a cikin waɗannan madogarai masu zuwa :

-tsarin cancanta don tantance mahimman ayyukan koyo, ƙwarewar da za a haɓɓaka, wurin aiwatarwa, nau'o'i haɗin kai da yanayin kimantawa ;

- tsarin koyarwa da koyo da kimantawa don tantance fagen ilimi, fannonin da ake da alaƙa, jadawali da hanyoyin tantancewa. Mun nace a kan waɗannan matanan, tun da yawan ƴan makaranta a cikin makarantu yana haɓɓaka mai tada hankali.

III.3. **Yaya za a sanya kimantawa mai inganci cikin azuzuwa masu yawan ɗalibbai ?**

De Jomtien (Sanarwar Duniya kan bada horo ga kowa a 1990) A cikin tsarin Dakar(don biyan bukatun ilimi masu mahimmanci a 2000), ƙasashen Afirika da dama sun yi ƙoƙarin bunƙasar da kansu, da samar da duka damar shigamakarantu. Tun daga wannan lokacin ake samun cinkoso azuzuwa, musamman a makarantunfiramare.Malamman suna fuskantar matsalar adadi mai yawa na ƴan makaranta, ba tare dasamun isasshen horo ba kan tafiyar da aikin cikin azuzuwa da kuma tsarin kimantawar abubuwan da aka koya. Idan aka fuskanci wannan yanayin,

yana da mahimmanci a tambayi yadda za a sake tsara hanyoyin koyarwa da dubaru don bai wa ɗalibbai damar koyo da su kuma malammai su kimantaabubuwan da ɗaliban suka koya. Ana jagorantar malammai don sake duba tunaninsu na koyarwa don haka tsarin su a cikin mahalli ayyukan kimantawa (Prosser et Trigwell, 1999). Muna ba da shawarar dubarun masu zuwa don yin kimantawa ya zama aikin da ake rabawa.

### III.3.1Sabbin hanyoyin koyarwa (koyarwa ta dabam)

A yau akwai sabbin hanyoyin koyarwa da suke bada damar yin wata irin koyarwa, koyo wani iri, da kimantawar wata iri ta hanyar sabon matakin koyarwa da yake ba ƴan makarantafifiko kan ɗaukar alkawalin, sabunta ayyukan ilmantarwa da horarwa, caccanza nau'o'in kimantawa da kuma amfani da tsarin fusa'o'in ƙwararru(Chamoux, 1986). Muna bada shawarar wannan fusa'ar Yi tunani-Kwatanta-Raba wanda za a iya daidaita ta zuwa adadi mai yawa na ƴan makaranta. Ta dogara ne akan ƙa'idoji da ayyuka masu zuwa :

-Ƙa'ida

Dubarar « Yi tunani-Kwatanta-Raba » an girka ta don bai dukan ɗalibbaidamar shiga cikin tsarin koyo a cikin babban rukuni. An bai wa ɗalibbai damar su yi tunanin wata matsala ko tambaya ɗaya bayan ɗaya sannan su kwatanta amsarsu da ɗaya ko da ɗalibbai da yawa sannan su raba wannan amsar a cikin babba rukuni.

-Yadda aikin yake tafiya

Ƙididdige mayan bayanai, masu mahimmanci ko waɗanda aka sani kamar masu wahala a koyarwa.

1. A aza tambaya kuma a tambayi ƴan makaranta kowa ya yi tunani (tunani) cikin ɗan gajeren lokaci. Yana iya dacewa ya zama a tambaye su su rubuta amsarsu don ba su damar tsara ta.
2. A tambayi ƴan makaranta su kwatanta amsarsu da ta makwabcinsu ko wani ƙaramin rukuni (bambanta) kuma su yarda da amsa gama gari.
3. A tambayi mayan rukuna na mutum biyu-biyu a kan mafita guda (rarraba). malam yana iya sarrafa wannan lokacin ta hanyar tambayar masu sa-kai don bayyana ra'ayoyinsu ko ta hanyar gano mutum biyu-biyu a haka.

1

http://www.cedip.developpement-durable.gouv.fr/IMG/pdf/Fiches_methodes_animation_cle29d6dd.pdf

Consulté le 10/03/2019

### III.3.2Sabbin siffofi na koyo (koyo na dabam)

Ya zama dole a yi hasashe don sabbin nau'o'in koyo da aka sama ido akan manufofin koyo da ake hange da kuma dubarun koyarwa masu yiwuwa. Don kimantaabubuwan da aka koya, yana da mahimmanci a yi tunani game da dubarun da alaƙa tsakanin matakai uku masu zuwa: 1) manufofin koyo 2) ayyukan koyarwa 3) dubarun kimantawa

1) Manufar koyo: menene ya kamata ɗan makaranta ya sani ko zai iya yi a ƙarshen darasin? Ana rubuta manufar koyo kamar haka: "a ƙarshen darasi, ya kamata ɗalibi ya iya + fi'ili Bloom"

2) Ayyukan ilimi: waɗanne ayyuka zan aiwatar don bai wa yara damar koyo? Wace dubara zan yi amfani da ita wajen aiwatar da darasin?

3) Dubarartantancewa:yaya zan tantance abubuwan da aka koya?

### III.3.3 Sabbin siffofi na koyo (kimantawa ta dabam)

Kimantawar abubuwan da ɗalibbaisuka koya wani sashe ne mai mahimmanci na tsarin koyarwa da koyo. Don zama mai inganci da manufa, ana iya amfani da mataki mai zuwa don ya zaman abun da aka zayana don jagoranci:

- Kirƙirayanayin koyo wanda yake tsara ɗalibi don cika wani aiki,
- A albarkacin tabbatar da wannan aikin, dole ne ɗalibi ya gamu da cikas,
- Don ya samu ya tsallaka wannan cikas, ana bashi ummurni da wasu matsaloli da kayan aiki ;
- Ta hanyar wasa da ummurnin kan matsaloli da albarkatun, ɗalibi yana aiki a hankali kuma yana girka sabon sani : manufar koyo.
- Wannan sanin, da zarar an gano shi, zai iya, bisa ƙa'ida, ya sake amfani da shi cikin wani aikin.

**Kammalawa**

Babin namu ya kawo abubuwa masu zuwa ta fuskar darasin da za mu koya. Ilimin da horo na gargajiya da tsarin ilmantarwa abubuwa ne guda biyu waɗanda suke nuna tsarin da aiki na Al'ummomin Afirika (Akkari et Dasen, 2004). Jama'a a cikin tunaninsu na ilimi wani ɓangare ne na sassa uku na rabawa, taimakonjuna, da haɗin kai. Kasancewar zamantakewa da Bambance-bambancen ƙabilanci su ne tushen da yake girka yanayin koyo a Afirika.

Hanyoyi da tsare-tsaren don tantance koyosun daɗe suna kan layi tare da kyawawan ayyuka waɗanda suke da tushe mai zurfi a cikin abin da aka amince da shi a matsayin alama da tambari na musamman ga Afirika.

Mun yi ƙoƙarin yin nazarin yanayi da ayyukan da kasancewar mai mulkin mallaka ya yi tasiri acikin tsarin ilimi wanda yake damun rayuwar yau da kullum na mutanen Afirika.

Babin ya yi nazari a kan yanayin koyo a Afirika da suke da al'adun gargajiya tare da matsalolinsa da albarkatunsa, tare da shawo kan cikas don nazarin hanyoyin kimantawa waɗanda ya kamata su dace da na koyarwa.

Mun daidaita tunani akan darajojin ilimi da horo na gargajiya da alaƙarsa tare da kimantawar koyo bisa ƙoƙarin mutum a makarantar zamani. Binciken ya kammala da cewa ana iya bayyana kimar koyarwa a cikin tsarin tsakatsaki wanda ya ƙumshi ƙayyadaddun kima daga ayyuka na ƙarshe da kuma nazarin darajojin da yake bayarwa.Duk da haka ya kamata a lura cewa babin cikin tunaninshi ya yi tambayar yiwuwar daidaituwada kuma sakamakon da aka samu ta fuskar canji a cikin ayyukan koyarwa. Gyaran tsarin karatu zai zama mafi kyawun nunawa alal misali don haɓɓaka albarkatun da suka fi dacewa da gaskiyar zamantakewa waɗanda suke gabatarda ayyukan da aka gabatar wa ɗalibbai tare da tsarin kimantaabubuwan da aka koya da suke maida hankali kan ƴancin kai, taimakon juna da haɗin kai, kima uku don samun mutum mai haɗin kai da al'umma kuma mai cin gashin kanshi(Remillard, 2010). Mun lura cewa binciken bai yi la'akari da abubuwa biyu da za a iya yin nazariba : ƙwarewar da malamai suke da su a halin yanzu game dailimin gargajiya da kuma ilimi mai zurfi don cin tsamo sanin.

- Karfin cibiyoyin horar da malam don horar da malamai don yin la'akari da ayyukan zamantakewa a cikin girka halayen koyarwa da kuma kimanta abubuwan da aka koya.

**Madogarai**


Akkari. A & Dasen. P.R. [dir] (2004). De l'ethnocentrisme de la pédagogie et ses remèdes. Pédagogies et pédagogues du sud. Paris : L'Harmattan.

Bancel, N., & Blanchard, P. (2003). Avant-propos/Culture post-coloniale: le temps des héritages. Nous, 1871(1931).

Caille, F. (2019). L'éducation en Afrique.

Chamoux M.-N. (1986). « Apprendre autrement ». In P. Rossel (dir.), Demain l'artisanat ? Paris : PUF ; Genève : Institut universitaires d'études du développement, p. 209-235.

Chan, C., Embi, M., & Hashim, H. (2019). Primary school teachers' readiness towards heutagogy and peeragogy. *Asian Education Studies, 4*(1), 11-21. doi:http://dx.doi.org/10.20849/aes.v4i1.602

Chevallard, Y. (1992). Concepts fondamentaux de la didactique : perspectives apportées par une approche anthropologique. Recherches en Didactique des Mathématiques, 12(1), 73-112.

Dasen, P. R. (2004). Education informelle et processus d'apprentissage. In A. Akkari & P. R. Dasen (Eds.), Pédagogies et pédagogues du Sud (pp. 19-47). Paris : L'Harmattan.

Ki-Zerbo, J. (Ed.). (1992). C0111pagnonsdu soleil. Paris: Fondation pour le Progrès de l'Homme - La Découverte - UNESCO.

Marin, J. (2000). Une éducation appropriée aux peuples autochtones d'Amérique latine. ln P. R. Dasen & C. Perregaux (Eds.), Pourquoi des approches interculturelles en sciences de l'éducation? (pp.261-280). Bruxelles: DeBoeck Université.

Mohamed Sagayar, M. (2011). Action du professeur et pratiques de formation : analyses en classes de cours préparatoires et dans une cellule d' animation pédagogique, dans le contexte du Niger. These en Sciences de l'Education, Université Rennes 2, Rennes, France.

Moumouni, A. (1967). L'éducation en Afrique, Paris, François Maspero. 399 p.

Perrenoud. P (1999). « De la gestion de classe à l'organisation du travail dans un cycle d'apprentissage »/ Revue des sciences de l'éducation, vol. 25, n° 3, p. 533-570.

Prosser, M., & Trigwell, K. (1999). Understanding learning and teaching: The experience in higher education. London: SRHE/Open University Press.

Remillard, J. (2010). Modes d'engagement : comprendre les interactions entre les professeurs et les ressources curriculaires. In G. Gueudet & L. Trouche (Eds), Ressources Vives, 201-216. Lyon/Rennes : INRP/Presses Universitaires de Rennes.

Shahvali. M & Zarafshani. K. (2002). « L'utilisation des techniques d'évaluation participative dans les zones rurales comme stratégies métacognitives pour développer les savoirs autochtones : une étude de cas », Revue internationale des sciences sociales n° 173, p. 453-459.

Yerly, G. (2017). Évaluation des apprentissages en classe et évaluation à grande échelle : quels sont les effets des épreuves externes sur les pratiques évaluatives des enseignants ? Mesure et évaluation en éducation, 40(1), 33–60. https://doi.org/10.7202/1041003ar

# Babi na 8

# Karin magana cikin koyarwa da koyon harsuna-al’adu a makarantar Afirika : arziki da aka mance.

Amadou Saibou Adamou

## Taƙaicewa :

Labarin yana kawo bayani kan karin magana a matsayin ƙirƙire-ƙirƙire na tabi’un jawabai na al’umma da ake iya amfani da su cikin halayen koyarwa a cikin azuzuwa koyar da harshe a Afirika. Da yake karin maganganu suka cikin kowace magana har ma a cikin rubutaccen bayani a Afirika, waɗannan ƙananan bayanai, da aka tsara cikin harshe da kuma suke da ma’ana ta al’ada.ba su zo ba cikin jadawalan makarantun boko, wato ba a aiki da su a fannin koyrawa na makarantu a Afirika. Mantuwa ce da ake gani zahiri. Wannan babi da za ya dogara da hanyar koyarwa, za ya yi nazarin hanyoyin amfani da karin magana cikin makarantu na zamani don a samar wa yara da tarbiya tagari, musamman ma wajen koyon harsuna-al’adu. Bayan mun ga matsayin karin magana cikin al’umomi na Afirika, labarin yana gabatar da shi a matsayin madogara da kuma wani jinsi na labarin mai amfani na koyar da harshe-al’adu ; a zahiri, a ƙarshe babin yana bada hanyoyin ayukkan koyarwa-koyo na bayanai a dunƙule a cikin harsuna a Afirika.

**Mahimman kalmomi :** Karin magana, koyarwa-koyo, harshe-al’ada, ƙwarewar harsuna, hanyar/madogarar koyarwa.

## Introduction

Ana ƙirƙira ko sake faɗin karin magana cikin dukkan al’umomi. An gaɗi karin magana daga kakanni ko ana ƙirƙira shi a halin yanzu don nuna yadda mutane suke ɗaukan wasu mutane ; don bada bayanin rayuwa. Karin magana yana cikin taƙaittacen bayani kamar wata yar magana, sheɗara, ko wani habaici….Galibi, karin magana wata sheɗara ce mai bayyana wani girma ko daraja da kuma yake koyar da mutane wasu tabi’u. Ana gane karin magana daga wasu alamomi na salo na juyen magana, na basirar koyarwa, don shi ake ganin karin magana yakan yin mahimmanci wajen nazarin harsuna da halayar dan Adam. Nazarin ire-iren waɗannan taƙaitattun maganganu ya aifar da wani ƙaramin fanni na sani ko darasi da ake kira paremoloji.

Wasu rukunai na al’uma a Afirika (musamman ma yankin karkara) sun sanya karin magana cikin bayanansu na rayuwar yau da kullum, a cewar al’umomin, ana iya cewa salo ne na magana. A halin yanzu karin magana ya shiga cikin duniyar rubutu, musamman ma ta hanyar wallafawar ƙananan litattafain paremoloji a ɓangare nazarin, kalamai, ƙirƙirar adabi (da ta buɗe wa labarin baka ƙota) da bayanai na talla da suke yawan amfani da bayanin karin magana.

Amma, idan ba ko katari ba, babu karin magana a cikin jadawalin makaranta, ballantana cikin littattafan da darussa koyarwa na makarantar a Afirika. Kenan, wani mahimmin abu mai tsari na cikin harshen al’uma a Afirika, wani abu ne mai daraja na harshe da al’ada, kuma wani arziki ne buƙata ta hanyar koyarwa take nan ajiye a gehen matsalolin makaranta, musamman a fannin koyarwa-koyo na harsuna-al’aduYa kamata karin magana ya samu wuri da ya dace da shi cikin ayukkan koyar da harsuna da al’adau, cikin horo da galibi a fannin tarbiyar

yaron Afirika kamar yadda aka sani can da. Ana cin moriyar karin magana cikin fannoni da dama na koyarwa-koyo.

Babi na farko za ya bayyana fa'idar karin magana cikin tsari na koyrawa-koyo na harsuna –al'adu. A taƙaice, wannan gudummar tamu ta dogara da gurirrika ukku : gano mahimmancin bayyana karin magna a cikin al'umomi na Afirika ; nuna amfanin shi a matsayin madogara ko hanyar koyarwa ; da bada shawarwari na hanyoyi na koyarwa da su bada damar cin moriyar karin magana cikin azuzuwan koyo harsuna a makarantu Afirika. A lura da cewa, shawarwari na galibi ne kuma ba za a yi aikin ba da su a wani mataki na karutu ba da aka ƙayyade. Hanyoyi ne da za su iya bada damar tafiyar da ayyukan koyo da kuma ma hujjojin da irin wannan salo na magana da ake amfani da shi a fannin koyar da harsuna-al'adu a Afirika.

**I. Tushe, matsayi dabam-dabam da ma'anonin karin magana**

Za mu buɗe wannan babi da bayanai na galibi bisan karin magana. Za mu bada tushisshika da ma'anonin karin magana a gaggauce bisan karin magana da kuma matsayin shi cikin ma'amala ta al'uma.

## 1.1 Tushe da matsayin karin magana[2]

Kowace al'uma ta ƙirƙira karin magana kuma ta yi aikin da shi dangance da gogewa, buƙatunsu ko halayensu na rayuwa. Duk duniya ta san karin magana. To, daga ina karin magana ya ɗauko tushe ? Wa ya ƙirƙiro karin magana. Bada amsar wannan tambaya yana nufin sai an koma baya a ga ire-ire karin maganganu na da ɗan Adam ya yi, yanayinsu, zamaninsu na wallafawatsu. Idan ana iya la'akari da aikin samo tushen karin magana daga ƙananan bayanai, littattafai na adabi ko duk wani kundi da aka rubuta da suka ƙunshi karin maganar, to za ya yi wuya a gane tushen musamman karin magana na baka. Abun da za a iya cewa, shi ne dukkan al'umomi na ɗauri ko na zamani sun ƙirƙira karin magana a kan hujjoji masu yawa kuma cikin halaye dabam-dabam.

Galibi, a ƙasar Masar (da ake gani kamar cibiyar al'adu na ɗan Adam) za a iya binciko bayani na farko na karin magana da aka sani (kalmar karin magana ita ce *sebayt*, a yare na Masar). Wani littafi (papyrus) mai laƙanin *koyar da Ptahhotep*, ko littafin na *bayanan Ptahhotep*, da ake zaton *Ptahhotep*, ya wallafa shekaru 2400 kafin aifuwar Annabi Isa kuma da wani

---

[2] Mafi yawan bayanai da aka tattara cikin wannan ɓangare a fiddo su daga cikin matani mai laƙanin « Karin magana daga ina : nazarin tushe » da yake saman shafin yanar gizo : http://les-proverbes.fr/site/cote-mots/plus-sur-les-proverbes/ca-vient-dou-un-proverbe/letude-des-origines/

mutumen Faransa Emile Prisse d'Avesnes ya gano a 1843. Ana zaton cewa da littafin ya yi amfani wajen koyar da ɗa'a da iya magana.

Al'adun tarifi na ƙasa Girka ya zo da bayanai na karin magana da ake kira *paroimia* (daga ina kalmomi paremoniya suka ɗauko tushe, wato cewa da karin magana da kuma wasu sheɗaru na bayanai, paremoloji tana nufin nazarin karin magana, ita ko paremogarafi, rubutun karin magana). Karin magana na Girka ya samo tushe daga al'ada ta jama'a wadda mafi yawa an gade ta daga al'adu na Masar. An samo dayawa daga cikin ire-ire karin maganganu, kuma an adana su ta hanyar rubuta su, cikin wasu littattafai kamar misali *ayukkan da ranaiku* da wani rubucin waƙe ya wallafa (Karni na VIII kafin zuwan Annabi Isa).

*Cewar ma rubuci na ɗa Athanase, cikin labarin da Mamoussé Diagne ya rubuto (2005, p 94) ; « ana kiran paroimia (para tou oimous = tsawon hanyoyi) saboda ana amfani da su bisan hanyoyi, don a kyautata koyar da matafiya/masu bulaguro ; […] ta wannan hali ake horon masu bulaguro da suke tunanin abun da suke karantaw ». Karin magana yana da amfani wajen da tunatarwa da kuma ya kasance kamar wani guzuri ne ga mai bulaguro, yana zama kamar amsar mafafiyi yake jira ga tambayoyinsa lokacin da yake bulagoro bisan hanyoyi, kuma galibi dukkan waɗanda suke kan hanyoyin rayuwa.*

Akwai wasu nau'o'i na karin magana cikin matanai na addinai kamar su Babil da Kur'ani. A yau kuma ana samun karin magana dayawa cikin jawaban (musamman a yankin karkara) cikin kirari/take na yan siyasa ko bayanai na talla, matanai na adabi, littattafai kamar yadda ci-gaba rubutun karin maganganu yana nuna a halin yanzu (Wallafawar littattafai na paremiya) da kuma cikin nazarin da aka yi kan jinsi da marubuta dabam-dabam suka yi (masu nazarin paremiya)

Idan tun fil-azal al'umomi sun amince da karin magana cikin tabi'unsu na jawabai, to lalle waɗannan bayanan suna biya musu buƙatunsu na harsuna, na ra'ayoyinsu da na zamantakewar al'umomi mutanen kuma suna zame musu wani ɓangare na tunaninsu, wata hanya ta tattaunawa ko kuma wata madogara ta koyar da halaye nagari.

**1.2. Ma'anonin karin magana**

Ma'anonin karin magana sun fito daga cikin al'umomi da suke ƙirƙira waɗannan bayanai, ko su kasance ƙwararru da suke yin nazarin karin maganar. Saboda Karin magana ya fito daga cikin basirar al'umomi, ana jira daga kowace al'uma da ta bada ma'anar ƙananan bayanai daga alamominsu. Masu nazarin karin magana suna bada ma'anarsu dangance da matakai na da suka dace da tsare-tsare na sani da dubaru da suke amfani da su. Musu bincike kan fanni al'adar ɗan Adam ta karin magana, suna bada ma'anar karin maganar daga hanyoyi biyu.
Akwai ma'anoni dayawa na karin magana. Don buƙatun wannan bincike, za mu yi aiki da waɗanda al'umomi biyu na Afirika ta yamma suka bada, Bambarawa na Mali da kuma Sanwayawa-zabarmawa na Nijar da muka samu ta hanyar masu nazarin karin magana biyu : Joseph Russo da Claude Buridant.
Bambarawa suna kira karin magana da kalmar « *n'dale* » da ta samo tushe da *« ne »* (ni) da *« da »* (baza). In an haɗa « *n'dale* » sai bada « ni baza), wato cewa da *« ni ne baza, bayani ». Zahan ya gano a wurin Bambarawa « n'dale wata faɗa ce da take bayyana tunani, saboda a tunanin wanda yake faɗin karin magana, yana wuce kullum abun da karin maganar yake cewa […] n'dale na haɗa gogewa biyu , inda guda take gabatar alaƙoƙin na kamanni da wani, wannan ita ce daɗaɗɗa* (Mamoussé Diagne, 2005, p. 71)» kenan karin magana yana haɗa halaye biyu : hali na yanzu da ake ciki na bayyana jawabi da ya haɗa masu magana biyu gaba da gaba cikin wani yanayi na ƙayyadewa da kuma hali na tushe da ake maido bayanin da aka yi cikin wata fasarar harshe daga aka gada daga kakanni.

Wurin sanwayawa-zabarmawa, kamar cikin al'umomi da dama (musamman a Afirika), ana gama karin magana (*yaasay*) galibi da dukkan jinsuna na gajeru labarai kamar su salo na maimaita, juyayyar magana, matsautaccen labari, salo na magana, ba'a, faɗa ds. Karin magana wani bayani na basira, duk wani bayani a dunƙule da ba tafiya kai-tsaye.

Ainafi, kalmar *yaasay* a wuri sanwayawa-zabarmawa , wata sheɗara da aka taƙaitawa da « *ya a say* » da ke nufi a hausa « in baza, in warwatsa » ko kuma « in sibka » , « in rarraba ». « Bazawa » *yaasay* kan iya zama ɓarewa, idan aka yi nazarin kamar don a gano na'anar. A wurin wanda ake wa *yaasay* kamar wani kacici ne ilimi, wani ƙoƙari na fahinta daga ake gayyatar shi ya bada ma'anar wannan ƙaramar magana, wato karin magana. Amma « sibka, rarraba *yaassay* yana farawa da laƙantar karin maganar, maimaita ta don a yi amfani cikin halaye waɗanda suka dace in da yake iya bada ma'ana da ta yi daidai.

A ganin mai nazarin karin magana J. Russo (2009) « karin magana wata gajerar sheɗara ce, da aka yi aikinta kuma cikakka da fito ga wani marubuci da ƙirƙiro ta cikin tarihin da, mai wata siffa da ba ta sauyawa kuma da take bayyana wata gaskiya da gargaɗi da aka amince da su. »

Shi ko C. Buridant ( a cikin labarin M. Diagne, 2005 p. 64) na cewa karin magana wani « *tunani ne ko ɗa'a cikin gwangwani a dunƙule cikin wata ragewa ta galibi, hukunci na ɗa ko gogewa dangance da ƙa'ida, Karin magana yana zama tamkar wani bayani ne mai yanci ko wani ƙaramin labari da yake da wani tsari na musamman. »*

Karin magana ya zamanto, duk da ganin da ake yi mishi, wata magana mai sassarƙiya wadda ma'anarta ba ta da wani tasiri. Abun da za mu iya riƙewa daga bayanan da muka tattaro shi ne (i) karin magana wata dunƙular magana ce ( yar kaɗan amma da ta ƙunshi abubuwa dayawa, to don haka ne, kamar yadda sanwayawa da zabarmawa suka ce, a « baza » shi kafin a fahince shi) ; (ii) wani yabaici ne maganar ɓoye ( shi ya sa suke amfani da hoto/ko kwatanci don a gane shi) ; (iii) Siffar karin magana da ma'anarshi ta wani ɓangare ko ta gaba ɗaya sun danganta da kowace al'adar gargajiya ; (iv) Ana fasara karin magana kai-tsaya. Alamominshi da wasu abubuwa suna son a ce mai yin karin magana da mai fasara karin maganar sun ƙware sosai don iya amfani da shi a halin da ya dace : Karin magana ya danganta da harshe da kuma al'ada. Karin magana yana iya zama wata mahimmiyar madogara ta koyarwa wajen ƙarfafa sanin yan makaranta a fanni harsuna da al'adu.

## III. Karin magana da koyarwar harsuna-al'adu

A ƙasar Nijar misali, duk yake jama'a ta sani, ba a ma ba karin magana wuri ba a cikin jadawalai ko littattafan yan makaranta. Can sai an koma ba ƙwarai a samu littafin karatu da suka zo da zancen karin magana. Wannan littafin shi ne « *Mamadou et Binéta sont devenus grands » da aka wallafa da faransanci* (Littafin ɗan makaranta aji na 5 da na 6) na A. Davesne da J. Gouin, da ya haɗa paremiya (kacici-kacici da karin magana) da koyarwa nazarin kalmomi da kalmai da suka danganta da jiguna 36 na da aka yi aiki da su wajen koyon faransaci. Kenan muna gani ba a buƙatar karin magana a fanni koyar da harsuna –al'adu cikin makarantun boko na Nijar ; tsarin da bai yi ba daidai idan aka yi la'akari da ɗimbun arziki na jawabin da karin maganar ya ƙunsa da kuma kasancewarshi cikin jawabai na yau da kullum..

### 3.1. Karin magana cikin tarbiyar gargajiya a Afirika

A Afirika, galibi, musamman a Nijar, manya ne suke amfani da karin magana don horon matasa. Ana amfani karin maganar a fanni dabam-dabam ; musamman ma, yana daganta da halaye, wajen : bada siffa, zuba labari, yin gargaɗi, bada umurni, sa hanya, jan kunne, jan hankali, koya, hana, ds. Kenan kamar yadda muka samu bayani *paroimia* da Girkawa, ana amfani da karin magana ma a matsayi madogarar koyarwa don tarbiyar yan makaranta. Ana koyon shi kuma a hardace shi kuma a riƙa amfani cikin hali da ya dace da kuma isar da dhi a wurin al'uma ta gobe.

Karin magana yana bayyana wani hali na faɗin wani abu ko wani hali na gani, tunani ; wani hali na kasancewa. Karin magana ya zama wani salo na bayyana magana da, a taƙaice yana nuna alaƙar mutum da kansa da kuma sauran mutane kai har ma duniyar waɗanda suke amfani da shi. Wannan yana nufi cewa ana amfani da karin magana cikin jadawalan koyarwa na makarantun zamani a Afirika, a ƙalla inda a son waɗannan makarantu su kasance wuraren koyar da tabi'u na jawaban al'adunmu na gado.

**3.2. Karin magana da koyarwa harsuna a makarantar zamani**

Ana iya sanya koyarwar karin magana cikin jadawalan makaranta a matakai biyu : kamar wasu halaye na harshe da kuma kamar wasu halaye na al'adu. A mataki na farko, suna iya kawo wa makaranta ɗumbi arzika a fannin harshe da na jawabi ; a mataki na biyu suna iya taimakawa wajen sanin gogewa, da ƙa'idoji na girmamawa na gungunan al'umomi da suke amfani da su. Cikin wagga hanya, koyarwa-koyo na karin magana na kasancewa ta hanyar misali, manya-manyan ƙwarewaru na tattaunawa waɗanda su ne : fahintar baka, rubutattar fahinta, tattaunawar baka, da kuma rubutattar tattaunawa. Bisa waɗannan ire-ire ƙwarewarun huɗu da suke da alaƙa a tsakaninsu akwai kuma fanni na al'aɗa da ya ƙaru da ya danganta da su. Koyawar karin magana na iya bada damar cimma gurirrika dabam-dabam : fannin harshe, ƙwarewar ta harshe (ta tattaunawa) da al'adu. Wato akwai buƙata ta ganin karin magana ya samu shiga cikin jadawalin kayarwa-koyo na harsuna-al'adu a Afirika.

Kafin a bada ire-iren ayukkan koyarwa-koyo kan akarin magana cikin tsarin koyon harshe-al'ada, ana iya kawo maganar jan hankali na yan makaranta don su bada ƙarfi wajen koyo irin wannan bayani.

Mame Couna Mbaye (2015) na tunatar da mu cewa « ɗaya daga cikin ginshiƙan koyarwa-koyo shi ne maganar sa yan makatanta hanya ko jan hankali, wato mahimmanci da za su ba duk wani aiki na koyarwa-koyo da ya danganta da karin magana. Daga haka mun iya cewa samun

sani karin magana ya dogara da wasu hanyoyi ma’amala tsakanin malam da yan makaranta da kuma yan makaranta a tsakanin su. »

Mafi yawan karin magana sun samu tushe daga cikin karkara. Duk yake ana samu akasin hakan, ana cewa yan makarantar yankunan karkara ko waɗanda suka zo daga wurare kamar haka sun fi waɗanda suka zo fito daga yankuna birane sanin karin magana. Hakan yana sanya a gano cikin aji rukuna biyu na yan makaranta : waɗanda suka saba da bayanin na karin magana da waɗanda ba su saba. Nasarar jan hankali na yan makaranta daga malam wajen koyo karin magana tana iya danganta da sanin wannan gaskiya ta cikin aji.

**3.2.1. Karin magana da ƙwarewa ta fahinta**

A tafi da cewa fahintar jawabi ba abu ba ne mai sauƙi ; jawabi yana da sassarƙiya da kuma ɗauri wani sa’i. Fahintar ma’anar karin magana ba baya saboda siffa da sharuɗɗa na amfani da irin wannan bayani. A wannan fanni ana yarda da yawun Jean-Pierre Cuq & Isabelle Gruco (2013, p157) da suke cewa « samun ma’ana yana wahala a tsarin koyarwar da wani harshe na ƙasar waje sabàda abubuwa da dama sun shigo a fannin ganewa da kuma na fasara. »

Idan ana son samar da ma’anar karin magana, sai an yi hankali da abubuwa da dama da suka shafi harshe : tsari, kariyar harshe, ma’anar kalma, salo, ds. Akwai kuma abubuwan da ba su da alaƙa da harshe su ma suna shiga cikin gina ma’anar bayanai na karin magana da ake ƙirƙirawa a wannan zamani : halin tattaunwa, matsayin masu magana, yanayi na al’ada, motse-motsen jiki, gatsinen fuska ds. Idan ana son a fahinci ta baka ko a rubuce ma’anar karin magana ko a gaba a iya ƙirƙira shi, malam yana iya misali, amfani da wani ɓangare ko na duk gaba ɗaya na abubuwan da suke bayyana ma’anar karin magana da muka ganin can sama. Malam yana iya kuma aiki da waɗannan hanyoyin ayukkan koyarwa :

1- Danganta da mataki (paramari, sakandari, ds) ana fara koyon fahintar karin magana ta ga wasu matakai na galibi ; misali ta hanyar ƙirƙira cikin aji wani mahalli na kayan kiɗa da rubuce-rubuce saboda a ja hankali yan makaranta wajen bayani na ɓoye musamman bayanin cikin karin magana. Ana iya kenan :

- Fara, cikin wani zaman aiki misali, wani nazari na gauggawa tare da yan makaranta kan lamari na tattaunawa da ire-ire siffofinta (ta mutum ko ta dabba), kan yanayinta (na

baka da wanɗanda ba na baka ba) ; da kan madogaranta (murya, jiki, rubutu, zane, wayar sadarwa, ds) ;

- Sanya yan makaranta saurare ko karanta da babban murya ko a bayyana wasu gatanoni/ tatsuniyoyi, kacici-kacici, matanan waƙa, almara, taƙaitacaccen bayani, karin magana daga yan makaranta ; kwatanta ire-ire waɗannan jawabai da wasu jawabai na yau da kullum ; da sanya yan makaranta su yi tunani kan siffofi da abubuwan da suke ƙunshe a cikin ire-iren matannan ;
- Kirƙira wani mahalli na rubuce-rubuce ta hanyar kyautata bangunan aji da kahe-kahe da wurare in da ake iya liƙa ƙananan matanai da yan makaranta suke iya gwada basirarsu ta al'ada ta hanyar gabatar da kacici-kacici, karin magana, habaici, ds.

Ana son ta tanyar waɗannan ayukka da kuma wasu ma, a ƙara haɗa abun da ake koyo a makarantar boko da kuma abun da ake yi cikin tattaunawa ta yau da kullum, ba ta hanyar makaranta ba. Ana son wato a waye kan yan makaranta da su natsu wajen jawabai da suke kewaye da su, su samu wata tabi'a ta saurare da ta gani cikin amincewa dangance waɗannan ƙirƙire-kirƙire bayanan.

A game da koyon fahinta baka kuma da gurirrika da kayan aiki da ake da, malam yana iya « koyar da » karin magana ta hanyar sassa ukku da aka tsara cikin madogarar koyarwa ta bayanan baka : Share-fagen saurare, saurare da bayan saurare.

**Sashen share fagen saurare** taki na farko zuwa ga fahintar jawabin karin magana. Ana iya a wannan sashe a gabatar da hali na sanya ɗan makaranta hanya da jan hankalinsa. Ana samar da ɗan makaranta gurirrika darasi, abun da ya ƙunsa da kuma siffar da za ji cikin halin tattaunawar. Ana iya, daga waɗannan gurirrika na darasin, jinsi da halin bayanin karin maganar, a yi wasu yan tambayoyi na fahinta ta gaba ɗaya, kan misali jigo, mai magana, gurin da ake son cimma, tsari bayanin da kariyar harshe ta karin magana, da kuma wasu abubuwa da ba su shafi harshe amma suke tafiya tare kamar su karan sauti, ds. Gurin wannan sashe na shiri shi ne na jan hankalin da nutsuwa ta saurare na yan makaranta.

**Sashen saurare** shi ne na lura da fahintar bayani na karin magana da abubuwan da sashen ya ƙunsa : mataki, yan bayanai, kalmomi, gaɓoɓi da sautin haruffa na cikin karin maganar. Bayanin yana iya kasance wani karin magane ne keɓaɓɓe (mai zaman kanshi) ko karin magana

a ƙunshe cikin wani dogon bayani. Malam da kansa ko « yan makaranta na gwaji » na iya faɗi saƙon na saurare, ko kuma ta hanyar wata madogara da ake da kuma aka tanadar don haka : radiyo mai rakoda, wayar kira, ds. Aikin malam a nan shi ne lura da yadda ɗan makaranta yake fuskantar bayanin. Daga gurirrika da ake son a cimma, ana iya saurare karin magana fiye da sau ɗaya. Saurare ba ya na nufin kashe kunne kwai ba ne, wani mataki na aiki inda ɗan makaranta za ya maida hankalinsa kuma ya yi amfani da dubaru da suka dace wajen fahintar bayanin don ya bada amsoshin tambayoyin da aka yi masa a sashe na share fagen saurare.

A wannan sashen na **bayan saurare** ana sanya yan makaranata su gudanar da ayukkan da za su ba su damar bada amsoshin tambayoyin da aka yi musa kafin saurare. A nan akwai hanyoyi biyu da suke bada damar fahintar baka ta karin magana :

1. Idan karin magana wata sheɗara ce keɓaɓɓa, ana iya ba yan makaranta damar gano ma'ana da baka ta hanyar yi musu ƙayyadaddun tambayiyo kan :

- Bayyanawa (wa yake bada bayanin karin magana ? Zuwa ga wa ? Cikin waɗannan halaye ? Ds.);
- Alamomi na tsarin kalamai da na furtawar bayani ;
- Fotunan da suke ƙunshe cikin bayani ;
- Alamomi na ma'anoni da na aikin karin magana ;
- Alomomi na al'adu;
- ds.

2. Idan an bayyana karin maganar cikin wani jawabi na baka wanda yake da ɗan tsawo (labari, bada siffa, tattaunawa ds. Da yadda ya danganta da madogara, ayukkan koyon gano ma'ana suna dogara da :
- Duk gaba ɗaya ko ɓangare na alamomi da muka zana ;
- (in son samu) halaye na bayyanawa da saurarawa ta musamman da hali na tattaunawa da suka haɗa motse-motse jiki, kwaikwayo, da suke girke cikin al'adar mai magana ;
- Ma'anar karin magana da yanayi da aka nuna ;
- Ma'ana ta bi kalma-kalma da ma'ana ta ɓoye ta karin magana ;
- Ayukka na jawabai da na tattaunawa na karin magani cikin matani ;
- ds.

Fahinta a rubuce ta karin magana tana zuwa ta bin hanyoyi iri ɗaya na fahintar baka : **mataki na waye-kai** da na sa hanya za ya gabato **karatun na dindin-dindin** na karin magana ko na matanin da yake ƙunshe da shi. ; **Mataki na nazarin** bayanin (shi ne mataki da ya fi biyu da muka gani tsawo) za ya biyo baya don yin nazarin matanin na karin magana. Nazarin ana iya shi kan kalmomi da kalamai, tsarin kalmomi, alamomi na al'adu na cikin karin magana, ds. A lura da cewa karin magana, misali wata mahimmiyar madogara ce da take iya bada damar nazarin lokuttan yanta na ayukkan da kuma matsayi dabam-dabam da sheɗara take iya ɗauka. Duk wannan za ya iya kai mu ga fahinta ta gaba ɗaya, amma da za a zurfafa da bayani, cikin zaman kanshi ko cikin alƙoƙinsa da suka danganta da harshe, ma'ana da na aiki tare sauran matani da ya ƙunshi karin maganar. Daga haka, dangance da jinsi na matani (na siffantawa, na zubin labari, na hujjantawa, na bada labari, na bada umurni, na waƙe, na talla ds ?), ana iya yin nazarin matsayin, siffa da aiki na karin magana cikin jawabi.

Bayan ayukkan fahinta (ta baka da rubutatta) ta karin magana, ya kyautu a sanya yan makaranta su yi bayani kan abubuwan da suka gano ko suka koya daga waɗannan bayanan na karin magana da yadda ake tafiyar da su.

### 3.2.2. Karin magana da basirar ƙirƙira

Basirorin ƙirƙire-ƙirƙiren (ko bayani) na baka da rubutattu haɗe suke da na fahinta. Sanin da aka lakanta a fannin fahintar baka ko rubutatta fahinta za a yi sake yin amfani da su wajen ƙirƙira bayanai na karin magana (na baka ko rubutattu).

Kirƙira ta bata za ta iya kasancewa a wurin :

- Karatu da babbar murya /a bayyane na karin magana ɗaya ko fiye da ɗaya : an iya lura da yadda ake faɗi karin magana ko da suke da tsare-tsare tafiya (da biyu-biyu, da ukku-ukku, ds) dabam-dabam ko iri ɗaya ; dangance da tashin murya, ma'anar karin magana, ds ;
- Bayani dalla-dalla na ma'ana karin magana cikin halaye dabam-dabam (don a gwadi ire-ire ma'noni na karin magana da suka danganta da in da a ka yi amfani da shi ;
- Amfani da karin magana daga hanyoyi da malam ya bada. Malam yana iya bai wa yan makaranta hali (wuri, aiki da za a yi), matsayi (masu magana), gurin da aka sa gaba (bada gargaɗi, bada umurni, hukuntawa,…) ;
- Badawa daga yan makaranta halaye na tattaunawa da suka dace wajen amfani na karin magana ;

- Bayana na karin magana da yake taƙaice wata kammalawa ta wani hali na ruyuwa ;
- Kirƙira ta baka ta karin magana bisa misalai da aka bada (tsarin tafiya biyu-biyu, ukku-ukku, maras foto, mai foto, mai kawo bayani na dabobi, na shibkoki, na mutane….) ;
- Ds.

A game da rubutattar ƙirƙira ta karin magana, ta iya shan bamban da ayukkan iri-iri da malam ya bada zaɓi kan su ko da yan makaranta su ƙirƙiro ; ga misalan wasu daga ciki :

- Gabatar da a rubuce wani karin magana da aka haɗu shi (cikin wata magana ko cikin wani karatu na labari) da ake so shi sosai ; ɗan makaranta yana iya yin bayani dalla-dalla kan halayen gano karin maganar kuma ya bada wujjojin da suke sa yake jin daɗin wannan bayani ;
- Bayan wani bincike, a gari, cikin unguwa, wurin mutane na buƙatu, a gabatar a rubuce wani ɗan bayani na karin magana na wurin ;
- Karkasa karin magana dangance da kusancinsu na ma'ana da kuma tsarin kalmominsu ;
- Bada bayani dalla-dalla na ma'ana karin magana dangance da halin tattaunawa ;
- Ta hanyar kacici gurabe, cika rubutun karin magana
- Sake rubutawa a daidai kalmomin da aka sauya wa wuri ;
- Kirƙira a rubuce karin magana ta hanyar yin koyi da siffa da bayanan da suke ƙunshe cikin karin maganar da aka sani ;
- Taiƙaice wani labari ko hali ta hanyar karin magana ;
- Kirkira wani labari wanda za a taƙaice kammalawar karin magana ;
- Ds.

Hanyoyi da karin magana da su bada damar fahintar halaye na ruyuwar ɗan Adam, a rubuce ko a baka suna da yawa, har ba iyaka. Ana iya bada hujjar cin moriyar da kyau ta abubuwan da karin magana ta ƙunsa ta iya bada damar girka yan makaranta cikin muhallinsu da al'adunsu ku ta bada damar buɗe ƙofa ga wasu al'adu.

**3.3. Karin magana da koyarwar al'ada**

« Al'ada wani garke na halaye da tabi'u na gama-gari, hali na gani, na tunani da na aiwatarwa da suke bada damar manufar inda mutanen suka sa gaba, cewa da gadonsu da suka raba da suka kasance a ciki suka samu kansu kuma suka zama wani ɓangare na tushensi » (Louis Porcher, 1995, p.55). Al'ada ta ƙunshi kuma wani garken jawabai da ƙirƙira daga wasu halaye da tabi'u na gama-gari. Wanin babba abu ne, al'ada. Banda aikin na tattunawa da yake cikawa,

karin magana yana da wani aiki da ake cin moriyarshi wajen koyarwa-koyo na al'adu. Ana yi nazarin manyan halaye na al'ada ta hanyar karin magana : Hali na al'adu, hali na yawan al'adu da hali na haɗuwar al'adu : hali na al'ada, hali na yawan al'adu da hali haɗuwar al'adu.

**3.3.1. Hali na al'ada cikin karin magana**

Kamar yadda muke gani cikin almarar dabbobi, karin magana yana amfani da duniyar mutane, ta dabbobi da ta abubuwan cikin muhalli don bayyana saƙo. Yana bayyana duk abun da ya shafi ɗan Adam. Ana iya riƙewa a kai duk wani kayan aiki da karin magana ya yi amfani don kwatantawa, ya dogara mutum, da mutum kawai.

Ana iya yin nazarin halaye na zamantakewar al'uma tare da yan makaranta ta hanyar yin amfani da kayan aikin da karin magana ya yi amfani da su. Misali ga yadda karin maganar sanwayawa da zabarmawa ya shirya matanin kwaikiwayon da duniyar dabbobi da kuma halaye na zamantakewar al'uma don kwatatawa ((Amadou Saibou Adamou, 2016).

Akwai dabbobi dayawa da ake yi wa matsayi cikin karin magana na sanwayawa-zabarmawa. Misali sanwayawa-zabarmawa sun aiki da alamomi na kamanin raƙumi, don ƙirƙira karin magana. Jimirin wannan dabba ya za ta zamanto wata madogara kuma yana bada damar ƙirƙira karin magana : *Da hari mooru kala yo* (Idan ruwa yana da nisa, to shirya raƙuminka). Haɗawarshi (raƙumi yana da tozo) ba ya ba shi damar ya kwanta reran ; ana ɗaukan wannan kamar wata al'ada mai bayyana ɗiyauci : *Yo ga bu a mana hangasu* (raƙumi sai ya mutu bai kwanta reran ba). Amma girman shi da dabbobi dayawa suke mangari da yake iya (idan an amfani da ita yadda ya kamata) takan iya kasancewa wata babbar riba, hamada : *Yo du jinde no a si waani a jaraw* ; *farkay kaŋ ga waani mo mana duwa* (Allah ya hore wa raƙumi dogon wuya, amma bai san yadda za ya kula da shi ; Jakki da ya iya, ba samu ba).

Wannan misali yana nuna halaye iri biyu da suka danganta dabobi (na gida da na daji) cikin jawabin karin magana : Ana girmama su wani sa'i, ko a ɓata su. Suna ɗaukan matsayi mutane cikin dukkansu a kullum ko halayen biyu.

Galibi, karin magana yana bada bayani kan ɗa'a da halin nagari da al'uma ta ayyana, wani sa'i ta hanyar abubuwa na kewaye. Daga haka, karin magana yana koya haƙu : *Suurante ga tondi hari zu* (Mai haƙuri shi kan dafa dutsi har ya sha romonshi), ko *Suurante no ga zan waayi* (Sai mutum mai haƙuri zai tatsi nonon budurwar sani a yau) Karin magana yana koyar da ma'ana ta awo da gaskiya wajen bada kai da yarda : *Talka ma doona kuunu ŋwaari* (talakka ya saba cin bisshiya) Naman bisshiya ba ya ƙosar da cin shi, amma ita ce mafi daidai da shi. Karin

magana ya buƙatar ƙoƙari, hanyar ɗaya ta samu yancin kai, saboda : *Ŋwaarrayyaŋhari si to gasoori ɲum* ( Ruwan da aka roƙo ba ya isar mai zawo wanka).

**3.3.2. Halin na yawan al'adu**

« Halin yawan al'adu wani hali na yin la'akari da al'umomi na al'adu da suka zama al'uma ɗaya. » (Cuq et Gruco, op-cit, p 59). Yawancin Kasashen afirika sun ƙunshi al'umomi da yawa na ƙabilu da kowace daga cikin su suna ƙirƙira karin magana da ya danganta da halayensu na rayuwa da kuma buƙatunsu da kuma yadda suke tunkarar duniya. Ana iya amfani da ire-ire karin maganar don a yi nazari kamar misali :

- Kaƙa kowace al'uma take ɗaukan kanta ta hanyar karin magana ;
- Kaƙa kowace al'uma take bayyana abubuwa dabam-dabam da alamomin rayuwa ;
- Buƙatu (ɗa'a, kayayyakin aiki, bada gaskiya, ds) mahimmai na kowace al'uma ;
- Kamanni da bambance-bambance ( na siffa, bautuwa, ra'ayoyi) na karin maganganu da al'umomi dabaù-dabam ;
- Yiwuwar haɗuwa tsakanin al'adu na al'umomi ;
- ds.

**3.3.3. Halin haɗuwar al'adu cikin karin magana**

Ana bada ma'ana Halin haɗuwar al'adu kamar « fahintar da wata al'uma yi wa wata al'uma. Ta hanyar lura, hulɗoɗi na kai-tsaye ko na wata hanya (kafofin sadarwa, fina-finai, adabi, na-ji-ana-faɗi ds) taskanin gunguna biyu A da B, kowane yana ba kanshi wani matsayi dangance da ɗaukan da yake yi wancan da ba yadda ya yi daidai da hakan ba kuma Halin haɗuwar al'adu wani al'amari ne na yadda ake ɗaukan mutum ko al'uma da akasari ya sha bamban da yake ƙarewa a wasu ra'ayoyi, wato wata shaida ta zato. ». P. Charaudeau, 1987, 27). Daga wannan ra'ayi ana yin la'akari da wasu karin magana kamar dunƙulallun jawabai na halin haɗuwar al'adu. Ga misalai nan na shaida ta zato da sanwayawa-zabarmawa suke yi wa fulani, ƙabilu biyu da suke rayuwa tare, da suke yi wa juna ta hanyar karin magana : Don su ce Bafilatani ba ya da gansuwa, sanwayawa-zabarmawa suna cewa :

> *I na fulan no kambe a deebe ga jase di* (Idan ka miƙa wa bafilatani hannu sai ya kama kafaɗa

- Don gwadin wautarsa ko halinsa na taɓi, a cewa da bafulatani :

  *Fulan ga fondo bay a ga fondo ha* (Bafulatani ya san hanya sosai amma kullum sai tambayi ina ne hanya)

Su ko Fulani suna cewa da sanwayawa-zabarmawa da suke kira Kado) waɗannan misalan :

- Don su nuna ƙetarsu :

  *Nyande kaado haaduno hattay* (Tun da Kado ya yi ɗaci, ba i sake sauya ba;
- Don nuna wautar sanwayawa-zabarmawa : *Ko kokkuda kaado fu no wundoto* (Duk abun da ka ba basanwaye-bazabarme sai ya rungune shi da hannu biyu

Cikin koyarwa-koyo na harsuna-al'adu, amfanin halin haɗuwar al'adu ba tattance kawai shaidar zato ba ne amma a san su, kuma a wuce su. Ana son daga al'ada ta gida, a sanya yan makaranta su gano kuma su yi aikin da wasu al'adu, cewa da su gina wata tabi'a kuma su amince da wancan. Duk wannan da kar bambanci ya zama bai da tasiri, amma kamar bambanci mai amfani wajen gina kai.

Cikin wannan hanyar ana iya tafiyar da ayukkan kewaye da karin magana tare da yan makaranta, kamar misalin :

- Zaɓa cikin karin magana na cikin al'uma waɗanda suke ɗauke da shaidodi na zato ;
- Bayan wani bincike, ku samo tushen shaidodi na zato na cikin karin magana ;
- Nazarun siffa, aiki da manufar shaidodin zato ;
- Tattance cikin karin magana ƙaƙa ake gabatar da kowane cikin wancan ;
- Danganta da shaidodin zato da abubuwa na gaskiya (mutane da halayen da karin magana yake bayyanawa sun yi kama guda kamar yadda aka nuna ?) ;
- Kula in shaidodin zato suna bayyana halaye nagari ko na banza ;
- Tattance cikin karin magana bambanci da kamanni na al'adu ;
- Tattance halaye nagari na wancan da aka bayyana cikin karin magana ;
- Mizanta matsayinka dangance da al'ada da ya zo cikin karin magana ; ds Abun riƙo a nan shi ne a taƙaice malam, ta hanyar karin magana, ya sanya yan makaranta, su fahinci cewa ban da son da jin daɗi da hali da ake samu cikin al'ada, akwai abubuwa na gaskiya, na sani, na ilimi na ɗa'a waɗanda ake iya samu ta hanyar koyo.

**Kammalawa**

Cikin wannan babi, mun tunatar da mahimmancin karin magana cikin bayanan ɗan Adam, amfani shi, azikinshi da kuma matsayi dabam-dabam cikin rayuwa. Muna riƙewa da cewa wasu baƙatu na harsuna da na al'adu da ba su da iyaka da makarantar zamani take iya cin moriyarsu a fanni dayawa na koyarwa-koyo, musamman na harsuna-koyo.

Kafin masu faɗi -a-ji da mawallafan usular koyo, jadawalai da littattafan makaranta na Afirika su bada umurni na na shigar karin magana cikin tsarin koyarwa-koyo a makaranta, malamai suna amfani da su wajen yin madogarai na koyarwa don koyon harsuna. Amma su yi aiki da halayen na al'adu da matakai dabam-dabam na koyo na yan makaranta

**Shawarwari na ayukka na zahiri**

- Ta hanyar tattara bayania a cikin al'umarku inda kuke rayuwa, ku gwaɗi tushen karin magana ;
- Kaka al'umar da kuke ciki take bada ma'anar karin magana ?
- Wace ma'ana ta yi muku daidai kuma kuke son koyar da yan makaranta ita ?
- Waɗanne ne mahiman ayukkan karin magani da kuka riƙe ?
- Cikin hanyoyin koyarwa da aka bada kan koyarwar karin magana, ku zaɓi wasu don ku ƙarfafa ƙwarewa a fanni harsuna, al'adu da tattaunawa ta yan makarantarku.

**Madogara**


ANSCOMBRE J-C. (2000), « Parole proverbiale et structures métriques », in *Langages*, n°1 39, pp. 7-26.

BERNARD, Y., et White-Kaba, M. (1 994), *Dictionnaire zarma-français*, Paris, ACCT.

CHARAUDEAU, P. (1987), « L'interculturel : nouvelle mode ou pratique nouvelle ? », in *Le Français dans le monde*, numéro spécial, février/mars, pp 25 à 33.

CAUVIN, J. (1981), *Comprendre les proverbes*, Editions Saint-Paul, Collection classiques africains.

MBAYE, M. C. (2015), « Pour une pratique d'enseignement-apprentissage des proverbes en classe de langue : l'exemple de la langue espagnole avec des étudiants francophones », https://books.openedition.org/apu/7183?lang=fr, consulté le 07-02-2021.

DIAGNE, M. (2005), *Critique de la raison orale. Les pratiques discursives en Afrique noire*, Paris, Karthala.

EL OUAFA, I., « Le proverbe : de la traduction à la communication », *Insaniyat /* [En ligne], 67 | 2015, mis en ligne le 20 juillet 2016, consulté le 25 novembre 2019. URL : http://journals.openedition.org/insaniyat/15024 ; DOI : 10.4000/insaniyat.15024

LEGUY, C. (2001) *Le proverbe chez les Bwa du Mali. Parole africaine et situation d'énonciation*, Paris, Karthala.

PORCHER, L. (1995), *Le Français langue étrangère ; Emergence et enseignement d'une discipline*, Paris, Hachette éducation.

RUSSO, J. (2009), « La ''grécité des proverbes grecs : un nouveau regard sur un genre ancien», in, Balansard, A. Dorival, G. et Loubet, M. (études réunies par), *Les Fondements de la tradition classique : en hommage à Didier Pralon*, Publications de l'Université de Provence, pp. 163-176.

SAIBOU ADAMOU A. (2016), *1000 et 1 yaasey. Expressions proverbiales chez les Songhay-Zarma*, Niamey, Editions Gashingo.

SARDAN (de), J-P., O. (1982) *Concepts et conceptions songhay-zarma. Histoire, Culture, Société*, Paris, Nubia.

**Kammalawa**

Dangane da wannan tafiyar aikin koyarwa mai babi takwas, me za ku tuna daga wannan littafin ?

Da farko wannan littafin makaranta ba ayi shirin aiki da shi ba. Ba ya bada amfani nan da nan a cikin azuzuwa. Manufarshi tunfarko ita ce ta nuna cewa bayanan zamantakewa da al'adun Nijar waɗanda ba a yi la'akari da su ba wajen samar da littattafan koyarwa, sun zama babbar dama ta sanya makaranta ba kawai wurin koyarwa da ilimi ba, amma kuma sama da duka wurin da ba ya cin amanar asuli da fatan ɗalibbai ta hanyar raba su daga tushensu na zamantakewa. A wata ma'ana, wannan littafin yana ƙoƙariya nuna ta hanyar tsarinsa na koyar da ilimi, ilmantarwa, a cikin kalma ɗaya ilimi (ilimi, sani, basirar rayuwa) da makarantar take bayarwa yana da mahimmancin yanayin ɗan adam wanda dole ne a yi la'akari da shi, don kafa makarantar zamani da za ta sa ɗalibbanta su zama masu daidaita al'adu da iya zamantakewa. Makaranta mai kyau ba ta taɓa zama wani abu ba sai wannan tsarin da yake haɗa sanannun da waɗanda ba a sani ba, tsofaffi da sababbi, wakillai da ainahin bayanai, abubuwan da suka dace, da dai sauransu. Don girka ma'anar, wannan jagoran ba ya bada darasi, amma yana bada hanyoyi don tunani kuma yana bada izini ga malamai da masu bada horo yan Nijar waɗanda zasuci moriyarshi kuma su amfani da shi kyauta ta hanyar daidaita shi zuwa yanayi dabam-dabam na ilmantarwa da za su wallafa.

Sannan mai karanta littafin ya gani nan take, wannan takardar ba ta da'awar gamawa ba, ta ƙumshi jigogi takwas ne kawai a cikin ɗarurruwan ko ma ƙaramcin yuwuwar. Wanda ya ba da sanarwar cewa ba zai zama na ƙarshe ba, cewa buga shi da fa'idarsa za su zaburar da wallafar da wasu littattafai a kan mahangar ilimin koyarwa.

Don haka muna riƙe da cewa bayana wannan kayan aikin sadarwa mai daraja, tare da jigogi dabam-dabam da mabambanta waɗanda suke haɓaka ilimi mai zurfi, alama ce da take nuna cewa wani abu yana kan hanya, mai yuwuwa ya sake yin tunani game da makarantar Nijar don mai da taingantacciya,ta yarda da kuma ta zamani na gaske. Wannan jagoran, watakila, izinin sake gina makarantar Nijar ne, tabbas, ƙoƙari ne na samar wa wannan makaranta kayan aikin samar da albarkatu da bunƙasa zuwa ga ilimi mai himma. A taƙaice dai muna fatan buga wannan littafin zai taimaka matuƙa wajen inganta harakar ilimi a Nijar.